[7/1, 11:52 AM] UMMU MAHER (MISS GREEN)🍃: *_💋D'AN HALAK💋_*

*_UMMU MAHER(MRS GREEN)🍃_*

~Wattpad~
Rabiatu333

~Arewabooks~
Rabiattu0444

1
_Destiny_
Around 5:pm

..........da mugun sauri ya d'ago yana kallon Salima sannan ya ce"yanzu Salima ni kike kira da d'an shege"?.

Ta wani juya idonta sannan ta ce" eh na fad'a idan k'arya ne ka musa mana"?.

Ya k'ara kallonta akaro na biyu, yaji tamkar zai bugeta saboda bak'in ciki yana da muguwar zuciya Idan ya ce zai yi magana zai iya shak'eta ta mutu, yayi saurin rintse idonsa sannan ya ce" get out of my side".
Ya fad'i hakan tamkar zai bugeta, ai kuwa ta firgita ta fita da saurin gaske saboda tsoronsa takeji da gaske saboda Haidar namiji ne guda acikin maza.

Go ahead ya bawa direbansa, nan da nan yaja motarsa sukayi gaba yana jin wani irin suya aransa tamkar zai mutu, kiran sunan Allah ya ke Amma shi kad'ai yasan masifar da ya ke ciki zuciyarsa sai k'una take hannunsa d'aya yana kan xuciyarsa har sukazo dai dai wata plaza tamfatsetsiya.

Ya dakatar da direbansa ya tsaya, da sauri direban ya fito domin bud'e masa ya dakatar dashi da Sauri ya fito ya bud'e da kansa yana wani juya kyakkyawan eyes d'insa Wanda kallo d'aya za kayi masa ka gane yana cikin matsala, domin sun kad'a sunyi jawur jijiyoyin kansa sun tashi sunyi rud'u rud'u kallo d'aya zai baka tausayi ayanayin da ya ke ciki.

'HAIDAR SHOPRITE'

Ya rintse idonsa yana jin wani irin mugun haushin tarin dukiyar da Allah yayi masa gashi bata amfanesa wajen samun macen da zai aura ba haryanzu duk don saboda wani rufaffan sirri Wanda fad'arsa ma bai da wani amfani, a iya k'iyasinsa ya nemi aure ya kai sau goma, sai Abu yayi nisa sai ya lalace saboda wannan bak'in dalilin Wanda baki ba zai iya furtawa ba.

Ya goge kwallar da ta zubo masa, ya fara tafiya cikin yanayin tafiyarsa me kama da tafiyar

hawainiya.

Aminu direbansa yayi magana afili ya ce" Allah sarki bawan Allah, haka kai kuma Allah ya tsara maka ga kud'i ga kyau ga ilimi Amma sai Allah ya yi maka wannan babbar jarabta ta rashin samun matar aure Wanda ko nasaba d'aya ka had'a acikin hud'un nan zaka samu matar aure, Amma sai gashi duk basa wani amfani awajen matan.

Tunda ya shigo kowa ya fara kai gaisuwa wajen babban oga Boss Haidar, sunan da suke fad'a masa kenan saboda yanayinsa na rashin son yin magana da kuma iya had'e girar sama da ta k'asa.

Tuni ya isa babban ofishin babban me kula masa da wannan babbar plazar.

Azaune ya samesa yana ta aikin ciccike wasu takaddu da Sanya hannu aciki, yana ganinsa ya saki fara yana ce wa" Boss wallahi yanzu Ina aikin nan amma tunaninka nake, saboda akwai wasu kaya da suka shigo tun jiya kuma kai nake jira ka sanya Han......"

Saurin dakatar dashi yayi, yana me zama ad'aya daga cikin manyan tamfatsa tamfatsan manyan kujerun da suke k'unshe cikin ofishin Wanda sanyin A/c ma kad'ai ya isa ka tabbatar abin na manya ne.

Hammud ya ce" Boss da damuwa kan fuskarsa fa? Ko dai Salima ce"?.

Ya furzar da numfashi sannan ya nisa ya ce" triple ayau na tabbatar da abinda mutane suke fad'a akaina, da duk gani nake zancan banza ne da shirme Ashe gaskiya ne domin masu iya magana sunce wak'a abakin me ita tafi dad'i, domin alokacin da ake fad'ar wannan mummunar maganar akaina d'auka nake babu mak'iyina irinsa, Amma ayanzu na gane masoyana ne su, tunda masu son abin hannuna basa iya fad'amin gaskiya sai dai suyimin shiru suna d'aukata shasha, domin yau Salima ta fad'a mini ba zata aureni ba tunda ba nida Uba duk ranar Dana nemo waye ubana inzo in aureta ita kuma ashirye take".

Hammud yayi shiru, yaji k'irjinsa yayi masa wani mugun nauyi ko kusa baya San ganin amininsa cikin matsala Amma ya zamar masa dole awannan karon yayi wani Abu domin ceto abokinsa daga halaka.

Ya nisa ya ce" Boss inason ka Sanya aranka wannan itace k'addararka, Kuma baka isa ka goge taba domin kuwa daman can an rubutashi alauhul mahfuz kaga babu wani bawan daya isa ya goge sa, yin hak'uri shi ne mafita Amma ka daina sanya damuwa sannan inason ka nutsu ka koma wajen Ammi ka k'ara tambayarta waye mahaifinka? Watak'ila awannan gab'ar asamu cigaba".

Ya d'an ja numfashi me fasali, sannan ya ce" kana ganin zan iya zuwa in sameta awannan gab'ar? Ka manta abinda yake tsakanina da ita ahalin yanzu? Rabon da mu had'u yau wata

hud'u kenan, nak'i zuwa Inda take tun bayan da nak'i karb'ar labarin da ta bani akaina, domin kuwa gani nake tamkar ba haka bane Idan kuwa hakane me ya hanata sanarmin tunda can"?.

"Duk wannan ba dabara bace Boss ba'a yiwa iyaye haka fa? Musamman ma Uwa, lallab'a lamarinta ake asannu domin gudun b'acin ransu tun sanda ka fad'amin na ce kaje ka bata hak'uri shi ne ka k'i? Ai Idan zaka yiwa wani zafin ranka bai kamata ka yiwa Ammi ba, tasha gori da habaici da zagi tun daga samuwarka har zuwa yanzu bata tab'a jin dad'in rayuwarta ba, kuma duk akanka haba Boss ka dinga sassauta zuciyarka domin gudun fad'awa halaka, kuma yin aure a irin wannan halin naka, domin su mata sunfi son namiji me sauk'in zuciya da nuna kulawa akoda yaushe, sai kaga mace ta sakar maka dukkanin abinda ya shafi rayuwarta harma da abinda baka tab'a tunani ba".

Ya gamsu da abinda ya ce, ammanfa wannan zafin zuciyar tashi baisan yadda zai yi dashi ba, domin kuwa haka Allah ya yisa awani lokacin ma Idan ransa ya b'aci sai yaji tamkar zai yi hauka saboda tsabar k'uncin abinda ya keji.

Hammud ya ce" akwai k'anwata Zahra, tana nan makarantar ABU Zaria ina ganin me zai hana Idan ta dawo ka neme ta? Tunda yarinya ce me hankali na kuma yarda da hankalinta da nutsuwarta".

Ya d'anyi jim, sannan ya ce" uhum Allah ya kaimu ni zan wuce maganar saka hannu kuma na bar maka wuk'a da nama duk abinda kayi dai dai ne".

Suna tafiya suna d'an tab'a hira har yazo bakin motarsa, Hammud ya koma ya cigaba da ayyukansa yana me jin tausayin amininsa aransa domin kuwa Haidar mutum ne me matuk'ar buk'ata Amma kuma Sam baisan Neman mata ba, sai dai ya gama ciwonsa ya bari babu Wanda ya sani Wanda ayanzu haka ya ke Neman Haifar masa matsala babba.

$$$$$$

......wani irin kuka nake yi, Wanda kana ganinsa kasan kuka ne na wacce ta gaji da duniya, sai zarya nake daga cikin asibitin zuwa waje hankalina duk amatuk'ar tashe ina tunanin halin da mahaifiyata take ciki, na samu wani d'an benci na zauna ina ta rusa kukana, mutane sai kallona suke wasu su tsaya su tambayeni lafiya? Wasu kuma suyi wucewarsu matsalata ce ba matsalarsu ba.

Na dad'e acikin wannan halin sannan na garzayo na dawo cikin asibitin, na lek'a d'akin y'an haihuwa na hangota can sai kiran sunan Allah take, na kwalla mata kira cikin tashin hankali.

"Umma! Umma!!".

Da sauri wata nurse tayo kaina tana yimin masifa, tana hargagi wai uban me Nazo yi?.

Jikina duk asanyaye na bar wajen, ina tafiya duk jikina amatuk'ar sanyaye na zauna ina tunanin halin rayuwa.

K'annena 8 ne, ni ce babbar y'ar mamanmu inada shekara 18 yanzu aduniya, mahaifina Sam bai damu da rayuwarmu ba sai ta matarsa wacce ta zamar masa y'ar lele, kuma bata tab'a haihuwa ba ta sanya rayuwarmu agaba da tsangwama da cin mutunci, mahaifiyarmu ba tada damar ko yin tari agidan sai ta tambayi ba'asin wannan tarin na ta, baki d'aya ayanzu ta had'a tsanar kowa agidan ta d'oramin wai duk mugun halin uwata na kwashe sa, duk hak'urina sai danaso tanka mata Amma mahaifiyata sai ta hanani.
ko yau dana kawo mahaifiyata asibiti dana je na faɗa masa ce min yayi ai dama ta saba haihuwar gida kaza uwar ƴaƴa, shi baida kuɗi saboda haka duk ma yadda zamuyi muje muyi idan taji haushi ta daina haihuwar, wannan maganar tashi ta ƙarshe ta sanyani acikin
wani hali, na fashe da kuka saboda bansan yadda zanyi wajen kai ta asibitin ba domin ba muda ko ƙwandala haka muka tashi gashi dama aikatau mahaifiyata takeyi kuma ba a bata kuɗin watanta ba ni kuma kullum tallan shinkafa da wake nake ɗauka da safe da yamma, dashi muke rufawa kanmu asiri ni da ƙanwata Amira ita tana ɗaukar nata da rana, wannan yasa mahaifinmu ƙara buɗa ƙafafuwa yake cin karensa babu babbaka domin kuwa sisinsa bata shigo mana, saboda wannan sana'ar tun dama ba wani abun kirki yake bayarwa ba naira ɗari biyar yakw bata
acewarsa tun safe har yamma, haka zamu ƙwaɗa garij ƙwaƙi idan mukasha ma lokaci ɗaya shikkenan, kuma kada kuce mahaifinmu zaune gari banza ne a'a shi ma'aikacin gwamnati ne sannan yana da gidan biredi ƙato shi da ƙaninsa wanda bayan an raba musu gado suka buɗe Gidan biredin tunda su biyu kacal iyayensu suka haifa ƴan asalin garin shanono ne.
wannan albashin nasa kaf na matarsa ne sai abinda tayi niyya take sammasa mudai wannan matar Allah ya isa bata goge mana baƙin cikinta domin kuwa kullum sai munyi mata amma ko ajikinta, domin dama mutane masu aikata rashin mutunci sunfi daɗewa agidan duniya.sam bana ganin mahaifina da daraja ko wani mutunci sau da dama ko amajalissarsu na gansa bana ko kallonsa, saboda da tsanarsa na taso agidan duniya bansan me yasa ya tsani mahaifiyata ba? Ko da yake nasan wani al'amarin sabida tana yaean haihuwa shiyasa ya tsane ta wai taƙi yin tsarim iyali, shiyasa ko kaɗan bana ganin girmansa domin da ba'a haihuwa da shi kansa ba'a haifesa ba.

Ina cikin wannan tunanin likitar ta fito ta ce" ke! mahaifiyarki ta haihu ƴan biyu duk maza, kije gida kuxo da ƴan uwanki ku biya kuɗi ku ɗauketa".
Jikina har ɓari yake domin in isa gare ta, likitar ta dakatar dani da ce wa" wa yace ki shiga? Ko gama gyarata ba'ayi ba kije dai can gida ki faɗa musu kafin nan an gama komi".
da hazama na runtuma da gudu saboda inason isa gida domin in ɗan siyar da wasu abubuwan in kawo, nasan dai abinda take nufi kuɗi ne ba wani abu ba.
https://chat.whatsapp.com/LcnDvIFNqL0Enq7lInpAVe

UMMU MAHER CE
[7/1, 11:54 AM] UMMU MAHER (MISS GREEN)🍃: *_💋D'AN HALAK💋_*

MALLAKAR
*_UMMU MAHER(MRS GREEN)🍃_*

*_AREWA WRITER'S ASSOCIATION📚_*

~*Arewabooks*~
D'AN HALAK:: https://arewabooks.com/book?id=6631fffa0eeb3b80f1ef8159

*Danna wanna link ɗin kai tsaye xaka samu 3k daga tsarin palmpay amma waɗanda basu taɓa buɗewa ba, kisa lambar wayarki zai kai ki inda zaki ɗakko application ɗinsu, idan baki gane ba ki tuntuɓe ni ta lambata 07068606171*
Hey, I use the PalmPay app for free transfers and to get cashback on every transaction. Use my link or my code "SUQD6653" to join and get ₦1000 welcome bonus.
https://link.palmpay.com/34vPB

2
__________sauri-sauri nake har ina ɗan haɗawa da gudu, har Allah yasa na samu damar isowa gida tafiyar danayi daga asibiti zuwa gida za tayi ta awa ɗaya idan a daidaita ne tafiyar minti talatin ne.
Tun daga nesa na hango mahaifina, riƙe da kaya niƙi niƙi kusan ledoji manya viva guda uku sai nishi yake kamar wanda ya ɗakko ingarmar dutse.
Nayi saurin matsar da idona daga barin kallonsa, domin arayuwata ayanzu babu abinda na tsana sama da mahaifina, idan na gansa maimakon naji irin daɗin nan da ƴaƴa sukeji da rahama daga kallon iyayensu a'a ni sai dai naji kamar na bindigesa, ban tsaya ba na kuwa wucewa ta abina zuciyata tana saƙamin in tsaya ko gaisuwa inyi amma na kasa domin kuwa Allah ya sani bazan iya hakan ba, Umma tasha yimin faɗa akan kada na kuskura fushin mahaifina ya tabbata akaina, domin bazan taɓa samun abinda nake so arayuwa ba kuma bazan samu albarka ba, saboda haka sai na canja shawara na dawo da baya har na isa kusa dashi na ce" sannu Baba bari in ɗaukar maka kaya...."
A'i tun kafin in ƙarasa yayi saurin dakatar dani, gamida ce wa" yanzu kika hangoni, marar albarka da zaki taho? ina tun daga titi kika hangoni, amma tsabar gulma sai da na kusa shiga gida zaki ce zaki tayani? Ko da yake idan bakiyi ba ai baki yo halin Rabi uwarki ba, mace sai iya gulma da kinibibi da son haɗa mutum da ƴan uwansa, ni dai ko mayu ne ku keda uwarki baku isa ku cinyeni ba, masu yawom tsiya tasi no gareji kuyi nan kuyi nan tun jiya kuka fita sai yanzu ne ke kika yi tunanin dawowa gida, tinkiya uwar tamɓele".

Wani irin malulun baƙin cikine ya tokare ni, na kasa haɗiye wani irin wahalallan yawu saboda tsabar jin zafin furucinsa "tinkiya uwar tamɓele". wannan maganar tashi ta ƙarshe ta sanya jikina yin la'asar, domin ban taɓa tunanin wannan ranar zata zo da mahaifiba zai dinga jifana da waɗannan miyagun kalaman ba, raina in yayi dubu ya ɓaci wato shi bai damu da tambayata inda ma naje ba? abinda kawai ya damesa shi ne zagi da aibata mu, abu ɗaya na yarda dashi shi ne bazan yiwa matarsa biyayya ba domin kuwa duk wani halin da muka shiga ahalin yanzu

ita ce ummul aba'asin haɗa wani abun, domin kuwa ada ba haka mahaifinmu yake mana ba tana zuwa ta buɗe masa ido da zuga, kullum cikin wulaƙantamu yake da aibatamu idan tashi tw ciwo shi cikin dare sai ki gansa aɗakinmu yazo wajen Ummanmu, ya lallaɓata su tafi ɗakinsa yana rarrashinta tamkar ba shi ba, ya gama ci mata mutunci atsakar gida an jima kuma yazo ya ce zai lallaɓata, ita kuwa Kande tana can tana sharɓar barcin asara domin kuwa bata sanin me ke faruwa? sai dai taga Umma da ciki ta haihu, wannan abu yana baƙanta mata rai sosai saboda ita ko ɓatan wata bata taɓa yi ba.
na goge busasshen hawayena na shiga cikin harabar gidanmu.

ina shiga na wuce ɗakinmu, tsakar gidan babu kowa kuma banji hayaniyar ƙannena na ba, ina shiga na hangosu atakure agefe ɗaya suna ta jan numfashi suna shasheƙar kuka, da sauri na ƙarasa gabansu jikina har yana kyarma saboda sam banason in gansu cikin wani hali, nima sai naji duka hankalina ya tashi na ƙaraso da sauri na rungumosu duk yawansu, ai kuwa duk suka maƙalƙaleni suna kuka na rintse idanuwana saboda nasan ƙwanan zancan ba zai wuce Baba kande ba, domin ta tsani buɗe ido taga waɗannan yaran gashi Umma kusan gwarnai take kafin ta  yaye take ƙara samun ciki, gashi mu 9 yanzu mun zama mu 11 cif cif tunda ga ƴan biyu nan.

"Anti ya jikin Umma"?.

cewar Amir, ƙanina ɗan shekara 12 me bin Ummi ita kuma tana da 15, sai Amira me shekara 17 ni kuma 18 da rabi sai sauran ƙannenmu dama ni ce babba.
na shafa kan Amir na ce" da sauƙi Amir ta haihu ma, ƴan biyu duk maza masu kama da kai da walid".
Ai tuni suka sanya ihu suna dariya da murna suna ce wa "Umma ta haihu! Umma ta haihu!!".
Tuni suka firfito har ƙaramarmu Anisa me shekara 2 tana tsalle ganin ƴan uwanta ma suna yi, na bisu ina kira amma ina har sun fice waje domin faɗawa maƙota nayi nasarar kamo Anisa na riƙe domin ita tayi ƙanƙanta bana bari ta fita, kullum tana goye abayana.
Amira ce ta shigo da murnarta ta ce" kai ai har naji daɗi Anti, wallahi tun jiya bamu runtsa ba ashe Umma ta haihu? yanzu Amir yake faɗamin".
Tuni Ummi tayi gaba, tana turo baki ta ce" ni wallahi banji daɗi ba ace kullum Umma ba tada aiki sai haihuwa,kuma idan ma ta haihun ko kaza ba a yanka mata balle taci ragon suna, shi ne za'a zo ana wani yaɗawa ta haihu".
  Amira ta ɗala mata duka ta ce"shegiya me zuciya irin ta Babanmu, yau da Baba kande ce ta haifeki da na ce kinyi gad........."

"uwarku ma ai mugun halin gare ta, shegiyar yarinya me zuciyar rashin mutunci wacce bata san annabi ya faku ba".
ta ɗaga labule.
"malam fito kaji zagin ala tsinen da wannan marar albarka take mini, fito ka tsitstsinewa shegiya ƴar gadon Fulani masu mugun hali".
Ai kafin ta rufe baki har Babanmi ya fito, yayo kan Amira da gudu tayi ƙofar gida Ummi me baƙar zuciya ta tsaya awajen ko nan da can bata je ba, domin ita Allah yayo ta da shegen taurin kai ga faɗa da son wulaƙanta mutane tamkar ƴar Baba kande.

Ni kuwa ɗakinmu na shige, ina saƙawa da warwarewa ga Anisa a hannuna har ta fara barci da alama yunwa takeji.
ya gama faɗansa da tsine tsinensa ya koma ɗaki, kamar baban ɗaki domin kullum yana ɗaka sai ka rasa me suke tattaunawa shi kuma ba sana'a yake ba daɗinta ma yana aikin gwamnati duk wata zai amshi albashi, amma yadda kasan baya samu dama shi duk ɗan albashi ya saba haka, duk sanda ya dawo daga aikiin ya shige ɗaki to sai dai sallah amma ko majalisa bai fiya zuwa ba, idan kuwa kaga ya fita to matar son nasa bata gari ne.

Amira ta shigo ta sameni na haɗa uban gumi, taɗan kalleni afakaice ta ce" yanzu Anti ya Umman? nasan dai kun tafi babu ko biyar to yanzu ya za'ayi asamu kuɗin sallamo Umma daga asibitin"?.

Shiru nayi kamar me tunani na ce" Amira me zai hana muje gidan DEEN MARSHAL gidan da muke aiki nida Umma muje su taimaka mana da kuɗin aikinta ko na rabin wata ne kinga ya isa mu bayar asallame ta".
"kin kawo shawara Anti Humaira, sai dai kinsan ba suda mutunci wallahi, kada mutun yaje su nemi su wulaƙantasa".
Kafin ta kammala maganarta na tuno da abinda ya faru abaya, sanda Umma na laulayi naje domin su bata kuɗin watanta sai da suka silleni sil sannan suka watsomin afuskata, ina kuka na ƙwashe kuɗin na dawo gida Umma sarkin haƙuri bata ko nuna min komi ba, ire iren wulaƙanci da nuna ƙyama duk suna mata saboda wani lokacin idan za'ayi sha'ani agidan ina zuwa in taya Umma aiki abiyani, amma tun da naga suna wulaƙantata sai na daina zuwa sam.

wani tunani ya faɗomin.
Na ce" Amira me xai hana muje wajen Baba Sadi, ina ganin kamar ba zai hanamu dubu ashirin ba dai tunda kinga ƴar uwarsa ce".
"eh to bazan ce komi ba Anti, amma sai dai ke kije domin bazan lamunci wulaƙancin matarsa ba ehe, domin tana yimin zan fito mata a asalin kala ta".
Inaji ina gani na goya Anisa abayana, domin bata fiya yarda da kowa ba Amira kumw dukanta take shiyasa bata yarda da ita.
Na kama hanya na tafi, da yake can Hotoro GRA yake nayi sa'a yana gida ba kowa, da yake yaransa biyu ne kuma duk suna makaranta matarsa kuma ma'aikaciya ce, shi kuma ɗan kasuwa ne amma ba kullum ya ke fita kasuwar ba.

A farfajiyar gidansa na hangosa, yana shan iska na ƙarasa da fara'ata yana karanta jaridar Aminiya, na ƙarasa na gaidashi saɓanin da yake amsawa da ƙer yanzu cike da gwanintar iya dariya yake yaƙe haƙora, har yana tambayata mahaifiyata da Babanmu.
Na ce" lafiya lau Kawu, inasu Fadil da Amrah da Maman Fadil"?.
ya amsa yana shafa gemunsa gamida ƙaremun wani irin kallo me cike da fassarori da dama, sai dai ni ban gane kallon ba ina tunanin ko dom yaga na rame ne yanzu oho?.
na sunkuyar da kaina, hawaye suka shiga ƙwaronyomin na fara irgo baya nan sala sala.
"dama Ummanmu ce ba lafiya Kawu, tana asibiti yau ta haihu da safe ƴan biyu amma Baba

babu kuɗin da za'a biya mata na asibiti kuma gashi suna son sallamarta".

yaɗan shafa gemunsa cike da tausayina ya ce" yi haƙuri kinji daina kuka, zo muje daga ciki sai in ɗakko miki kuɗin".

jikina asanyaye na tashi na bishi, ina godewa Allah domin kuwa nasan kukana ya ƙare tunda yaji tausayina ya ce zai bayar, duk da Kawu Sadi aƙwaisa da masifar son kuɗin tsiya ko matarsa sai ta yi da gaske take ɓanɓarar rabonta abinda dai ya sani shi ne kawai ya ɓoye abinsa, shi ba da sadaka ba balle zakkah.

Babban falon gidan ya ce in zauna, Anisa taji sanyin AC sai tayi barci ni kuwa sai kallon falon nake, wai ace ɗan uwan mahaifiyata ne yake da wannan kuɗin? amma ni har yau har gobe ya kasa samun damar taimakawa Ummanmu ko da jari ne.
can ya fito daga shi sai jallabiya, ya ƙaraso da fara'arsa yana ce wa" kinga ma alwala nayo an shiga sallah, bari inyi sallar sai na dawo in baki saƙon har da kuɗin mota, ki shiga wannan ɗakin kije ki ɗauro alwalar".

na tashi ina masa godiya, na sauke Anisa akan kafet ɗin ɗakin ahankali saboda kada ta tashi ni kuma na shiga ɗakin domin ɗauro alwalar.
ɗaki kamar me saboda tsaruwarsa da kyawunsa, kuma daga gani bama nasu bane wataƙil na Fadil ne domin ayanzu saurayi ne sa'a na ne ma.
Kofar ban ɗakin naji an turo, da sauri na juyo ina shirin ɗaura ɗanƙwalina sai dai me??????
tsoro da firgici suka sanyani kurma wani uban ihu ina firfito da idanuwa.............

INA GODIYA MASOYANA, AƘARA BADA HIMMA WAJEN TAYANI YAƊA WANNAN LITTAFIN DOMIN KOWA YA KARU DA ABINDA KE CIKINSA.

*MRS GREEN GRAPHICS*
MUNA KOYARDA KALOLIN GRAPHICS MASU KYAU DA TSARI KAMAR SU.
Invitation card
Logo
3d mockup
3d render
Cover book
Banner
da dai sauransu, idan kina buƙatar koya kiyimun magana ta lambata kamar haka
07068606171

UMMU MAHER.
[7/1, 11:54 AM] UMMU MAHER (MISS GREEN)🍃: *_💋ƊAN HALAK💋_*

MALLAKAR

*_UMMU MAHER(MRS GREEN)🍃_*

*_AREWA WRITER'S ASSOCIATION📚_*

~*Arewabooks*~
D'AN HALAK:: https://arewabooks.com/book?id=6631fffa0eeb3b80f1ef8159

*Danna wanna link ɗin kai tsaye xaka samu 3k daga tsarin palmpay amma waɗanda basu taɓa buɗewa ba, kisa lambar wayarki zai kai ki inda zaki ɗakko application ɗinsu, idan baki gane ba ki tuntuɓe ni ta lambata 07068606171*
Hey, I use the PalmPay app for free transfers and to get cashback on every transaction. Use my link or my code "SUQD6653" to join and get ₦1000 welcome bonus.
https://link.palmpay.com/34vPB

3
__________Ganin yanayin dana shiga yasa Baba Sadi saurin tura ƙofar banɗakin da yake glass ce, na waje ma ba zai hango duk abinda ya ke faruwa ba.
Ya sanya babban ɗan yatsansa dai dai laɓɓansa, sannan ya ce"shittttttttt!".
yana me zaro manyan idanuwansa waje, jikinsa sai rawa yake yana wani irin smilling na rainin wayo, sannan ya lashe harshensa tamkar yadda asalin ƙwartaye suke idan suka samu cafka. ni kuwa ina rakuɓe sai tafiya nake da baya baya har Allah yasa ya taddani har zuwa inda nake, tuni hawaye suka cika idona ga uwar majinar dana ke ja tamkar an buɗe kogin tafkin maliya.

yana wani banzan murmushi irin na basawa muryarsa tana rawa tamkar rawani ya kunce akan basarake ya ce" inaso ki bani dama in nuna miki zallar abinda yake raina, tun kina ƙaramarki kike burgeni sosai saboda Allah ya yi miki halitta, ga kyau, ga fari, ga kyawun diri, wallahi Humaira ina matuƙar sonki da sha'awarki inaso ki bani dama in dinga ɗaukarki ina kaiko hotel duk abinda kikeso zan miki shi ko menene sh..........."

tun kafin ya ƙarasa nayi wani kukan kura na bangajeshi yayi taga-taga ya faɗa kan jakuxi, na'urar wanka sannan na samu damar buɗe ƙofa ban san ba har na faɗi naji ciwo agoshi na, na yi saurin ɗaukar Anisa dake barcinta hankali ƙwance sai naji dama in dawo Anisa domin ita ɗin bata san komi ba, rayuwarta take cike da kula da jin daɗi bata san wata damuwa ba, ni kuwa ashekara 18 danayi arayuwata na fuskanci ƙalubale da dama, domin duk namijin daya kalleni sai ya kuma kallona, kai hatta jinsina na mata basu daina furta kalmar ina burgesu ba har zuwa kamar rana ta yau basi daina ambaton kalmar burgewa ba.
Gudu nake sosai har na isa bakin titi, gashi ba nida kuɗin mota gashi na haɗa wani irin uban gumi tamkar an tsamoni aruwan sama, sai wulƙita ido nake tamkar wacce ta samu kyautar tsabar sisin naira.
Anisa sai kuka take na goyata ina rarrashinta, na dinga tunani azuciyata ko dai bara zan fara yi ne? domin abincin da xamuci yazu yana nema ya gagaremu dama mahaifiyarmu ke wanke wanke da shara agidan 'DEEN MARSHAL' saboda haka duk wata ake bata kuɗi dubu talatin har da biyar, saboda wanke wanken gidan kamar na buki haka yake ga uwar harabar gidansu duk

faɗinta ita ce take sharewa har tausayinta nake ji.
Kuka nake har nazo gida, amma ina shiga gidan na goge hawayena saboda ƙanwata Amira nasan zan sanyata cikin wani hali, saboda haka sai na wayance har da dariyata kamar na samo wani abin arziƙi, nan kuwa babu abin arziƙi sai na tsiya domin kuwa ban samo komi ba sai bara abulayi bara akufai.
Amira tayi saurin miƙewa ta ce" ya dai!? an samu kuɗin kuwa"?.

na zauna yaraf dani kamar kayan wanki, sannan na ce" uhum naje baya gida ma amma yanzu ya zamuyi Amira"?.
"Anti meye agoshin ki"?.
na shafa ina ɗan wayancewa na ce" uhum faɗuwa nayi ne"?.
ta nuna damuwarta har da miƙomin ruwa me sanyi a aranda, Amira tana matuƙar sona da kuma jin tausayina da tana da hali da ko ƙuda ba zai hau kai na ba.
ta ce" uhum ni ina ganin muje gidan da Umma take aiki kamar yadda na kawo shawara abaya, ita ce dai shawarar da ta rage mana tunda Baba Sadi baya nan wa zamu samu a ƴan uwan Umma? tunda dama sun tsani Baba kinga kuwa babu me taimaka mata, kuma dama kullum suna ƙorafin ta fiya haihuwa".
Ummi tayi caraf ta ce" oho dai dole ayo da ita ai, kullum Umma cikin haihuwa tamkar wata kaz......."
Duka Amira ta kai mata, ta kauce tana ƙunƙuni.

$$$$$$
Ammi ta rintse idonta ta ce"Zaki kazo inason ganinka gobe".
da yake sunan da take kiran Haidar dashi shi ne ZAKI.
ya ɗanyi jim, sannan ya ce" ok in sha Allahu zanzo".
Daga haka bai ƙara magana ba, itama ta kashe wayar ba tare da ta ce komi ba, domin tasan miskilancinsa ba magana zai yi ba sannan daga jin muryarsa yana cike da damuwa sosai.
Ammi tana ajje wayar Mimi ƙanwar Haidar ta ce" Ammi wai me yasa wasu ƴaƴan basa son ganin farin cikin iyayensu ne?".
Ammi ta gane inda maganarta ta dosa amma sai ta nuna bata gane ba ta ce" Mimi ban gane maganar ki ba? waye baya son farin cikin iyayensa? indai ƊAN HALAK, ne ai dole yayi biyayya".
"Ammi gaskiya na tsani bro Haidar, wallahi baya son farin cikinki yanzu ga irinta nan, kullum sai ciwonki ya tashi ni na lura ma so yake ki mutu yayi mun biyu babu tunda ni Abbana ya rasu shi kuma dama baisan zafin uba b..........."
cikin zafin nama Ammi ta kai mata bugu, tun kafin ta ƙarasa maganar da taso yi ɗin Ammi ta nuna ta da yatsanta ta ce" ni zaki faɗawa wannan maganar Mimi? ban faɗa miki banason wannan mugun furucin naki ba? ke da ɗan uwanki amma kina nuna masa tsana? akan abinda bai da laifi aciki, har kina kiransa da wannan muguwar maganar? uban waye ya ce miko baisan zafin uba ba? to don ubanki arziƙin ubansa kike ci ayanzu".
Sosai Mimi ta fashe da kuka, ta tsugunna gaban Ammi gamida riƙe kunnenta cike da yarinta ta ce" ki yafemin Ammi rai na ne ya ɓaci amma na tuba bazan sake ba".

Ammi ta ɗago ta, ta sanya lallausan hannunta tana goge mata hawaye ta rungumeta a ƙirjinta tana rarrashinta tamkar ƴar Baby, sannan ta ce" ko wani bawa da kike ganinsa da kalar ƙaddararsa, bawa baya iya kaucewa ƙaddara saboda haka baki ɗaya rayuwar Zaki rayuwa ce ta jin daɗi abayyana amma abaɗini ba haka bane sam baya jin daɗin rayuwarsa shiyasa ya zaɓi yin rayuwa shi kaɗai, wai don ma yana da kuɗi da babu me kulasa nasan Haidar cikinsa da wajensa yana da matuƙar haƙuri yana son yayi aure amma hakan ya faskara, saboda rikitattan al'amarin daya faru abaya wanda ni nasan shi ɗin ƊAN HALAK ne, amma mutane da dama sun ɗauka ba ɗan halak bane".
Mimi tayi saurin gogewa Ammj hawaye, tana maƙale a ƙirjinta ta ce"Ammi duk nasan da hakan amma banason inga ranki yana ɓaci Silar ɗan uwana, bazan so ace ɗan uwana yana yawan ɓata miki ba domin bana son fushinki ya tabbata akansa domin ko da bakice komi ba Allah yaga zuciyarki kuma abin zai dinga bibiyarsa".

Ammi ta janyo hannun Mimi ta fara nuna mata hotunan wasu mata kyawawa, waɗanda suka amsa sunansu a mata kuma kana ganinsu ka ga ƴaƴan manya.
"Ammi waɗannan hotunan fa"?.
tayi ƴar dariya ta ce" Zaki zan nunawa su ko Allah zaisa adace yayi aure nima ko zan samu jin daɗi domin bana jin daɗin halin da yake ciki kusan shekara arba'in amma ba mata".
"taɓ, ai kuwa Ammi dama bakiyi wannan wahalar ba, domin kuwa nasan ko kallon arziƙi ba zai musu ba saboda kinsan halinsa".
"hakan dai zan nuna masa, sannan in nuna masa ɓacin raina indai har bai zaɓi ɗaya daga cikinsu ba saboda idan na sanya masa ido haka za ayi tayi, sannan iyayen waɗannan yaran sun san komi na rayuwar ZAKI bana tunanin zasu juya masa baya".

badon Mimi ta so ba ta biyewa Ammi, amma sam bata son ɓacin ran ɗan uwanta domin tasan wannan haɗin maimakon yayi masa daɗi sai ma sanyasa damuwa da za tayi.

***
"Anty Salima wallahi ki ƙara tunani, amma bai kamata daga an faɗa miki abu ki hau kai ki zauna ba, domin ni na tabbatar wannan batun na Anti Tahira zancan ƙanzon kurege ne saboda tana baƙin ciki kin samu miji ita bata samu ba, tsakani da Allah da yaya ma kika samu zuciyar Haidar, kinsha wuya sosai har Allah yasa ya fara kulaki yana damuwa da lamuranki, amma don me zaki ce masa wai shi ba ƊAN HALAK bane yo ko ba hakan bane ma menene? Tunda kina sonsa yana sonki menene to? yanzu ke zaki iya cire sonsa acikin zuciyarki"?.

shiru Salima tayi, hawaye masu zafi suka fara zubo mata ta ce" Hanan, wallahi ina cikin matsala wallahi tunda na faɗa masa wannan maganar nake jin ba daɗi har cikin raina wallahi amma na kasa jurewa ne har sai dana faɗa masa, amma yanzu kuma ina cike da nadama me tsanani akan hakan".

"My freind indai har kin yarda ga wayarki danna ki kirashi yanzu, ki tabbatar masa da lallai kinyi laifi ya yafe miki".
Salima taji kamar idan tayi hakan ta zubar da mutuncinta na mace, ga ta matsayin ƴar sarauta

kuma gimbiya Salima taya zata sakko nan da nan ta bawa namiji haƙuri.
"daman nasan baza ki iya ba, biyo bayan girman kanki Allah Salima ki daina wannan girman kan domin zai cutar dake anan gaba, abinda kake so ai baka yi masa wargi". Salima ta tashi tana gyara alkyabbarta da yake yau zata kasance wajen mahaifinta domin neman da yayi mata na gaggawa.

tana fita Hanan tayi saurin ɗaukar wayar Salima, nan da nan ta ƙwashr lambar Haidar tana ta wani mugun murmushi domin Allah ya sani wannan damar ta daɗe tana jira, sai yau da ƙawar ta ta buɗe wayar agabanta taga pin ɗin wayar.
tayi wani shu'umin murmushi sannan ta adana wayarta ta cigaba da binciken wayar Salima, tana yi tana cige leɓe tamkar zata fasa leɓen saboda ita kaɗai tasan irin tashin hankalin da take ciki tun daga ranar da ƙawarta ta sanar mata da wanda take soyayya taci alwashin mallakarsa ta ko'ina, da ta ɗauka zata sha wahala ta ɓangaren Salima amma ayanzu ta tabbatar Salima sokuwa ce ita da kanta zata taimaka mata wajen cika burinta na mallakar namijin maza ZAKI Aliyu Haidar.

*UMMU MAHER CE*
[7/1, 11:54 AM] UMMU MAHER (MISS GREEN)🍃: *_💋D'AN HALAK💋_*

MALLAKAR
*_UMMU MAHER(MRS GREEN)🍃_*

*_AREWA WRITER'S ASSOCIATION📚_*

~*Arewabooks*~
D'AN HALAK:: https://arewabooks.com/book?id=6631fffa0eeb3b80f1ef8159

*_UMMU MAHER BUSINESS CENTER📲_*

*koyon sana'o'i 5 kamarsu*
👇🏻👇🏻
1 MAYAFI NA BEAD WORK
2 MAYAFI NA STONE WORK
3 HULUNA
4 COVER BOOK
5 INVITION CARD

dukkaninsu zaki koya akan 500 ƊARI BIYAR KACAL.

*KIBI WANNAN LINK ƊIM DOMIN SAMUN DAMAR GARAƁARSA SHIGA GROUP ƊINMU👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻*

https://chat.whatsapp.com/CMIWt3cUVvkDAXPthThNQx

4

_________Hanan tayi wani murmushin yaudara sannan ta fita daga masarautarsu Salima tana wata irin dariya me cike da fassarori da dama.

tana ganin ta fito ta duba bayanta ko wani ya biyo ta, tayi maza ta fito da wayarta ta dannawa wata lamba kira.
Can aka ɗaga, taɗan sanyaya muryarta kamar wata marainiya me neman taimako ta fara magana" assalamu alaikum, nasan baka sanni ba Alhaji Haidar amma don Allah inason ka saurare ni wallahi ina cikin wata matsala ne kuma Allah ne zai fitar dani sai kuma kai, wallahi kamar yadda rayuwata ta zama abin tausayi haka taka take duk kuwa da irin tarin ni'imomin da jalla wa'ala yayi maka, kafin ƙarfin komi arayuwa amma kuma kana cikin ƙaddarar rayuwa mafi muni duk wanda ya rasa abokin rayuwa ai ya rasa babbar madafa arayuwarsa, duk da yana da ni'imomi da dama da yayi masa kamar yadda ka rasa abokiyar rayuwa nima haka na rasa, ahalin yanzu miji ya gagareni samu duk wanda yazo sai ya tafi, saboda ana min kallon ba YAR HALAK  bace, ada can baya ina addu'ar Allah ya kawomin wanda zanyi shawara dashi agameda abinda yake damuna, sai gashi cikin ɗan ƙanƙanin lokaci Allah yasa ya kawomin kai cikin rayuwata, don Allah ka ceci rayuwata kada kace zaka ƙi karɓar tayin soyayyata wallahi ni kaɗai nasan abinda nake ji sai kuma Allah sai wanda yasan irin ƙaddarar da Allah ya jehomin ma'ana me irin ƙaddarata kamar kai ɗinnan".

Shiru Haidar yayi, yana tunanin irin amsar da zai bata, gashi kuma Allah ya hanasa kashe wayar domin zuciyarsa tuƙuƙi take tana wani haƙilo gamida amon tafashshiyar wuta na masifa, abin mamaki ma yake basa wato tsabar ya zama tasi no gareji ta yaya za'ace wai mace ta kirasa tana faɗa masa wai itama irin ƙaddararsu ɗaya? wato kowa ma yanzu yasan shi ba ƊAN HALAK bane, ɗan shege ne shi? kai wannan baƙin ciki da yawa yake, shiyasa akullum sai yayi kuka akan wannan mummunar ƙaddarar tasa wacce tun yana ƙarami take bibiyarsa har yanzu, wacce yaci ace yanzu tuni an manta da wani rashin asalinsa, amma tun yana da ƙananan shekaru yake fuskantarsu har zuwa yanzu da yake da kusan shekara 38.

ya goge wata ƙwalla me masifar zafi.

Jin yayi shiru kamar ruwa ya cinyesa yasa Hanan tasha jinin jikinta, da sauri ta katse shirun da ce wa" Allah ya huci zuciyarka yallaɓai, nasan daman ba lallai ne ka karɓi tayina ba, saboda ba nida asali wallahi yallaɓai banyi hakan domin ɓata maka ba, nayi hakan ne saboda na duba gabas da yamma babu wanda na dace dashi sama da kai.........."

Jin ɗib tayi, tun kafin ta ƙarasa ya kashe wayarsa yana jan numfashi me masifar zafi yana ajje wayar akan tamfatsetsen gadonsa ya fashe da wani irin wahaltaccen kuka, duk kuwa da zafin zuciyarsa bai hanashi yin kuka ba, abune mafi wahala wanda zai sanya gadanga ƙusar yaƙi kuka, amma yau sai da yayi me isarsa sannan yayi shiru.

Shi da kansa ya bawa kansa haƙuri, domin yana so yaje wajen Ammi bisa bin umarnin da tayi masa, ta ce kome yake yau yazo.

ya ɓata lokaci da dama yana wanka, yana saƙe saƙe azuciyarsa daga tunani me kyau sai ta koma masa akasin haka, wanda kowacce zuciya idan tunani yayi mata yawa xa kaga tun tana tunani me kyau sai ta koma mara kyau.

yana cikin komin wanka, wanda ruwan har ya taɓa dai dai wuyansa ruwan wankan kalar filawar dake cikin ruwan wato kalar yellow, sai ƙamshi ruwan yake gashi da ɗan ɗumi ɗumi daɗin ruwan yana ratsa dukkanin ɓargo da jikinsa, yana ɗan lumshe idonsa yana buɗewa.

ga tamfatsetsiyar tv wacce take manne jikin bangon haɗaɗɗan banɗakin, wacce yake kallon labaran bbc cikin harshen hausa, yana matuƙar son yarensa Hausa shiyasa aduk tsahon shekara goman da yayi a Italiya bai taɓa barin yarensa ba, saboda shi mutane da dama sun iya yaren hausa, domin duk rashin son maganarsa baya hanashi koyawa turawa yarensa na hausa, duk da shi ba duka bane hausa mahaifiyarsa ita sam bama ƴar nigeria bace, ƴar ƙasar Mali, amma ayadda Amminsa ta faɗa masa mahaifinsa Bahaushe ne abinda ta kasa faɗa masa shi ne asalin waye Baban na sa, wanda akullum wannan shi ne tunanin da yake hanasa barci da sukuni.

abu biyu ne ya kasa fita daga zuciyarsa, na farko wannan baƙin tabon na rayuwarsa, na biyu mutuwar amininsa wanda bai da kamarsa sai Hammud wanda da ayanzu haka suke tare, Triple ake kiransu saboda yadda suka shaƙu da juna, kuma duk a ƙasae Italy sukayi karatu.

MU'AZZAM.
Amini na gari me son ganin wani yayi farin ciki, aminin da baya tonawa amininsa asiri, ga ilimi ga addini, mutum ne wanda ya samu tarbiyyar uwa da mahaifi babansa ɗan asalin Niger ne garin maraɗi, babban malami ne wanda ake ce masa Malam Mousa Ali shahararran malami ne wanda yake da ilimi me yawan gaske, sannan yana da faɗi aji agarin Maraɗi har ma da Niger ɗin baki ɗaya, ɗansa ɗaya namiji aduniya wato Mu'azzam sai ƙannen Mu'azzam ɗin biyu mata sai yayarsa guda ɗaya.

Alokacin da suka haɗu a Italy da faɗa suka fara, domin shi Haidar mutunne marar haƙuri wanda baka isa ka nuna masa yatsa ba, komi girmanka idan ka nemi ka takasa sai kun ƙwasa dashi.

Mu'azzam kuwa mutum ne me masifar haƙuri, yakana, sanin ya kamata, addini da hankali duk babu wanda bai haɗa ba.

yana shigowa makarantar da lafceciyar motarsa me tsari da kyau, baƙa ƙirar jip yayo hanya samɓel yana tafiya yana bin waƙar daya saka ta wizkid me taken ilove u.

Mu'azam yayi gefe, Haidar ya ƙara yin hanyar da yake ya canja wata ma nan ma bata canza zani ba, daga ƙarshe saura ƙiris ya bugesa Allah ya taimakesa yayi gefe da gudun gaske ya faɗa kan wasu green grass waɗanda suke shimfiɗe acikin gefen makarantar waɗanda suka daɗa mata kyau.

cike da mugun fushi ya fito daga motar, alokacin Haidar yana cike da yarinta da kuma rashin sanin darajar ɗan adam domin giyar kuɗi na ɗibarsa.

Bawan Allah yana rakuɓe agefe yana duba yadda duk jikinsa ya kurje, silar faɗawarsa cikin wannan ciyayin tunda tsalle yayi ya faɗa cikinsu.

ya cire gilashin idonsa, ya ƙare masa kallon ƙasa da sama kana ganin Mu'azzam kasan ya cika dukkanin kamalarsa amma kana ganinsa yanayin shigarsa kasan ba ɗan wani bane, hatta agogon dake manne a hannunsa kana ganinsa kasan ba me kuɗi bane.

"wani irin mahaukaci ne kai? so kake na bugeka in baka kuɗin rigistration na makaranta ko?".

Cikin turanci yake masa maganar, yana wani gimtse fuska yana wani ya mutsa ta wai shi me kuɗi.

Mu'azzam bai ce masa komi ba ya karkaɗe jikinsa, ya ƙaraso gar gaban Haidar ya haɗa hannayensa biyu waje ɗaya, gamida maƙale jakarsa a hammatarsa ya ce" yallaɓai kayi haƙuri, ni ba kowa bane kuma ba ɗan kowa ba kuma ni nayi maka laifi kayi haƙuri don Allah".

duk ƙwamdor masifar daya so sauke masa sai da jikinsa yayi sanyi, yana ji yana gani Mu'azzam ya wuce ba tare daya ce masa komi ba.

sai daya daɗe atsaye sannan ya shiga motarsa ya tayar, jikinsa asanyaye yana tuƙi yana tuna abinda ya faru ranar bai je lakca ɗin bama ya koma ƙerarran gidansa wanda ke cikin birnin Italy.

ko rufe ido yayi sai yaga Mu'azzam yake gani, sanyin halinsa da nutsuwarsa sai yaji ya ƙwanta acikin zuciyarsa. tun dama can shi mutun ne me son mutum me sauƙin kai da son mutane amma fa shi halinsa ba haka bane, domin kuwa ko shiga mutane bai son yi shiyasa ko hostel bai nema ba ya siya ƙaton gidansa me matuƙar kyau da tsaruwa.

Washe gari a inda suka haɗu ya tsaya, sai dai duk zaman da yayi bai ko ga ƙurarsa ba, jikinsa yayu matuƙar yin sanyi addu'arsa ɗaya Allah yasa ya gansa.

sai da yayi ƙwana biyu yana zuwa amma bai gansa ba, daga baya sai ya canja shawara ya koma cikin makaranta yana ɗan duddubawa.

Can ya hangosa gindin wata bishiyar filawa me cike da ni'ima yana zaune irin kan kujerun nan na makaranta waɗanda aka ginasu da dutse.

ƙur'aninsa izu sittin a hannunsa yana tilawa, ya yi matuƙar nutsuwa da abinda yake yana cike da ƙanƙan da kai tamkar yana gaban ubangiji.

ya ƙarasa cike da nutsuwa kusa da Mu'azzam wanda ya gama nutsuwa, kamala ta haɗu da ƙwarjini.

Mu'azzam ya ɗago ahankali, domin yaga daɗewar da Haidar yayi atsaye saboda bayason katse sa.

da fara'arsa ya ce"sannunku bawan Allah, kamar kaine wanda muka samu kuskuren fahimta rannan ko"?.

Haidar ya ɗan faɗaɗa fara'arsa ya ce" eh ni ne, nasha wahalar nemanka tun ranar amma sai yau Allah yayi".

ya faɗi maganar agajarce, kuma dama can shi ba irin mutanen nan ne masu yawan magana ba, ko jan magana.

ya matsa masa ya zauna, fuskarsa ɗauke da fara'a Haidar yana ta kallonsa al'amarin bawan Allahn yana burgesa saboda yana da masifar haƙuri.

Haidar ya ce" amma anan kake karatu"?.

"eh anan nake, yanzu shekarata ɗaya da fara zuwa wannan makarantar, ni ɗan asalin Niger ne duka iyaye na ƴan can ne amma mahaifiyata ƴar asalin ƙasar  Mali ce".

"oh, nima mahaifiyata ƴar asalin ƙasar mali ce".

"mahaifinka fa"?.

Sosai kansa yayi nauyi kansa ya fara juyawa saboda jin tambayarsa............

*SHARE*🥰

*$HAIDAR*
*$MU'AZZAM*

*UMMU MAHER*.
[7/1, 11:54 AM] UMMU MAHER (MISS GREEN)🍃: _💋D'AN HALAK💋_*

MALLAKAR

*_UMMU MAHER(MRS GREEN)🍃_*

*_AREWA WRITER'S ASSOCIATION📚_*

~*Arewabooks*~
D'AN HALAK:: https://arewabooks.com/book?id=6631fffa0eeb3b80f1ef8159

*_UMMU MAHER BUSINESS CENTER📲_*

*koyon sana'o'i 5 kamarsu*
👇🏻👇🏻
1 MAYAFI NA BEAD WORK
2 MAYAFI NA STONE WORK
3 HULUNA
4 COVER BOOK
5 INVITION CARD

dukkaninsu zaki koya akan 800 ƊARI BIYAR KACAL.

*KIBI WANNAN LINK ƊIM DOMIN SAMUN DAMAR GARAƁARSA SHIGA GROUP ƊINMU👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻*
https://chat.whatsapp.com/CMIWt3cUVvkDAXPthThNQx

5
__________ganin kamar ran Haidar ya ɓaci game da tambayarsa yasa ya juya hirar da ce wa" wanni course kake karanta"?.

ya ɗan ja wani wahallan yawu sannan ya faɗa masa course ɗin, amma har lokacin jikinsa baki ɗaya yayi sanyi indai har za a masa maganar mahaifi sai yaji duk duniya komi ya sare masa, sai yaji tamkar ya shaƙe kansa saboda haushi, mutane da dama suna masa kallon wanda bai da galihu saboda rashin uba, bai san awata duniya mahaifinsa yake ba? ko sunan mahaifin nasa ma bai sani ba, domin Ammi ko sunan mahaifin nasa bata bari ya sani ba, akullum dai tunaninsa bai wuce ace ta yaya zata ɓoye masa mahaifinsa alhali kuma tasha faɗa masa shi ɗin ƊAN HALAK ne, ɗan sunnah tamkar ko wani ɗa?.

Mu'azzam yana ta yimin hira amma ni ban ma san yanayi ba, hankalina da nutsuwata baki ɗaya yana can kan tunanin halin dana ke ciki, duk kuwa da gata na da komi nawa na rayuwa.

ɗan taɓani yayi, firgigit na dawo hayyacina na kalleshi cikin nutsuwata yana kallona ya ce" bawan Allah ka daina wannan tunanin, domin ita ƙaddara babu yadda zamuyi da ita domin ita ce mahaɗin rayuwarmu, kuma duk wanda kaga Allah ya jarabcesa da wata lalura ko ƙaddara

haƙuri da addu'ah ce kaɗai zata fitar da bawa daga dukkanin ƙaddarar daya faɗa, mafi akasarinmu abinda yasa muke samun matsala arayuwa shi ne rashin cinye ƙaddara domin ita ƙaddara abuce me wahalar gaske, idan ka daure kayi haƙuri sai kaga ka cinye ta".

Haka ya dinga yimin nasiha.

tun daga ranar muka ƙulla abota da Mu'azzam, anan na gane rayuwa bata yiyuwa sai da haƙuri, duk rashin haƙurinka ka sabawarka kanka haƙuri da juriya koda ƙanƙani ne. domin abu na farko daya sanya alaƙarmu yin ƙarfi shi ne haƙuri, domin ni kamar zawo nake sam ba nida haƙuri ko da kaɗan kuwa, amma ahankali sanadiyyarsa ya koyamin halinsa na haƙuri da juriya da yakana da sanin ya kamata.

Tunda nazo karatu ƙasar Italy na daina kiran Ammi, duk wata kafa danasan zata neme ni na toshe ta, domin Allah ya sani na tsani ƙwane-ƙwanen da take min musamman nacin da nake mata na son gaskiyar lamarin ni waye? wanene ubana? A'ina yake? Yana cikin ƙoshin lafiya ko akasin haka? yana raye ko ya mutu?.

Aƙwai wani bature wanda suka saba harkar business da Ammi, dama ita shahararriyar ƴar kasuwa ce wacce ta saba kai kaya daga ƙetare zuwa ƙasata.

babu yadda bai yi ba wajen nemana, amma bai samu damar hakan ba saboda duk wata kafa da zata bashi damar sanin inda nake na rufeta babu damar hakan.
ni aganina ana fushi da uwa azauna lafiya, rannan muna zaune da Mu'azzam yana ƙara min karatun islamiyya littafin ahlari, wayata tayi ƙara kamar bazan ɗauka ba sai na ɗauka ɗin.

Fashewa da kuka Ammj tayi, atake naji wani abu tamkat mashi ya faɗomin akaina silar jin muryar mahaifiyata, jikina yayi sanyi domin ko ba ita ba banason jin kukan mace tausayi yake bani gamida kashe jiki.

"yanzu Haidar ka kyauta kenan? kasan kuwa irin wahalar dana sha wajen neman lambarka? wallahi na rasa me kake so ka zama Haidar? wa yake zugaka ne? kasan kuwa halin da na shiga? tsawon wata huɗu kenan amma sam na gaza samunka? me hakan yake nufi? Shin kana fushi dani ne saboda abinda ƙaddara ta riga fata"?.

Shiru nayi, na kasa bata haƙuri ko in ƙwantar mata da hankali saboda banason buɗe bakin ma ballantana har inyi maganar da zata ɓata ranta, kawai sai na kashe wayar ma baki ɗaya.

Mu'azzam ya ce" yallaɓai ka gafarceni idan na kasance me laifi agareka amma inason inja hankalinka, kan wani kogin kuskure danaga kanasan faɗawa su iyaye suna da muhimmanci da girma, musamman ma uwa shiyasa Manzon Allah (S.A.W) ya ce kabi uwa kabi uwa har sau uku, sannan ya ce kabi uba. saboda muhimmancinta arayuwa Manzon Allah (S.A.W) ya ce da zaka ɗauki mahaifiyarka zuwa umrah, ka zagaya ka'abah da ita agoye abayanka sau babu adadi, bai kai ya haihuwarka da tayi ba shiyasa uwa take da wannan falalar, amma Haidar ba'a

fushi da uwa ka kiyaye fushinta akanka, yanzu in baka misali yanzu ba jarabawa kukayi ba ka faɗi kakeson zana wata? kuma alhali ada kanada ƙoƙari sosai? sanadin hakan yanzu gashi ba kada wani kataɓus akan hakan kuma wallahi ko kaffara bazanyi ba nasan wannan laifin da kayi mata shi ne ya hanaka cin wannan jarabawar, tunda ada ka saba kome zakayi sai ka nemi shawararta, ita kuma ta sanya maka albarka saboda haka ina me jan hankalinka da ka kiyaye fushin uwa domin ba abune na wasa ba".

Nasiha me ratsa jiki ya dinga yimin, daga ƙarshe na ɗauki nasiharsa na kira Ammi muka sasanta nayi ta bata haƙuri, da kuma nuna mata nayi kuskure.

sosai nayi sabo da Mu'azzam, saboda na gane zama da aboki nagari yana ƙara maka hasken makarantar rayuwa.

Ranar da bazan taɓa mantawa da ita ba, ranar da na nemi Mu'azzam amakaranta na rasa ranar ban taho da masu tsaro na ba, hankalina ya tashi domin nima ba ko'ina na sani agarin ba balle in tafi nemansa, sau tari ko ba ranar makaranta ina shigowa don kawai naga Mu'azzam, nasha bashi shawara akan ya koma gidana amma yaƙi ya ce inyi haƙuri zamansa anan yafi ye masa.

duk wanda nasan zan tambaya na tambaya, amma shiru babu labarinsa wayarsa na kira yafi sau shurin masaki amma shiru ba a ɗaga ba.

Bansan lokacinda naji wani zazzaɓi ya rufeni ba, jikina ya hau ƙerma. ganin zazzaɓin na neman kaini ƙasa yasa na bugawa bodyguard ɗina na ce suzo su kaini gida.

suka kiramin likita ya dubani, sannan na samu barci acikin barcin nawa na dinga mafarkin Mu'azxam wai yana cikin wani hali, yana neman taimakona amma na kasa basa, sai kuka nake shima yana yi dai dai lokacin na tashi daga barci tamkar wanda aka ƙwarawa ruwa jikina ya jiƙe sharkaf, ga sanyin AC amma tamkar babu wata alama ko kafar da iska take shigowa ta ɗakin.

Allah ya taimakeni na samu na tashi na shirya, banyi wani cikakkan shiri ba na fito zuwa makaranta, ina addu'ar Allah yasa Mu'azzam ya dawo.

Innalillahi wa inna ilaihi raji'un.

abinda bakina yake iya furtawa kenan, saboda nauyin da yayi min daga baya naja bakina nayi shiru tashin hankali fal jiki da ruhi.

domin na tambayi ƴan hostel ɗinsu sun tabbatarmin Mu'azzam bai dawo ba, suma kuma tun jiya suke nemansa amma basu gansa ba, kuma gashi wayarsa da glass ɗin idonsa duk suna nan, da yake yana sanya gilas a idonsa saboda yana da ƴar matsalar ido.

Ganin hakan yasa na bazama nemansa, wajen ƴan sanda na wuce kai tsaye na shigar da report nan da nan suka fara bincikar case ɗin, ni kuma na dawo gida saboda na gaji sosai gashi

kuma ban saba tuƙi ba duk inda zanje kaini ake, saboda haka naji duk jikina yayi lugub tamkar wanda aka daka a turmi.

*BAYAN ƘWANA BIYU*

Labarine yazomin da ɗumi ɗuminsa, wai anga Mu'azzam awani gida babu numfashi, wasu mutanene suka kamasa amma yanzu da suna hannun ƴan sanda ana tuhumarsu.

Bayan an kai shi asibiti aka dubasa aka tabbatar lafiyarsa ƙalau sai gajiya da yayi sun hanasa ruwa da abinci.

mutum uku ne, kuma duk baƙar fata na dinga kallonsu ina musu Allah wadai domin sun bani mamaki matuƙa irinsu ne masu lalata mana suna ace duk ƙasar da baƙar fata yaje sai ya zama wani mugun ƙusan rashin mutunci.

Duk tuhumarsu da ake baku faɗi gaskiya ba, ce wa suke su bazasu faɗi wanda ya aikosu ba da yake ƙasar turawa ce sai aka ƙara barinsu su huta aka daina matsanta musu, aka biyo musu ta hanyar dabara da wayo aka barsu ba tare da an ƙara tuhumarsu ba, akayi musu ɗaurin talala har da abinci me kyau da ruwa ake basu.

Alokacin naji haushi sosai, sai nake ganin kamar basuyi mana adalci ba ya za'ayi masu laifi a barsu tamkar masu aikin lada? amma dana faɗawa Ammi halin da ake ciki ta tabbatarmin sanya musu ido suka ƙarayi domin da sun saki jiki shi wanda yasanyasu zai kawo kansa da kansa tunda yaransa ne.
Haka na ɗauki shawarar Ammi, na cigaba da faɗawa Allah akan ya bayyana wanda ya yiwa Mu'azzam wannan mugun ƙullin, sai gashi kuwa rana tsaka su da kansu yaran sun faɗi waye.

nemansa aka duƙufa dayi amma tuni ya ɗaga zuwa Nigeria, sai dai da passport ɗinsa aka fara bincikarsa, aka gano ashe ɗan jami'armu ne ma wani ɗan ƙusar gwamnati ne yaron bayajin magana ko kaɗan, kuma karatun ma da aka turosa bai tsaya yayi ba, sai shashanci da bin abokan banza da kuma lalata ƴaƴan mutane waɗanda sukazo daga Nigeria da ƴan sauran ƙasashe.

Ranar har hawaye nayi, saboda tausayin Mu'azzam to me yayi musu? me ya sanyasu yi masa wannan abin? abinda ya sanyani kuka bai wuce yadda olsa tayi masa mugun kamu ba, gashi idonsa baya gani sosai saboda ya saba mu'amala da gilashin idonsa, gashi shi ba ɗan kowa ba balle a ƙwato masa ƴanci, amma ni nayi alƙawarin kama wannan yaron aɗauresa har ƙarshen rayuwarsa.

Ganin yadda nake hawaye yasa Mu'azzam dafa kafaɗata ya ce" Haidar wai mi yasa kake da zuciyar mata ne? me yasa kake zubar da hawayenka akaina? banason kana zubar da hawayenka akan wani, domin idan kana haka zama da mace ma bazaka iya ba idan har tasan

kana da rauni akanta, kuma ina me tabbatar maka na yafewa wanda ya aikatamin wannan laifin, domin nasa yayi ne sanadin wani abu nashi wanda ni na cucesa ba shi ya cuceni ba, domin awani hadisi an rawaito ce wa 'WALA TAJASSASU' ma'ana kada mu yawaita bincike. yin hakan zai iya jefamu cikin babbar matsala".

Da sauri na kallesa wai jin cewar ya yafe masa, naji baki ɗaya idona ya ƙafe hawayen ma sun tafi wannan wani irin bawa ne me yafiya, me haƙuri"?.

"Haidar nasan kana mamaki dana ce na yafe masa, Annabin tsira yana son mutum me yafiya domin muma munawa Allah laifi ya yafe mana".

Na buɗe bakina da niyyar yin magana sai ga................

*SHARE🥰*

*$HAIDAR*
*$MU'AZZAM*

ƊAN HALAK GRP LINK
https://chat.whatsapp.com/LcnDvlFNqL0Enq7IlnpAVe

*UMMU MAHER*
[7/1, 11:54 AM] UMMU MAHER (MISS GREEN)🍃: *_💋D'AN HALAK💋_*

MALLAKAR
*_UMMU MAHER(MRS GREEN)🍃_*

*_AREWA WRITER'S ASSOCIATION📚_*

~*Arewabooks*~
D'AN HALAK:: https://arewabooks.com/book?id=6631fffa0eeb3b80f1ef8159

*_WELCOME TO UMMU MAHER BUSINESS CENTER_*
______¥¥¥¥¥¥¥

*TIME TABLE NA KOYON SANA'A*

CLASS 1👇🏻
______________

*KOYON MAYAFI NA BEAD WORK BEAD WORK*
*MAYAFI NA STONE WORK*

*HULUNA*
*RIGUNA*
*FANTIS*
*WANDO JEANS*
👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻
~Naira~ 800

CLASS 2👇🏻
_______________
*INVITION CARD*
*3d logo*
*3d mockup*
*3d render*
*Cover book*
👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻
~Naira~  800

CLASS 3
__________
*Turaren wuta*
*Humrah*
*Gyaran jiki*
👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻
~Naira~ 1k

a tuntuɓi ummu maher ta lambarta👇🏻
07068606171

*DOMIN SHIGA WHATSAPP GRP ƊINMU👇🏻*
https://chat.whatsapp.com/CMIWt3cUVvkDAXPthThNQx

6
_________da sauri na kalli wanda ya shigo, na haɗe  rai jikina har ɓari yake saboda ruwan masifa idanuwana suka canja kala asalin Haidar ɗina ya bayyana baki ɗaya.

"Mu'azzam anya kana da hankali kuwa? wannan fa shi ne wanda naga an rataye hotonsa a wajen folis shi ne wanda ya sanya ka wannan jinyar alhali bakaji ba baka gani ba? To yanzu kuma meye ya kawosa wajen nan? ai kuwa yau aƙwai Inda ba ƙasa"..............

maimakon naga ransa ya ɓaci sai ma naga yayi murmushi mai ma'anoni da dama, ya ƙaraso kusa dani ya ce" Bro Haidar, ka daina kumfar baki domin shi wanda na yiwa abun ya daɗe da yafemun, wallahi ban taɓa ganin bawa me masifar haƙuri irin Mu'azzam ba, bawan Allah ne wanda bai damu da kowa ba, ban taɓa yin tunani akan duk abubuwan dana ke aikatawa ba,

ban taɓa tunanin zanyi abun yazo ya dameni ba Mu'azzam ya yafemun yanzu kai kaɗai ya rage Haidar, domin Mu'azzam ya nunamin muhimmancinka arayuwarsa, ya faɗamin tamkar Hassan da Usaini kuke, jini ɗaya ciki ɗaya don Allah ka taimaka ka yafemun".

Haɗa hannayensa waje ɗaya yayi yana neman yafiyata, sai naji duk masifar dana tattaro ta koma na samu waje na zauna, ko dama ni can hukuma ne sai da rarrashi inada zuciya sosai wacce idan ina cikinta bana iya gane hagu balle kuma dama, haka nake rayuwata ni kaɗai ba nida wani aboki wanda zance ina iya gayawa sirrina, ko ayanzu danake jin Mu'azzam tamkar jinina ba komi ya sani na sirrin rayuwata ba, saboda ni mutum ne me masifar zurfin ciki, da wuya kaji cikina in har ba laɓewa kayi kaji saƙon zuciyata ba, ko kuma akayi wani abun agabanka to shi ne zaka ɗorar da wani abun.

na kalli Mu'azzam yana zaune akan gado, yayi wata irin muguwar rama tamkar wanda ya daɗe yana jinya, abin tausayi dai sai naji dama in koma me irin zuciyarsa saboda nasan mutum ne shi me masifar haƙuri da sanin ya kamata, babu ruwansa da rayuwa balle ƙele ƙelenta. nasan kome zanyi bazan taɓa komawa irin zuciyarsa ba saboda dama ni can mutum ne me masifar zuciya balle lokaci ɗaya in canja ta nasan ba abune me yiyuwa ba, sai dai in zama me yafiya ko iya wannan ma na tsaya na daki wani makami na siraɗin rayuwa wajen hayewa da tsani me kyau.

na buɗe bakina tamkar me ciwon baki na ce" ba komi na yafe maka, tunda wanda aka yiwa laifin ya yafe, kaga ni ƙarashe ne nawa saboda haka na yafe maka Allah ubangiji ya yafe mana baki ɗaya".

Sosai naga farin ciki akan kyakkyawar fuskar Mu'azzam, abun ya bani mamaki sai ya shiga bani tausayi kuma, saboda nasan duk inda me haƙuri ya kai to Mu'azzam ya kai kuwa.

abinda yake min yawo bai wuce abinda ya janyo wannan yaƙaddamar ba, tunda ni nasan shi ba mutum ne me faɗa ko neman masifa ba, da dai nine sai ince zan aikata tunda nasan yadda na iya fitina da tada zaune tsaye, domin ɗan abu kaɗan zaka yimin in tada zaune tsaye.

"ina son jin abinda ya kawo wannan taƙaddamar"?.

ɗan murmushi duka sukayi, Mu'azzam ya ce" ni ne da laifi Haidar ni na shiga gonarsa domin bai sakoni a harkarsa ba ni na shiga nayi kane kane, duk abinda babu ruwanka daɗin ji gareshi ban zama me kauda kai akan ɓarna ba, daman ni can haka nake in har za'ayi abinda ba dai dai ba agabana zan faɗi gaskiya, amma ta cikin nutsuwa da neman maslaha nake komi, amma inason ya faɗa maka komi da bakinsa kada na faɗa ba dai dai ba kasan na fara jin sauƙi kada na karkace in faɗo ƙarya".

dukkansu sukayi ƴar dariya.

"Sunana Hammud Mai Nasara, mahaifina yana da kuɗi sosai ta inda baka tunani amma halin

rayuwa yasa yanzu ya samu karayar arziƙi, ina ɗaya daga cikin masu safarar miyagun ƙwayoyi daga wata ƙasar zuwa Nigeria, na tara kuɗi sosai ta wannan harkar bana tsoron kowa harkar gabana kawai nake, mahaifina yayi yayi in daina wannan harkar naƙi na daina, alhali ni kaɗai ne ɗansa namiji wanda yake tunƙaho dashi gashi ina karatu wanda daga baya na daina karatun ma baki ɗaya, abinda ya kawoni na daina sa sai shashanci da kule kulen ƴammata, babu ruwana da karatun da mahaifina ya ƙwallafa rai akansa ayanzu haka silar abinda nake ya sanyawa mahaifiyata mummunan hawan jini, Mu'azzam shi ne mutum na farko daya karyamin alƙadarina saboda babu wanda yake iya kallon cikin idona ya faɗi laifina sai shi, depertment ɗinmu ɗaya dashi ganin bana karatu yasa ya ke janyonu ajiki tare da nunamin abinda nake bai kyautu yinsa ba, amma na rufe kunnuwana na sanya musu toka na daina ganin kowa da jin komi, ahaka har na daina zuwa makaranta jin na daina zuwa yasa Mu'azzam bibiyata yaji ina nake zuwa? babu inda bai tambaya ba kowa yace baisan inda nake ba, har aka samo wani ya faɗa masa amma ya nemi daya ɓoye sunansa domin kowa tsorona ya keji, ahaka yazo ya sameni ya dinga yimin nasiha, ko ɗaya ban ɗauki nasiharsa ba sai ma niyyar fansa danaso ɗauko akansa, saboda sanin inda nake da yayi zai iya tonamin asiri domin wannan ƙasar ba irin ƙasarmu Nigeria ba ce, duk harka da manya da kake idan har kayi laifi ko kai waye sai an ɗauki mataki akanka, daga nanne na sanya aka ɗakkominshi nayi ta azabtar dashi, amma da yake Allah ba azzalumin bawansa bane sai gashi ya shiryenu cikin gaggawa, aɗan zaman danayi dashi haka ya cigaba da yimin nasiha duk da ina azabtar dashi ta ko'ina amma bai gajiya wajen daina yimin nasiha ba, cikin nasihar tasa yana yawan faɗamin.

_KAJI TSORON ALLAH HAMMUD, KA SANI ITA DUNIYA BA WAJEN ZAMA BACE WAJEN ARO CE DOMIN SHI KANSA RAN ARO AKA BAMU, BA DON ARO AKA BAMU BA DA TUNI BABU MUTUWA TUNDA RAN NAMU NE, SANNAN DUK ABINDA KAKE KA TUNA DA CE WA ALLAH YANA GANINKA, KAJI TSORON ALLAH KA GYARA MU'AMALARKA DA KOWA DUK DA WANI KO GOYASA ZA KAYI VA ZAI DAINA JIN ZAFINKA BA TUNDA DAMA KOWA YANA DA MAƘIYI, TUNDA MANZON TSIRA YAYI MAƘIYA DOLE KOWA MA YAYI SU SHI DA ALLAH YA WANKE BAI TAƁA LAIFI BA, KAJI TSORON ALLAH KA TUNA RANAR MUTUWA. RANAR DA ZA A ƊAUKEKA BA KADA BAKI  BA KADA IDO BA KADA HANNUN AIKATA LAIFUKA IDAN KAYI AIKI NE KYAU KAYITA KUKA KANA CEWA KADA SU KAIKA, IDAN KUMA KAI ƊAN ALJANNA NE KAYI TA MURNA ZA A KAIKA INDA ZAKA HUTA DA FITIN TUNU DA WAHALAR RAYUWA....._

ire iren waɗannan nasihun yake mun, bai taɓa gajiyawa ba har Allah yasa ayanzu na gane komi ina kuma roƙon Allah ya shiryi dukkanin masu hali irin nawa, Allah kuma ya daɗo irin masu halin Mu'azzam domin da ana samun irinsu da munafunce munafunce baiyi yawa ba".

Tun daga wannan ranar muka zama abokai, duk da bayan lokacin sai da Hammud ya shiga hannun hukuma tunda ba irin ƙasarmu Nigeria bace, ko da kaida kayi report ka yafe to suma suna da hakki, idan baka haɗa da addu'ah bama har gidan yari zaka tafi tunda su can laifin gidan yari ba wahala ne dashi ba.

Bayan an gama shari'ah bisa addu'ar da muka dingayi Allah ya taimakesa da kansa sukace ta

tafi.

Mun haɗe kanmu tsintsiya ɗaya maɗaurinki ɗaya, saboda haka a makaranta aka sanya mana suna TRIPLET ƴan uku kenan, kowa da haka ya sanmu duk dani halinmu ya banbanta dasu domin su suna da haba haba da jama'ah, ni kuma sam ba nida fuska kullum fuskata aɗaure, sannan ba nida sakin jiki da kowa idan ba da triplet ɗina ba, bana shawara da kowa sai su Mu'azzam yana ƙara mana karatu sosai cikin ikon Allah sai gashi har mun haddace ƙur'ani azaman shekara 6 da mukayi tare.

cikin abinda na ɓoye musu shi ne asalina, ban taɓa nuna musu ni ba ƊAN HALAK bane, duk wanda yake hirar mahaifinsa sai dai ni inyi shiru saboda ba nida abinda zance sai dai damuwa ce fal araina domin nasan ina cikin rayuwa mafi tsanani.

Domin acikin babbar ƙaddara ta rayuwa rashin fitowa ta hanya tsarkakkiya ita ce babba, domin kowacce ƙaddara ta biyo bayan wannan domin su iyayen da suka aikata ɓarnan basa jin daɗi da kuma rashin ƙwanciyar hankali, sannan uwa uba shi yaron daya zo ta wannan hanyar rayuwarsa na lalacewa ne tamkar dai yadda abinci yake lalacewa idan yayi wasu ƙwanaki.

asannu duk zurfin cikina suka gano komi, sun tayani alhini kuma sun shiga cikin tashin hankali fiye da yadda nake ciki, saboda suna ɗaya daga cikin manya manyan masoyana.

mun gama makaranta lafiya, kowa yana ta murna amma mu muna cikin tashin hankali na rabuwa da juna, har gwara ni da Hammud saboda muna ƙasa ɗaya state ɗaya, shi kuma Mu'azzam yana wata ƙasar daban duk da muna kusan maƙota da Niger, har tsokanarmu akayi tayi.

*BAYAN RABUWA*

Haka kowa ya dawo gida, sakamakonmu yayi kyau sosai tunda dukkanin bama saka wasa adukkanin harkokinmu, Mu'azzam yana yawan ziyartarmu akoda yaushe har na bashi shawara ko zan bashi manaja a kamfanina, tunda ni da kaina inada kamfanin da bansan adadinsu ba a ƙalla zasu kai ɗari ko ma sama da haka domin ina da dukiyar da nima ban san ta yadda aka samota ba, tasowa nayi na sameta na cigaba da kula da ita ban fara tsorata da rayuwa sai bayan dawowa ta daga ƙasar Italy, rayuwata ta zama abar farauta domin duk waɗanda Ammi ta ɗora kan kasuwancina macuta ne ta yadda suka dinga aikata ɓarna babu ruwansu, domin sai yadda sukayi da Ammi kuma ko sisi basa kawo mata, domin ita bata ma damu da kuɗin ba tunda tana dasu har ta rasa ma yadda za tayi dasu.

Ganin wannan ɓarnar yasa duk na koresu na ɗauki aminai na Mu'azzam da Hammud suka zama masu kula da komi sai dai ni inzo kawai in duba, sannan ina kula da hada hadar kasuwancina na ƙasashen waje...............

*SHARE🥰*

*$HAIDAR*
*$MU'AZZAM*

ƊAN HALAK GRP LINK
https://chat.whatsapp.com/LcnDvIFNqL0Enq7IlnpAVe

*UMMU MAHER*
[7/1, 11:54 AM] UMMU MAHER (MISS GREEN)🍃: *_💋ƊAN HALAK💋_*

MALLAKAR
*_UMMU MAHER(MISS GREEN)🍃_*

*_AREWA WRITER'S ASSOCIATION📚_*

~*Arewabooks*~
D'AN HALAK:: https://arewabooks.com/book?id=6631fffa0eeb3b80f1ef8159

7
_______Mu'azzam da Hammud suna iya bakin kokarin su wajen gina wannan rusassun kamfanonin da aka lalata, nan da nan sai gashi an samu tsabar zunzurutun kudaden da ba'a taɓa samu ba, hankalina ya kwanta da aikinsu, saboda sam basa nuna min mugunta suna zaune dani tsakani da Allah.

A wata ranar juma'ar da bazan taɓa mantawa da ita ba, ina zaune a babban ofis ɗina na ƙasar Faransa sai naga kira daga wata lambar da bansan ko waye ba?.

Mutum uku ne suke da lambata ta ƙasar waje, Mu'azzam da Hammud sai kuma Ammi wacce itama bata daɗe da sanin lambata ba, domin sai da Mu'azzam yayi yaƙi dani Sannan na bawa Ammi lambata.

"Hhhhhhh".

Dariyar dana ji ce ta bani mamaki sosai, sai naji gaba kid'aya kasalar dana keji ta ƙaru sosai, na buɗe baki da niyyar yin magana sai naji Muryar wani mutumi wanda tabbas nasanta amma halin mantuwa na manta inda na sansa baki ɗaya.

"Haidar"....

Jin sunana yasa naja wani numfashi me cike da jin daɗin kiran sunana, sai daga baya ne kunnuwana suka jiyomin wani mummunan lamari, wanda yasa na tashi amatsanan mugun bugawar zuciya, wanda ta sanya gangar jiki da ruhi acikin wani mummunan yanayi.

"dama na kira ka ne da babban murya, Haidar wannan sanya idon naka yayi yawa kai da amininka Mu'azzam ina ƙara faɗa maka kayi a hankali kayi a sannu kuma domin ayanzu haka ka haɗa ruwa da wuta awaje ɗaya, wanda sai nan gaba ne zaka gane dukkanin abinda ake nufi, amma ahalin yanzu dab Mu'azzam yake da bankwana da duniya, domin wannan wutar da ka haɗa shi da ita ta kusa cinyesa baki ɗaya har ƙashin ɓargonsa".............

Tun kafin ya ƙarasa na gaza haƙuri zan hau masa ka, da sauri ya kashe wayar kaina ya ruɗe baki ɗaya, na rasa wani irin tunani zanyi ne? To me wannan mutumin yake nufi? Matsalar dana shiga abaya ita ce zata dawo yanzu? Duk wanda na ɗora a kamfanoni na mutane masu amana sai kaga sai wani mugun abu ya faru dasu, ko dai a kashe su ko kuma a lahantasu, Misali akwai waɗanda da dama sukayi hauka, wasu kuma ciwon laka wasu ciwon wuya.

Wani irin ɓacin rai ne ya ziyarce Ni acikin daƙiƙun da basu fi uku zuwa huɗu ba, na samu waje na zauna ina tuno tunatar War Mu'azzam a kaina akan duk damuwar dana ke ciki in miƙa lamurana ga sarki Allah, sannan inyi ta maimaita Inna lillahi wa Inna ilaihi raji'un.

Kalmar danayi ta ambatawa kenan har Allah yasa naji nutsuwar zuciya.

*Bayan wasu awanni*

A mugun kiɗeme na fito nayi hanyar gidana dake cikin kasar Farisa, ko gabana bana gani sam baki ɗaya naji zuciyata tayi min zafi tamkar tafasasshiyar wutar gashin tsire.

Mutuwar Mu'azzam ta tarwatsa dukkanin wasu notikan kaina, adaren nayi bisa na dawo ƙasata ta haihuwa Nigeria tare da ɗimbin tashin hankalin daya gaza wassafuwa azuciyata da gangar jikina, lokaci ɗaya na fita daga hayyacina na rame sosai.

Abirkice na shigo kamfanin yayinda na sameshi cike da mutune, ana ta tayani baƙin ciki a fuska, Hammud na hango zaune ya haɗa uban tagumi sai haɗiyar zuciya yake babu ma ruwan hqwayen sai kukan zuci da wasi wasi.

Yana ganina ya taso da mugun sauri yayo kaina, dukkaninmu muka saki wani irin kuka me ban tausayi, sai da muka yi ne isarmu sannan muka yi shiru.

Ko gawar Mu'azzam ba a gani ba, domin a inda yayi hatsari motar ta kama da wuta sai toka aka ɗiba aka yiwa addu'ah.

Na shiga tashin hankali sosai, Hammud ma ya shiga damuwa mu biyu muka haɗu muka ta bawa juna haƙuri har Allah yasa muka rage damuwar.

Hammud ya shiga tashin hankali bayan ya koma aiki, saboda ya saba sosai da Mu'azzam sai ya zamanto komi yayi baya harkar cinikayyar ta ja baya, saboda shi wanda yake kula da dukkanin al'amuran ya zama abin a tausaya wa.

Su kura masu jiran Nama, su Alhaji Hadi aka cigaba da tafiyar da harkoki cikin almundahana da aikata ɓarna da kuɗin da ko kusa ba suda gadonsa.

Da ƙer na fara dawowa hayyacina, har Allah yasa na samu nutsuwar zuciya nayi tafiya zuwa Niger bisa kwatanta Mu'azzam wanda ya bani wasiyya tun kafin ya rasu.

Nayi tafiya na dawo lafiya bayan na cika mahaifinsa da abin arziki domin tun kafin in taho sunsan da rasuwar Mu'azzam ɗin. Bayin Allahn sun bani tausayi sosai mahaifinsa da ƴan uwansa mata waɗanda suke ciki ɗaya, domin sun shiga damuwa sosai.
Mahaifinsa har na taho bai daina kuka ba, domin shi kaɗai ne ɗansa namiji wanda yake matuƙar so da ƙauna.

*Cigaban labari*

______da mugun sauri na farka daga nannauyan tunanin dana daɗe ina yi, jikina har ɓari yake nayi wankan na fito.

Wajen Ammi na fara zuwa saboda dama ta ce tana nema na.

A babban falonta na same ta, ita da wata mata ban wani tsaya ba na wuce zuwa saman bene, saboda yana yin tunanin danayi ɗazu ya dawo mun da komi daya wuce, mutuwar Mu'azzam ta dawo sabuwa fil azuciyata.

Abakin rantsatstsan gadonta na zauna, duk jikina asanyaye saboda Ni mutun Ni ne masifar

saka damuwa araina.

Ta ɗan daɗe kaɗan a kaina, tana nazarina sannan ta ƙaraso cike da kuzari ta zauna kusa dani, uwa kenan ita kaɗai ce take gane yanayin damuwar zuci da ta fuska, sai da ta ƙaremin kallo sannan ta ce

"Haidar
Wani abu na damun ka ne"?.

"Babu komi Ammi".

Daga nan ban ƙara magana ba, itama taja bakinta tayi shiru domin kuwa tasan ba lallai ne in ƙara magana ba.

"Haidar don Allah inason ka rage damuwar da take damunka, duk fa bawan da ka gani a gidan duniya da irin ƙaddararsa kuma haka yake amsar ta ayadda tazo masa hannu bibbiyu, amma sam Haidar baka cikin bayin da suke da yarda da ƙaddara, ka zama me yarda da ƙaddara me kyau ko mara kyau idan kaga rayuwar wani sai ka tausaya masa, saboda ƙaddararsa ta munana amma ahaka ya karɓe ta saboda ya samu ya tsira kuma ya dace, yarda da ƙaddara yana ɗaya daga cikin shika shikan musulunci, bawa baya cika na kwarai har sai ya kasance me yarda da ƙaddara, Haidar ban taɓa zama na baka labarina ba shiyasa bakasan wahalar danasha a rayuwata ba, amma lokaci da zai zo da zan bayyana maka asalin Ni wacece sannan kaima kasan Asalinka".

Har lokacin bance mata komi ba, taja nunfashi alamar tanason yimin magana domin duk lokacin da kaga Ammi taja nunfashi akwai Magana me muhimmanci da take son yimin.

Wasu hotuna ta ɗakko kamar diary, ta miƙomin gami da ce wa" karɓi ka buɗe ka gani".

Tamkar raƙumi da akala haka na buɗe, na fara cin karo da hotunan kyawawan y'ammata, waɗanda suka amsa sunan su kuma daga ganinsu ma yaran masu shuni da hannu ne domin ko kusa babu ɗigon talauci ajikinsu.

Tun ban gama ba na ce" Ammi wannan kuma fa"?....

Tun kafin in ƙarasa ta ce "cigaba da dubawa dai ina ganin akwai wacce zata yi maka cikinsu".

Wani mugun malolon baƙin ciki ne ya tsaya min, wato har na kai lokacin da za a dinga min tallan mata? Raina ya ɓaci amma saboda mahaifiyata ce babu yadda zanyi.

Na tashi tsaye, gami da zuba hannuna cikin aljihu na juya bayana sannan na ce" Ammi shi

aure da mutuwa lokaci ne, banason auren macen da banaso, domin shi aure ba a yiwa ɗaya tilas kiyi haƙuri Ammi amma babu wacce tayimin a cikinsu".

Ban ƙara tsayawa ba na fito kai tsaye direbana ya buɗe min mota na shiga zuciyata na yimin wani irin tururi yanzu har lokacin tallah na agari yayi? Wata ƙila ma Ammi ce ta bawa wacce ta kirani jiya lamabata, sam zuciyata ba daɗi asalin Haidar ɗina ya bayyana sak a fuskata..........

$$$$$$

Tare muka tafi Ni da Amira gidan da Umma take aiki, da ƙer me gadin gidan ya bar mu muka shiga kai tsaye muka wuce wajen masu aikin gidan.

Iya Abu muka tarar tana girki akicin, muka gaisheta sai ƙara kallon gidan nake saboda tsabar kyawunsa da tsaruwarsa abin sai wanda ya gani, kicin kamar aljannar duniya.

Bayan mun gaisa take tambayar mu mahaifiyarmu ta haihu kuwa?.

Muka bata amsa da eh ta haihu, amma tana asibiti babu kuɗin sallama.

Jikinta yayi sanyi ta ce" kai Allah ya tsinewa wasu mazajen wallahi, sam ba suda tausayi bare imani, yanzu ace matarka tana asibiti amma saboda tsabar salalan tsiya ka kasa biya mata kuɗin asibiti? Kai Allah dai ya gyara wallahi, shiyasa na kashe auren nayo nan saboda mutanen gidan nan akwai kirki wallahi ba dai ka nemi abu ka rasa ba, yanzu dai bari inje in faɗawa Hajiyar nasan za a dace in Sha Allah".

Tana shiga cikin gidan muka fito daga babban kicin ɗin wanda yake manne da babban falonsu.

Muna fitowa Amira ta shiga kallon gidan, tana riƙe da haɓarta tana santi na dungureta ta dawo hayyacinta da sauri.

Ta ce" ayyah anty wallahi gidan nan kullum kamar ana ƙara masa kyau, dubi fa yadda aka canja masa wani hamshaƙin fenti tamkar gidan y'an katun"?.

Muna haka Iya Abu ta fito jikinta duk asanyaye, Ni kuwa cikina sai kaɗawa yake saboda bansan me ya faru ba.???

_IYA ABU_

Kai tsaye wajen Hajiya babba tayi, saboda Hajiya ƙarama bata nan itace amarya kuma tana da

kirki sosai saɓanin Hajiya babba, sam bata san darajar mutane ba da ita da yaranta ba suda mutunci yadda suke murza talaka tamkar lokacin murza bayi..........

*Ayi haƙuri jina shiru, na canja wayane sai danayi settling ɗin komi*

UMMU MAHER CE
[7/1, 11:54 AM] UMMU MAHER (MISS GREEN)🍃: *_💋ƊAN HALAK💋_*

MALLAKAR
*_UMMU MAHER(MISS GREEN)🍃_*

*_AREWA WRITER'S ASSOCIATION📚_*

~*Arewabooks*~
D'AN HALAK:: https://arewabooks.com/book?id=6631fffa0eeb3b80f1ef8159

*~Wattpad~*
D'AN HALAK

https://www.wattpad.com/story/368199708?utm_medium=link&utm_source=android&utm_content=story_info

8

________ Tasleem ce a falon Iya Abu sai sallama take amma ta maishe ta banza, abun ya ƙuntata ran iya har batasan lokacin da ta ce" Haba Tasleem ko baki sanni ba ai kya amsa sallama ta ko? tunda na fito daga tsatson musulunci........"
Tun kafin ta ƙarasa kalaminta tayi saurin miƙewa, da wayarta tankamemiya a hannu ta yiwa Iya wani kallo sannan ta watsar ta ce" ke har kin isa in amsa sallamarki? ke wacece? me kika taka aduniya da har kika isa ni Tasleem Marshal in amsa sallamae baiwa ƙasƙantacciya irinki?, To idan ma mafarki kike ki farka domin ni da kike ganina nafi ƙarfin banza kiyashi ƙaramar alhaki in amsa sallamarki, kiriminal kawai ƴar ƙauye kuma zan tambayi momi zaman uban mi kike agidanmu da kike ganinmu ɗaya dake".

Iya Abu ta sunkuyar da kanta, ta kusa daskarewa awajen saboda tsabar tashin hankali, tunda

take aduniyarta babu wani mahaluƙin daya taɓa yi mata wannan mummunan zagin irinta, tunda take ba'a taɓa faɗa mata maganar da ta kusa tarwatsa ƙwanyarta irin maganar da Tasleem ta faɗa mata ba'a taɓa faɗa mata kamar wannan ba, gaskiyar hausa da suka ce me ƙwaɗayi shi yasan gidan me rowa, banda haka ina Tasleem ina zaginta da batazo gidansu da sunan aiki ba da bata zage taba.

Dai dai nan Hajiya Babba ta fito, cikin shirinta tsaf na tafiya aiki da yake alƙaliya ce, taci uban gashin atach tamkar wata asalin baturiyar ingila, da yake gashin ba me kalar baƙi bane irin me haske ne ja kamar na turawa.

gashi taci uban glass me kalar fari kamar ruwa, ƴar ƙaramar jakarta a hannunta yadda kasan wata budurwa ƴar shekara 18 saboda tsabar son zuciyarta ko takalmin ƙafarta ya isheka gane budurwar zuciya ce da ita.

Ganin autarta Tasleem a wani yanayi yasa ta cire gilashin fuskarta, tana wani firfito da idanuwa tamkar taga abin tsoro domin arayuwarta ta tsani ganin yanayin Tasleem ya canja, ko da kuwa ciwo take to fa sai kaga hankalinta duk yabi ya tashi saboda tana masifar sonta cikin yaranta.

"Babyna me ya faru? Uban waye ya ɓata miki rai"?.

Tasleem ta dallawa Iya Abu harara, sannan ta ya mutsa fuska ta ce" Momi wai uban waye ya bawa wannan matar damar aiki agidan nan"?.

da wani irin sauri Iya Abu ta kama hanya zata arce, domin Allah ya sani tana masifar son aikinta bata son abinda zai taɓa aikinta.

Wani kallo ta yi mata sannan ta dakawa tsohuwar wata gigitacciyar tsawa.

"Ke!!!!!!!!!".

da mugun sauri ta dawo, yadda hanjin cikinta ya kaɗa tuni taji gudawa na neman zubo mata, ta rikice tayi saurin tsugunnawa sannan ta ce" Allah yaja da ranki ayimin afuwa, wallahi sallama nayi bata amsa ba nayi mata magana to fa shi ne ranta ya ɓaci, amma don Allah don annabi domin sonki dana iyayenki ki yafemin kada ki koreni daga aiki".

Wani banzan wulaƙantaccen kallo ta bita dashi, sannan ta ce" wallahi yau ɗinnan zaki bar gidan nan uban wa ya faɗa miki ana ɓatawa autata rai? Yar uban wacece ke da zaki takurawa ƴata? saboda waccan mahaukaciyar kucakar matar ta ɗaukeki aiki shi ne zaki zomin ɓangare ki dameni? To bari uwar ƴan karanbanin ta dawo, zan faɗawa Alhaji komi idan yaso ta zauna babu me aikin, Haba wannan masifa da yawa take an auromin mata tunda jajayen sahuna ba'a

barni ba, tsinanniya masu shiga su fita da asirinsu na buzaye".

Haka dai tayi ta yin maganganunta, har daga bisani ta sanya Iya Abu bawa Tasleem haƙuri.

taƙi haƙura wai har sai ta dafa ƙafafuwanta sannan zata haƙura, iya tana kuka ta dafa ƙafarta tana bata haƙuri sa'ar jikokinta amma take dafa ƙafarta tana bata haƙuri saboda ita talakace su kuma masu kuɗi.

ahaka ta tashi jiki ba nauyi, tana share hawayenta da gefen zaninta, domin cin mutuncin ya kai cin mutunci amma duk da haka cewa take sai ta wulaƙantata sai ta kore ta daga aiki.

_HUMAIRA_

Tsananin fushi da aman wutar da take cin zuciyata Allah kaɗai yasani, saboda labarin da Iya Abu ta bamu yanzu na ci mata mutunci da sukayi, sosai raina ya ɓaci har na gaza ɓoyewa na ce" amma waɗannan mutanen bazasu ga annabi ba, ace don suna da kuɗi su dinga murza mutane son ransu Allah ya wadaran naka ya lalace, Allah ya shiga tsakanin nagari da mugu".

Suka amsa da amin.

Saboda tsabar ɓacin rai Ameera bata gama saurararmu ba ta fice fuuu, daman nasan duk zuciyata ta dameni da ita da Ummi zuciyarsu har mamaki take bani domin ita idan zuciyarta ta motsa bata iya gane waye agabanta waye abayanta, sannan idan Amira ta saka ƙafar wando ɗaya da kai ko magana baka isa tayi maka ba.

Hayaniya naji muka fito da sauri.

"INNA LILLAHI WA INNA ILAIHI RAJI'UN".

Ganin Ameera nayi tsaye a bakin babban falonsu wanda zai sadaka da mutanen gidan, ta riƙe ƙugu tana ta ruwan ashar da bala'i tana masifa idanuwanta arufe bata ganin na gabanta dana bayanta.

Jikina amatuƙar zafafe na ƙarasa kusa da ita ina riƙe ta, amma ina sai da ta sada kanta har cikin babban falon da yake irin me gilas ɗin nan ce,nan da nan ta buɗe da kanta ta shige tana ihu tana zage zage.

Ni dai da Allah zaisa in kama Ameera sai na naɗa mata na jaki, domin naga alamar so take ta janyo mana masifa tunda gashi tana son taɓa masu hannu da shuni, waɗanda ubansu idan

baizo na farko a masu kuɗin nigeria ba zai iya zuwa na biyu.

Hajiya babba tana tsaye inda Iya Abu ta barta, tana rarrashin autarta Tasleem. kamar daga sama suka hango Ameera tamkar mahaukaciya, dukkansu sunyi matuƙar mamakin ganinta gamida tsorata, saboda harga Allah sun ɗauka mahaukaciya ce ashe me hankali ce abu ɗaya ya ɓata mata rai yadda suka wulaƙanta Iya Abu, domin ko kai waye indai Ameera tana kusa ka wulaƙanta wani musamman ma talaka to fa sai inda ƙarfinta ya ƙare.

"wacece Hajiya babba acikinku"?.

ta hau nuna su da yatsanta, ni kuwa sai janta nake ina rufe mata baki, tana yarfar da hannuna saboda dama ta fini jikin girma ni yadda kasan a hure ni haka nake.

Tasleem ce ta matso sosai tana mata kallon mahaukaciya ta ce" hey! who are u? are u mad"?.

wani dallelen mari Ameera ta bata sannan ta ce" hey! criminal, ba dake nake ba alamu sun nuna ba ke bace waccan guzumar ce".

ta nuna Hajiya babba wacce ta tsorata sosai da marin da aka yiwa ƴarta, idanuwanta suka firfito za tayi rashin mutunci ta tunkaro Ameera gadan gadan tana wani irin huci tamkar farar wuta..........

_HANAN_

Sosai ta ƙurawa hoton Haidar ido, har tana mamakin yadda zuciyarta take tsananin bugawa idan tana kallonsa, lallai sai yanzu ta gasgata rashin hankalin Saleema da ta kasa gane irin baiwar da Allah ya yiwa Haidar, namiji acikin maza namijin daya haɗa komi uwa uba kuɗi, gaskiya dole ma ta ƙwacewa Saleema Haidar ko anaso ko ba aso dole ma ta ƙwace mata shi, domin idan ta bari akayi wannan auren mutuwa za tayi, domin Allah ya sani ahalin yanzu ta tsani buɗe ido taga Saleema ita da Saleemar ma zata mutu da kowa ya huta.

ƙarar buɗe ɗakinta taji, da sauri ta mayar da wayarta ta ƙwanta harda jan minshari domin tasan ba kowa bane wanda ya wuce mahaifiyarta domin bataji shigowarta ba kuma bata faɗa mata ta dawo ba, tunda tasan dama ba nisa tayi ba bazata wuce wajen Saleema ba tunda duk gisa ɗaya suke gidan sarauta, amma sai ka ɗauka unguwarsu ma dabance amma duk agida

ɗaya ne, banbancin dai shi ne su sun fita dabanne agidan tun bayan da wani ɓoyayyan al'amari ya faru.

tana jin wucewarta tayi saurin ɗakko wayarta, ta danna lambar Saleema sai da ta kirata sau wajen uku sannan ta ɗaga.

Alamar tasha kuka ta gaji, jin muryarta yasa Hanan yin kalar tausayi tamkar dai tana gabanta ta ce"haba Saleema kar dai kice min haryanzu kukan nan kike? Ni banason ganinki cikin damuwa don Allah, damuwarki tana hanani sukuni ki gane ki daina don Allah".

daga can taja ajiyar zuciya sannan ta ce" ayya! Hanan bazaki gane irin son da nakewa Haidar ba, inason with all my heart sona tsakani sa Allah, wallahi idan har ban auresa ba komai zai iya faruwa dani".

"ki mutu mana".

Cewar Hanan azuciyarta, domin idan har ta mutun sai tafi kowa murnar hakan, ada dai tana tsananin son aminiyartata amma ahalin yanzu kiɗa ya canja ya koma tsana sanadin gadanga ƙusar yaƙi Aliyu Haidar.

da ƙer ta saita kanta sannan ta ce" Hanan kenan, ai ke kika rusa damarki ke da kanki da kikayi bincike kin gano cewa babu kalmar da Haidar ya tsana sama da ace masa ɗan shege, amma saboda kinason ki ƙuntata masa kika faɗa masa kalmar da tafi masa zafi fiye da kowacce".

Saleema ta rushe da kuka, ta ce" Hanan idan ba damuwa gobe da safe kizo, inaso inje har gida in bawa Haidar haƙuri saboda ni kaɗai nasan halinda nake ciki gashi me martaba ya matsamin in fito da miji".

Hanan taɗan taɓe baki, sannan ta ce" haba Saleema wai me yasa kikeson aikata abinda zai xama laifi ne? ina ke ina zuwa gidansu Haidar? Idan Memartaba yaji me zakice? Kinsan fa bayason fita ba tare da an sanar dashi ba".

Shiru tayi tana tunani, sannan ta ce" to naji Hanan, yanzu me kike so ayi? Ni kaina ya kulle wallahi, ga son Haidar na neman kaini lahira".

"ki bari gobe idan nazo akwai maganar da zamuyi dake me muhimmanci, kuma cikin sauƙi zai yarda ya yafe miki laifin da kika yi masa".

bayan sunyi sallama, mahaifiyar Saleema uwae gidan sarki Abdussalam ta shigo.

Sosai ta ƙare mata kallo sannan ta ce" Saleema, wai me yake damunki ne? ƙwana biyun nan bakya zama kan dining sam ko a falo bana ganinki, anya kuwa lafiya"?.

Kuka ta fashe dashi duk da dauriyar da take arowa, ta dinga yinsa babu kama ƙafar yaro Fulani ta barta tayi kukanta me isarta sannan ta ce" Fulani, wallahi Haidar ne ya kasa gane abinda nake nufi bisa binciken da Memartaba yayi akansa ya gano ba shida uba, ni kuma wallahi inasonsa tsakani da Allah"........

Tun kafin ta ƙarasa ta galla mata wani irin kallon banza sannan ta ce" amma Saleema kin bani mamaki, yanzu ke saboda rashin hankali ɗan shegen kike son aura?.....................

*_WELCOME TO UMMU MAHER BUSINESS CENTER_*
_____~~¥¥¥¥¥¥¥~~

*TIME TABLE NA KOYON SANA'A*

CLASS 1👇🏻
______________

*KOYON MAYAFI NA BEAD WORK BEAD WORK*
*MAYAFI NA STONE WORK*
*HULUNA*
*RIGUNA*
*FANTIS*
*WANDO JEANS*
👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻
~Naira~ 800

CLASS 2👇🏻
________________
*INVITION CARD*
*3d logo*
*3d mockup*
*3d render*
*Cover book*
👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻
~Naira~  800

CLASS 3
__________
*Turaren wuta*

*Humrah*
*Gyaran jiki*
👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻
~Naira~ 1k

a tuntuɓi ummu maher ta lambarta👇🏻
07068606171

*DOMIN SHIGA WHATSAPP GRP ƊINMU👇🏻*
https://chat.whatsapp.com/CMlWt3cUVvkDAXPthThNQx

*UMMU MAHER*
[7/1, 11:54 AM] UMMU MAHER (MISS GREEN)🍃: *_💋ƊAN HALAK💋_*

MALLAKAR
*_UMMU MAHER(MISS GREEN)🍃_*

*_AREWA WRITER'S ASSOCIATION📚_*

~*Arewabooks*~
D'AN HALAK:: https://arewabooks.com/book?id=6631fffa0eeb3b80f1ef8159

~*Wattpad*~
D'AN HALAK
https://www.wattpad.com/story/368199708?utm_medium=link&utm_source=android&utm_content=story_info

9

________da sauri Saleema ta kalli Fulani mahaifiyarta, sannan ta sunkuyar da kanta ƙasa tabbas taji zafin maganar da ta faɗa akan Haidar, domin tabbas da wanine da sai inda ƙarfinta ya ƙare, domin babu abinda ta tsana nab gidan duniya wanda ya wuce cin mutuncin burin zuciyarta kuma sahibinta Haidar.

"ba dake nake magana bane? saboda an taɓo miki inda yake miki ƙaiƙayi dolenki kiyi shiru ai, to ki buɗe kunnuwanki ki jini indai har ina raye baki isa ki auri wannan shegen yaron ba, ni ina ruwana da kuɗinsu? kuɗin da ba'a ginashi ta hanyar halal ba? ai daman ance can yawon

banzanta ta sameshi, saboda haka mu zuri'armu ba'a haɗa haram da halal yaje can ya samu ƴar uwarsu shegiya amma ba ƴata ba, domin ke ɗinnan matar ƴan gidan mutunci ce waɗanda sukasan mutuncin mutane da kuma girma, amma ba ƴaƴan terere ƴaƴan kwalta ba".

Fashewa da kuka tayi, sannan ta ƙarasa gaban Fulani ta durƙusa gwiwarta duk a ƙasa ta dafa ƙafarta ta ce"Mama Fulani don Allah don annabi kiyimin rai, ki ceceni don Allah ki taimaka ki barni da Haidar, wallahi nayi muku alƙawarin kare mutuncin wannan masarautar, don Allah ki taimakawa rayuwata rasa Haidar yana nufin rasa rayuwata ne baki ɗaya, don Allah ki taimaka ki barni dashi".

ta haɗa hannayenta waje ɗaya alamar ban haƙuri, amma ko kallo bata isheta ba daga bisani ma ta hankaɗata gefe tayi wucewarta.

sosai take kuka har batasan iya adadin hawayen da ta zubar ba, gani take tamkar ba Fulani ce ta tsugunna ta haifeta ba, domin kuwa ayadda takeson Haidar ya kamata su gane halin da take ciki.

da sauri ta ɗakko wayarta tamkar mahaukaciya tana neman hotunan Haidar, ada can baya ma hotonsa ne akan wayarta amma ayanzu ta ciresa ne saboda abubuwan da suka dinga faruwa marasa daɗi.

ya subhanalillah, baki ɗaya taji zuciyarta na tsinkewa gamida bugawa acikin lokacin da bai fi sakan guda ba, jikinta yahau rawa saboda ganin hoton Haidar wanda yake ƙara mata wutar mikin sonsa acikin ɓargon zuciyarta da ruhinta.
sai da tasha kukanta ta ƙoshi, domin babu wani mahaluƙin da zata faɗawa abinda yake damunta sama ga sarki buwayi gagara misali, tunda uwar dama ta haifeta ta nuna bata santa ballantana kuma wani?. tunda duk son da wani ko wata xai nuna mata bai ka ga na mahaifiyarta ba.

ta ɗauro alwala tayi sallah raka'a biyu ta ɗaga hannayenta sama tana addu'ar neman zaɓin ubangiji, domin ayanzu ta gane ba zaɓin mutum ne alheri ba, zaɓin Allah shi ne alherin ba zaɓin mutum ba.

*******

ganin haka yasa tun kafin ma Hajiya babbar ta ƙaraso ita da kanta ta rage mata aiki ta ƙaraso, tana wani cika tana batsewa ta nuna Ameera da yatsanta ta ce.

"ke ƴar uban waye da zaki shigomin gida kizo har falona kice zaki cimin mutunci"?.

"Ameera tayi wani gyatsine gamida gyara tsayuwarta, sannan ta ce" ni ba ƴar kowa bace amma ina da Allah domin shiya halicceni kuma yake sona, kinga kuwa ina sa babbar katangar da babu

wanda ya isa ya wulaƙantani duk kuɗinsa kuwa".

tana tsananin huci ta ɗaga hannu da niyyar kaiwa Ameera mari, da muguwar azama Ameera ta riƙe hannunta abinka da jikin yarinta sai ga hannun Hajiya babba agefe, Ameera ta nuna ta da yatsanta ta ce" talaka suna ya tara kada ki ɗauka ina ɗaya daga cikin waɗanda kika saba wulaƙantawa rayuwa, na faɗa miki baki isa ki wulaƙantani ba tunda dai ina da Allah, sannan inason faɗa miki gaskiya ruwanki ki ɗauka ruwanki kiƙi ɗauka domin ba matsala ta bace, matsalarki ce kuma nan gaba ke zata dama ba Ameera ba.

"kinga wannan ƴar ta ki"?.

ta nuna Tasleem wacce take tsaye, tanaji kamar ta shaƙo Ameera ta zauna kanta amma ko da me kurna tafi magarya zaƙi domin whtsiyar raƙumi tayi nesa da ƙasa Ameera ta fita komi, jiki tsayi yanayin ƙarfi da kuma manyan gaɓɓai na ƙira, saboda haka yasa ta ɗaga mata ƙafa banda haka da tuni ta dilmiya kanta ƙasa domin ba zata ɗauki wannan rashin mutuncin data zo dashi ba.

"ki tabbatar kin koya mata tarbiyya kafin ta shiga ɗakin miji, domin wallahi ko nice na miji bazan taɓa auren lalataciyyar yarinya irin taki ba, domin kowanne namiji da kika gansa yana son yarinya me hankali, ba mara mutunci ba wacce batasan darajar kowa ba".

tana faɗar hakan ta janyo hannuna, tamkar ƴa da uwa ni kuma na bita muka tafi nayi saurin juyowa don inga halin dasu Hajiya babba suke, suna tsaye sai huci suke suna wani irin kallo tamkar zasu haɗiyi maita ita kuma Iya Abu tana raɓe a gefe tana zubar da ƙwallah.

Kai tsaye gida muka nufa, babu wanda ya cewa ɗan uwansa ƙala saboda kowa da tunanin da yake acikin ma'ajiyar sirrinsa wato zuciya.

Acan gidanmu kuma ƙofar gidanmu ne cike da mutane, wanda ya sanyamu saurin ƙarasawa domin ganin abinda ya faru.?????

Baba Kande ce da kishiyar Ummanmu, sai kuma Ummi wacce naga tana wani irin kallo tamkar zata ari bakin kare ga rigarta tun daga sama har ƙasa a yage kana hango zararan cinyoyinta farare ƙal, dama duk sun fini haske ni ce ma ba wata fara ba.

da sauri muka ƙarasa, Ummi tana ganinmu ta ƙaraso da gudu ta rungumeni, sannan ta fashe da kuka tana manne dani tamkar za'a ƙwaceni daga jikinta.

tausayinta ya kamani, duk da bansan me ya faru ba? amma hankalina yayi matuƙar tashi sosai domin ina matuƙar son Ummi domin yarinyar tafi Ameera sauƙin kai, sai dai fa itama ba tada haƙuri ko kaɗan kamar jira take ka taɓata yanzu kaji maganganu masu dukan zuciya.

ɗan dukan bayanta na hau yi ina bata haƙuri bakida lallashi nake bata saboda naga yadda take haɗiyar zuciya, ta shiga bani labarin abinda ya faru tana kuka.

_BABA KANDE_

Ummi ce ta shigo gidan da jakar islamiyya akafaɗarta, tana shigowa ta ajje jakarta sai taga bama nan ta fito tsakar gida domin haɗa kan ƙannai na su tafi nemanmu, dama kuma duk inda mukaje nida Ameera in har mu biyu muka tafi to duk inda muke sai sun nemomu har sun saba da hakan ma.

wani yaro ne ya shigo ya ce" wai ana sallama da wadda ta shigo yanzu".

Baba kande tana ƙofar ɗakinta tayi saurin ce wa" kai yaro zo, waye ɗin yake sallama da wannan ƙwailar wacce batafi shekara goma sha shida ba?".

Yaron ya ce" wanine yana ƙofar gida cikin wata babbar mota, me kuɗi ne sosai nima ɗari biyar ya bani yanzu wai in kira masa yarinyar da ta shigo gidan nan yanzu".

wata uwar ashar ta mulmulo sannan ta ce" to uban me zai ci da wannan fugigiyar yarinyar me irin jikin uwarta? kace masa ba nan gidan take ba........"

Ummi ta ce" je kace ina zuwa, ai ba zaman wani nake ba zaman uwata nake da ƴan uwana sabofa haka babu wanda ya isa ya hanani fita ai inda ba ƙasa nan ake gaddamar kokawa".

tayi saurin ɗaukar figigin mayafinta ta fira sai huci take, domin dama takeso ta dama da ita ta samu lokacin zane Baba Kande kan shisshigin da take mata, batasan daman haushinta take ba dangane da ƙuntatawa mahaifiyarta da akeyi agidan.

tana fitowa ta hangosa cikin motarsa, kyakkyawane sosai amma ba fari bane amma yana da sikin me mugun ɗaukar hankali da kuma sheƙi, kana ganinsa ba sai an faɗa maka ba kasan dukiya ta samu gindin zama awajen, sannan ba wai yaro bane a ƙalla zai yi 45 a ƙiyasi.

haka kawai gaban Ummi ya yanke ya faɗi, sai take hango wata kama a idaniyarsa amma sam ta manta wacce kamar ce, sannan kama da wanda take tunanin ta sansa na kusa da ita ne idan ta ɗauro ma tana ganinsa kullum amma Allah baisa ta tuna waye ɗin ba.

Ganin ta kasa ƙarasowa ya ce" ƴammata ƙaraso mana".

daga can Ummi ta tsaya, kunyarsa ta cika mata ciki amma saboda tana ganin cika mata idon da yayi ta kasa ƙarasawa ta fara tafiya ahankali har ta ƙarasa bakin motar duk jikinta asanyaye.

Yayi murmushi sannan ya ce" in fito ko? nasan abinda yasa kike tsorona ganina acikin mota to bari in ƙaraso".

ya fito kansa tsaye idonsa akan Ummi, yarinyar da ta sace zuciyarsa cikin mintunan sa basufi ɗaya ko biyu ba, daga zuwa super market na bakin titi siyayua yaga Ummi zata tsallaka titi, shikkenan yaji ta ƙwanta masa ya biyo ta, duk da Ummi sa'ar ƴarsa ce ta fari amma babu yadda zaiyi tunda haka Allah ya ɗora masa, kuma bawa baya kaucewa ƙaddararsa banda haka da tun kallon farko ya haƙura da ita tunda ƴar cikinsa ce, amma ya kasa haƙura har sai daya zo inda take yaga gudansu, kuma baiso ya fara magana da ita ba har sai ya nemi izinin mahaifinta amma yana ganin bazai iya haƙura ba tare da sake sanyata a idonsa ba har sai wani bayan lokaci wanda shi ayanzu so yayi masa mugun kamu.

kallon yarinyar yake tamkar zai kamota ta zama tasa alokacin, amma babu yadda zai yi domin shi gani yake ba lallai ne ma yarinyar ta auresa ba.......

*_WELCOME TO UMMU MAHER BUSINESS CENTER_*
______¥¥¥¥¥¥¥

*TIME TABLE NA KOYON SANA'A*

CLASS 1👇🏻
______________

*KOYON MAYAFI NA BEAD WORK BEAD WORK*
*MAYAFI NA STONE WORK*
*HULUNA*
*RIGUNA*
*FANTIS*
*WANDO JEANS*
👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻
~Naira~ 800

CLASS 2👇🏻
________________
*INVITION CARD*
*3d logo*
*3d mockup*
*3d render*
*Cover book*
👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻
~Naira~  800

CLASS 3
__________
*Turaren wuta*
*Humrah*
*Gyaran jiki*
👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻
~Naira~ 1k

a tuntuɓi ummu maher ta lambarta👇🏻
07068606171

*DOMIN SHIGA WHATSAPP GRP ƊINMU👇🏻*
https://chat.whatsapp.com/CMIWt3cUVvkDAXPthThNQx
[7/1, 11:54 AM] UMMU MAHER (MISS GREEN)🍃: *_💋ƊAN HALAK💋_*

MALLAKAR
*_UMMU MAHER(MISS GREEN)🍃_*

*_AREWA WRITER'S ASSOCIATION📚_*

~*Arewabooks*~
D'AN HALAK:: https://arewabooks.com/book?id=6631fffa0eeb3b80f1ef8159

~*Wattpad*~
D'AN HALAK
https://www.wattpad.com/story/368199708?utm_medium=link&utm_source=android&utm_content=story_info

_____"nasan baki sanni ba ƴammata, amma kiyi haƙuri ki yafemin idan har na shigar miki lokacinki babu yadda zanyi ne, shiyasa har hakan ta faru dafatan abin bai sosa ranki ba"?.

Ɗaga kai tayi, lokaci ɗaya kunyar bawan Allahn da ganin girmansa suka shige ta, sai ta jiyo muryarsa yana ce wa" ƴammata nazo wajenki ne akan wani lamari duk da bana tunanin ƙwaƙwalwarki zata iya ɗaukar darasina, amma da sannu yaro ke rarrafe har ya fara tafiya kuma da sannu ƙaramar bishiya ke girma har ta kai ga cika waje, ban sanki ba ban taɓa ganinki ba amma Allah ya ɗora jarabar sonki cikin lokaci ƙanƙani".

suna cikin maganar ne Baba Kande ta leƙo tana sababi, har tana tsinewa Ummi wai ta zama karuwa tana janyo maza.daga nan ta fara dukanta har tana yaga mata riga. mutumin yana bata haƙuri amma taƙi haƙura ta dinga zaginsa har sai da ta koresa ya tafi domin tana son haɗa masa wani sharrin, shi kuwa ya wuce da sauri ba don yaso ba, domin har ya tafi bai daina kallom Ummi ba kana ganin fuskarsa kasan tausayinta yake ji.

*Cigaban labari*

na ƙara rungume Ummi sosai ajikina, yadda take kukan bilhaƙƙi haka zuciyata ma take bugawa da gaske, domin da gaske bana son duk wani abinda zai taɓa ƙannai na, yadda nake sonsu bana son kai na haka.

Baba kande tana ta maganganunta na ɓacin rai, babu wanda ya kulata domin har Ameera ta shiga gida abinta domin daman da wata aƙasa, biyo bayan abinda ya fari tsakaninta da Hajiya Ƙarama, wanda agefen zuciyata nima ya maƙale yaƙi fita domin nasan ba zasu yarda ba, kuma aikin Iya Abu nasan ya lalace haka zalika aikin Ummanmu ma ya lalace asara goma da ashirin.

Allah ya taimakemu Babanmu baya nan, saboda haka yanzu shawara muka cigaba da yi ta yadda za'ayi mu biya kuɗin asibiti.

Ihun Fahad ne ya katsemu daga shawarar da mukeyi, duka atsorace muka kallesa ya ƙaraso da gudunsa kan cinyata ya miƙomin ƴan bandir ɗim kuɗi.

Na waro ido waje domin sanin wanda ya basa, da ido nayi masa tambayar wa ya basa?.

"Antinmu wani ne ya bani, ya ce wai in bawa Anti wai ince mata wanda yazo ɗazu ne".

Da sauri Ummi ta kallesa har tana haɗe harshe wajen ce wa.

"me....me.... wanda..yazo ɗazu dai"?.

Yaron ya ɗaga kai.

Godiyq muka shiga yiwa Allah, daya sa aka samu zunzurutun kuɗi haka wanda aƙalla za su kai dubu ashirin ko su ɗanfi ma.

Sai alokacin ne Amira tayi magana, cike da fara'a ta ce" oh Allah mungode maka Ummi ke me sa'a ce wallahi yanzu kinga mun samu kuɗin da zamu kai asibiti a sallamo mana Ummanmu".

Tashi mukayi mu dukanmu muka shirya ƙannenmu muka ɗunguma zuwa asibiti, muka samu adaidaita sahu har asibitin murna fal zuciyata domin da bamu samu wannan kuɗin ba da yaya za'ayi kenan?.

muna zuwa kai tsaye na wuce wajen da aka tanada domin biyan kuɗi, na cake dubu ashirin na bayar dubu biyar kuma na ajje a gefen zanina dama kuɗin da muka ƙirgasu dubu ashirin ne da biyar.
Dama kuma kuɗin asibitin dubu ashirin ne.

Sosai su Ummi suke murna, saboda ganin mahaifiyarmu cikin ƙoshin lafiya ga ƴan biyunta duk maza farare ƙal ƙal kamar Ameera domin ita duk ta fimu fari.

Umma ta tsuramin ido tana kallona, hankalina ya tashi sosai na ƙarasa kusa da ita domin jin laifin da nayi mata, ko domin na daɗe ne dana fita? ko kuma wani abun ne dai?.

na durƙusa gabanta, gamida riƙo ɗan yatsanta babba na ce" Ummanmu lafiya kuwa? ko dai wani laifin nayi ne ban sani ba? idan ma laifin nayi Umma ayafemun domin darajar ƴan biyu masu farar fuska".

Dariya mukayi mu dukanmu, sai Umma ta ce" to na haƙura Humaira  h amma a ina kika samo kuɗin da kika biyamin kuɗin asibiti"?.

Caraf Ameerah ta ce" Umma wani ne ya bada kuɗin, wai yaga Ummi yana sonta to akan hakan nema akayi faɗa da Baba kande har ta yagawa Ummi riga, bayan mun dawo gida shi ne ya aiko da waɗannan kuɗaɗen, dama kuma muna ta neman hanyar da zamu samu kuɗin mun rasa to sai yanzu Allah yasa aka samu, don har gidan DEEN MARSHAL munje amma bamu samu kuɗin ba, harma mukayi faɗa da Hajiya Babba".

Da sauri Umma ta kalli Ameerah ta ce" me yasa kuka je gidan? kunsan wacece Hajiya babba kuwa? kunsan ƙarfin ikonta agidan? to ko uwar me gidan ce tace akora za'a kore ta, sannan ni ayanzu haka ma nasan ba barinmu za tayi ba, dalili da meyasa bakyason zaman lafiya Ameerah? ina yawan faɗa miki rayuwa bata yiyuwa sai da haƙuri, kayi haƙurinma ya ka ƙare

ballantana akasin haka? sannan ga wannan abin da ya faru na Ummi".

ta kalli Ummi wacce kanta yake asunkuye dom kunya ta ce" Ummi shin kinsan mutumin ne? kuma tun yaushe kuka haɗu"?.

"Umma wallahi ni bansanshi ba, kuma sau ɗaya na taɓa ganinsa yau kenan amma ban taɓa ganinsa ba amma dai yana yimin kama da wata fuska wacce na santa amma na rasa fuskar waye"?.

Umma ta ɗaga kai, sannan ta ce" to duk sanda ya ganki ya tsayar dake kice yazo ya samu mahaifinki kinji"?.

ta ɗaga kai alamar taji.

Ameerah ta ce", uhum Umma wallahi kina da haƙuri yanzu duk abinda Babanmu yake miki bakya gani? har kike son wani yazo ya gansa daganan ya lalata lamari duk da Ummi yarinya ce amma ai ana aurar da yara ashekara 15, tunda babu wanda zai ce hakan saɓon Allah ne, ko don ƴan baƙin ciki ai dole a yardar masa ya turo kawai ayi, muma Allah ya zaɓa mana abinda yafi alkhairi".

"Ameerah koma dai meye mahaifinku ne, sai haƙuri kuma ba'a hannuna neman aurenku yake ba a hannunsa yake saboda haka ko inaso ko bana dole ne a nemi auranku a wajensa, uba ubane koda kuwa a turu aka cirosa".

Ameerah dai don haushi bata ce komi ba, ni ce ma na ce" hakane Umma Allah ubangiji ya ganar da Baba".

Duka suka amsa da amin.

Bayan an sallamo Umma, mun fito da taxi muka hango ƙofar gidanmu cike da mutane damƙam...............

$$$$$$

Haidar ya ɗaga wayar tamkar bazaiyi magana ba sai kuma ya amsa.

"ina jinki"?.

Hanan taɗan daidaita muryarta sannan ta ce" ka kuwa gane ni?".

Ya basar ya cigaba da aikinsa saboda sam bayason yin waya da kowa ayanzu saboda shi kaɗai yasan halinda yake ciki, wanda kuɗi ko mulki ba zai iya bayarwa ba domin ayanzu haka aƙwance yake yana fama da ciwon cikin dake azalzalarsa wanda yake motsa masa duk bayan wani lokaci, wanda likitoci suka tabbatar masa rashin aure ne ya janyo masa.

Hanan taɗan dakata da magana, saboda taji kamar yana cikin wani yanayi ne saboda haka ta ce" kayi haƙuri bansan kana cikin wani yanayi ba, ko zan iya taimaka maka da wani abun?".

bai katse kiran ba, kuma bai ce mata ƙala ba saboda haka har Hanan ta gama maganarta bai san abinda take cewa ba.

Da ƙer ya lalubo lambar Hammud, bugu ɗaya ya ɗaga yana jin yanayin aminin nasa hankalinsa ya tashi sosai da sauri ya sanya jallabiyyarsa ya fito daga ƙerarran gidansa wanda ya gamasa ƙwanannan.

***

Yana zaune gaban likita, yayi shiru yana jin dukkanin bayanansa har ya kai ƙarshe Yana kallon yadda hankalin Hammud ya tashi sosai.

"likita yanzu meye mafita?".

Cewar Hammud wanda baki ɗaya hankalinsa yake atashe.

likitan ya gyara farin gilashinsa sannan ya ce" solution dai ɗaya ne yayi aure domin wannan matsalar tasa babu wani magani ko tablet da zamu basa yayi masa magani kawai dai gwara yayi haƙuri ya daure yayi auren shi ne magani, sannan kada ya daɗe ahaka ba tare da yayi auren ba komi zai iya faruwa".

Hammud ya kalleni, na rintse idona inajin wani irin suya araina.

Hammud ne ya kamani muka fito, dai dai wani ɗan desk naso faɗuwa yayi saurin ruƙoni yana ce wa" sannu Haidar kayi ahankali".

Hammud wannan wata irin ƙaddara ce? anya kuwa zan iya jure wannan ƙaddarar? ace ina da lafiya ta da komi Allah ya horemin komi na rayuwa amma Allah bai sanya nayi aure ba, saboda

wani dalili wanda aka shafamin kashin kaji, idan ma laifina dana zo duniya ne ai ba ni na aikata laifin ba, sannan Allah ne yaso inzo ta wannan hanyar"!!.

na faɗi maganar tawa cikin ƙaraji.

Hammud ya ce" kash! Aminina bai kamata adingajin wannan kalaman masu muni daga bakinka ba, kamata yayi ace ka mayarda komi ba komi ba ka cigaba da addu'ah komi yayi farko yana da ƙarshe kuma in sha Allah komi zai zama kamar ba ayiba, kuma auren ma ƙwanannan zaka yisa in sha Allah".

Haka dai ya dinga rarrashina har muka dawo gida, allurar da suka yimin ta fara ratsa ƙwanyata, barci me nauyi yayi awon gaba dani.

_HANAN_

wani malolon baƙin cikine ya kusa kasheta atsaye, wannan wani irin ɗan rainin hankalin namiji ne? ace da ranta da lafiyarta namiji yana wahalar da ita? gaskiya doleta ta samowa kanta mafita, tun kafin gari ya waye mata.

Yayarta Asabe ta kira, kirab farko ta ɗaga tayi mata bayanin komi.

Yaya Asabe ta ce" aikin banza aikin hofi au dan ɗan wannan ƙaramin alhakin shi ne kika tada hankalinki?"...........................

*_WELCOME TO UMMU MAHER BUSINESS CENTER_*
_____¥¥¥¥¥¥¥

*TIME TABLE NA KOYON SANA'A*

CLASS 1👇🏻
_____________

*KOYON MAYAFI NA BEAD WORK BEAD WORK*
*MAYAFI NA STONE WORK*
*HULUNA*
*RIGUNA*
*FANTIS*

*WANDO JEANS*
👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻
~Naira~ 800

CLASS 2👇🏻

---

*INVITION CARD*
*3d logo*
*3d mockup*
*3d render*
*Cover book*
👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻
~Naira~  800

CLASS 3

---

*Turaren wuta*
*Humrah*
*Gyaran jiki*
👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻
~Naira~ 1k

a tuntuɓi ummu maher ta lambarta👇🏻
07068606171

*DOMIN SHIGA WHATSAPP GRP ƊINMU👇🏻*
https://chat.whatsapp.com/CMIWt3cUVvkDAXPthThNQx

UMMU MAHER
[7/1, 11:54 AM] UMMU MAHER (MISS GREEN)🍃: *_💋ƊAN HALAK💋_*

MALLAKAR
*_UMMU MAHER(MISS GREEN)🍃_*

*_AREWA WRITER'S ASSOCIATION📚_*

~*Arewabooks*~
D'AN HALAK:: https://arewabooks.com/book?id=6631fffa0eeb3b80f1ef8159

~*Wattpad*~
D'AN HALAK

https://www.wattpad.com/story/368199708?utm_medium=link&utm_source=android&utm_content=story_info

11

__________Hanan tayi saurin ce wa"yaya Asabe don bakisansa bane, wallahi da kimsan waye shi da baki ce haka ba, sam ba shida fuska ma ballantana har kayi sha'awar kawo masa wargi inda irin jigari jigarin samarin nanne da tuni wani zancan ake ba wannan ba".

"ke dallah! wuce ki bani waje wacce batasan abinda takeyi ba, har wani banzan namiji ne zai ɗaga miki hankali saboda wata izzarsa? anya kuwa ke ƴar danginmu ce kuwa? domin kaf danginmu babu mara zuciya irinki? ai ka samu wanda yake sonka kake sonsa ba wai wanda baya sonka ba, ko asiri akayi masa wataran zai iya karyewa tunda ba son tsakani da Allah bane".

"to yanxu yaya Asabe ya kikeson inyi? so kike in haƙura dashi ko me? kinsan dai bikin magaji ai baya hana na magajiya".

"eh na sani, yanzu dai yaya sunansa?".

"Aliyu Haidar, shi ne me manyan filazozin nan na cikin gari HAIDAR SHOPRITE".

"La'ha'ila'ha'ilallah
Au yanzu ke Hanan kina son wannan babban kamun shi ne baki faɗamin tunda wuri ba? amma anyi sokuwa wallahi, mara sanin inda yake mata zafi ai mu tuni mun warke kaf danginmu matuƙar kika auri wannan multi biloniya ɗin".

"uhum ai yaya asabe shiyasa nakeson ayimin abinda zai soni ya manta da wata banza Saleema, ya aureni agabanta asha shagali shegiya dama zata mutu kowa ya huta".

"au dama wannan busasshiyar yake so? wacce babu abinda namiji zai taɓa ajikinta yaji daɗi? ahaf ai wannan ma ba zai yi wuyar nemowa ba, kawai dai yanzu abinda nakeso dake ki buɗe bakin aljihu kawai ayita zanbaɗo miki abubuwa na jan hankali da sauransu, ta yadda har danginsa sai ya tsana sai ya fititaki sama da kowa nan gidan duniya, kina dai ganina da Dr yadda na zame masa ƙarfen ƙafa domin hatta danginsa sai gani sai hange hadarin kaji".

Hanan tayu buɗa ta ce" haka nakeso Anti na, nima haka nakeson zamewa Haidar shida pan uwansa sai gani sai hange, yanzu dai ta ina zamu fara ne"?.

"aƙwai wani boka a garin gujungu, ƙwanannan aka ƙwatanta minshi amma bazai dawo ba sai ƙarshen watan nan da muke ciki yayi tafiya ne".

nan dai suka cigaba da miyagun shawarwarinsu har suka tsaya kan matsaya guda ɗaya akan cewar bokan yana dawowa sumq zasu fasa kai suje wajensa.

Allah ka tsare mana imaninmu Allah kasa muna cikin bayi ƴantattu.
Anan nakeson kawo wata ƴar nasiha ta, mata mukasance masu imani mu kasance masu nisantar bokaye ƴan tsibbu yawaitar zuwanmu wajen bokaye yawaitar zuwanmu wajen bokaye yawaitar yawanmu cikin wuta ne, idan kinayi ki daina ƴar uwa domin babu abinda zasu ƙareki dashi sai nadama aikin dana sani, saboda haka ki tsaftace zuciyarki ki kasance me nisantar aikata babban saɓo musamman haɗa wani da Allah wannan shi ne babban saɓo.

$$$$$$$
dukanmu amatuƙar tsorace muka ƙarasa, jikinmu sai rawa yake musamman ma ni da nake riƙe da jariran dukansu domin hana kowa taɓasu nayi sai ni kaɗai.

Umma tayi saurin kallona aɗan tsorace ta ce" ba dai ahalin Deen Marshal ne aƙofar gidanmu ba? domin ga motar gidansu can aƙofar gida".

Atsorace na ce" inna lillahi ai kuwa su ɗinne domin ga Hajiya ƙarama can tana tada jijiyar wuya har tana dukan ƙofar gidanmu".

Wayyo Allah na, shikken Humaira ta janyowa ahalinmu abin magana, yanzu ya zanyi da rayuwata"?.

Humaira dake gefe tana wani yatsina fuska cikin fushi ta ce" haba Umma? wallahi ke da Anti kuna da tsoro wallahi, abinda ya kai na tsoro da wanda bai kai ba duk sanyasa kuke a mizanin tsoro, ni Allah kaɗai nake tsoro bana tsoron kowani ƙato wallahi sai ke sai yayata ku kaɗai zanji tsoro amma babu ɗan ƙatuwar dake ciyar dani saboda haka babu wanda ya isa inji tsoronsa idan ba sarki buwayi gagara misali ba, naga nan mukaje neman taimako gidansu ko? waya taimakemu acikinsu? ai naga zagi ne da cin mutunci ya biyo saboda haka duk tsiyar da suke ji da ita nima inaji da ita".

Umma don haushi bata ce komi ba, kawai dai binta tayi da wata harara ta watsar agefe.

"yauwa gasucan ƴaƴan matsiyatan jikan matsiyata waɗanda duk ahalinsu babu mutanen kirki sai na"................

Caraf Humaira da Ummi suka kama harda haɗa bakinsu.

"mu kaf danginmu babu matsiyata, bansani ba ku kai dai baza'a rasa ba tunda gashi kuma sai kurin kuɗi da cika baki amma babu wanda kuke taimako ballantana asaran ku masu mutuncine da sanin ya kamata, kunga kuwa babu wanda ya kaiku tsiya".

Umma tayi saurin buɗe bakinta da niyyar basu haƙuri, sai ga jiniyar motar ƴan sanda ai kuwa tuni maƙota da ƴan sa'idu sukayo waje baki ɗaya suna kallon abinda yake faruwa, masu Allah ya ƙara na yi masu takaicin cin mutuncin da za'ayiwa su Humaira na yi.

Kai tsaye Hajiya Babba ta basu umarnin kamasu nan da nan kuwa suka cika aikinsu, hatta ni sai da na shiga motarsu Umma ce kawai Hajiya babba bata bada umarnin kamata ba, sai kuka muke muna kiran Umma ni da Ummi Amma Humaira ko ajikinta kallon hadarin kaji ma kawai take bin Hajiya dashi.

Dai dai lokacin Anti Salamatu ƙanwar Ummanmu ta ƙaraso jikinta duk amatuƙar sanyaye.

ganinmu cikin motar ƴan sanda yasa duk jikinta yayi sanyi ta fara kuka tana tambayarmu abinda ya faru? Umma ta fashe da matsanancin kuka amma babu bakin magana.

Kai tsaye folis sitation aka wuce damu, Umma kuwa sai bin motar take tana kuka ina ciki ina hangota tausayinta fal zuciyata, domin yau nasan ko barci bazata iya ba ga kuma haihuwar da tayi tana buƙatar hutu sosai.

Da ƙer mama Salamatu tasanya ta agaba da nasiha suka shiga cikin gidanmu, suna shigowa Baba Kande ta kyalkyale da wata irin muguwar dariya har da hantsilawa, ta yiwa Umma wani mugun kallo ganin ƴan biyunta farare tas tas, ai kuwa abin ya tsaya mata sosai domin ita haryanzu ko ƙwai bata ajje ba.

Mama Salamu tayi wucewarta tana mata wani irin mugun kallo na tsanar halinta, domin suna masifar jin haushin abinda takewa yayarta, na zuga mijinta yazo yayi ta sirfa mata rashin mutunci yana zagin iyayenta ta uwa ta uba.

Umman ma wucewarta tayi domin ita kaɗai tasan yadda zuciyarta take mata ga baƙin cikin an tafi da yaranta har uku ga baƙin cikin abinda mijinta yayi mata, ƙwananta ɗaya a asibiti amma bai iya zuwa asibitin ko ɗan aike bai tura ba.

Ummq tana shigowa ɗaki ta fashe da matsanancin kuka, ta ce" Salamatu ina ce dai kina ganin abinda kande take min ko? yanzu haka da yana nan wallahi da tuni ta haɗamin wani baƙim sharrin, shi kuma ya biye mata yazo yayi ta zagina yana cimin mutunci".

Dafa kafaɗarta tayi, sannan ta ce" kiyi haƙuri yaya, wallahi nasan komi kumw nasan abinda yake faruwa sam zuciyoyinmu basa mana daɗi akan abinda yake faruwa, amma ki tuna furucin

mahaifinmu kafin yabar duniya, idan kika kashe aurenki da Adam ba shi babu ke kuma Allah ya la'ance ki".......................

Da sauri Umma ta rufe mata baki tana kuka ta ce, na sani Salamatu shiyasa nake haƙuri da dukkanin halin da zan shiga agidan nan, wallahi yaran nan ne suke bani tausayi saboda mugun bakin da yake binsu dashi akullum, shegu matsiyata Allah ya tsine musu ire iren waɗannan zagin aibatawar yake musu, zuciyata tana tsananin bugamin aduk sanda na jiyosa, idanuwana suna raɗaɗi da muradin son zubarda hawaye amma ahaka nake haƙura.

Umman ma wucewarta tayi domin ita kaɗai tasan yadda zuciyarta take mata ga baƙin cikin an tafi da yaranta har uku ga baƙin cikin abinda mijinta yayi mata, ƙwananta ɗaya a asibiti amma bai iya zuwa asibitin ko ɗan aike bai tura ba.

Ummq tana shigowa ɗaki ta fashe da matsanancin kuka, ta ce" Salamatu ina ce dai kina ganin abinda kande take min ko? yanzu haka da yana nan wallahi da tuni ta haɗamin wani baƙim sharrin, shi kuma ya biye mata yazo yayi ta zagina yana cimin mutunci".

Dafa kafaɗarta tayi, sannan ta ce" kiyi haƙuri yaya, wallahi nasan komi kumw nasan abinda yake faruwa sam zuciyoyinmu basa mana daɗi akan abinda yake faruwa, amma ki tuna furucin mahaifinmu kafin yabar duniya, idan kika kashe aurenki da Adam ba shi babu ke kuma Allah ya la'ance ki".......................

Da sauri Umma ta rufe mata baki tana kuka ta ce, na sani Salamatu shiyasa nake haƙuri da dukkanin halin da zan shiga agidan nan, wallahi yaran nan ne suke bani tausayi saboda mugun bakin da yake binsu dashi akullum, shegu matsiyata Allah ya tsine musu ire iren waɗannan zagin aibatawar yake musu, zuciyata tana tsananin bugamin aduk sanda na jiyosa, idanuwana suna raɗaɗi da muradin son zubarda hawaye amma ahaka nake haƙura, saboda nasan halin dana ke ciki sai yafi halinda zan tafi in barsu gashi yanzu anzo har gida an kamasu wanda nasan ubansu yana dawowa zaiyi tsalle ya ce bazai je ba ko kuma ma yayi musu wani mugun bakin".

"uhum ai gaskiya ban taɓa ganin mutum mugu irin mijinki ba yaya Aisha, saboda sam baisan mutuncinki ba ballantana na iyayenki, ni na rasa abinda yasa ma yace in har kika kashe aurenki bai yafe miki ba, ai naji daɗi kake tunawa bana sababa idanda yaji daɗi dashi ne kome ya ce ta zauna, amma babu daɗin zaune balle na tsaye, Allah ubangiji dai ya bawa ƴaƴanki mazaje nagari sai kika har shima ɗan baƙin cikin ya huta ba ke kaɗai ba da yakewa baƙin cikin".

"uhum, ni yaran nanne ma arainq wallahi bansan halin da suke ciki ba? sunci abinci ko basu ci ba? inna lillahi wa inna ilaihi raji'un wallahi ina cikin wani hali Allah ubangiji ya kawomin ɗauki".

"Allah zai kawo miki ɗauki yaya, in sha Allahu ba zaki taɓe ba kuma duk me binki da mugun

sharri sai dai ya ƙare akansa bi'izinillah".

a tsakar gida ya tsaya, ganin ƙofar ɗakin umma kamar da mutane, sai hararar ƙofar ɗakin yake Baba kande tayi saurin fitowa cike da salon munafurci da yaudara ta ce" Malam ka dawo ne? ai da yake gidan yau ba daɗi ina can ina ta tunani shiyasa bansan ma ka shigo ba?".

Da sauri ya ce" tunanin me kuma? meya faru agidan"?.

Da sauri ta ce" uhum ai waɗannan yaran ne suka jajiɓo mana abin kunya akazo har ƙofar gidan nan aka kamasu saboda sunje sunyi faɗa da matar da uwarsu take aiki agidansu wai ko DEENI ko wa!?".

Da sauri ya ce" la'ha'ilallah muhammadurrasulillahi, wannan hamshaƙin me kuɗin DEENI MARSHAL? la haula fisha atillahi au yanzu waɗannan yaran abin kunyar da zasu janyomin kenan? ina zaman zamana su janyomin abin kunya?".

"ato ya zamuyi tunda sun samu ɗaurin gaban uwarsu, ai da sunsan idan sukayi zata tsawatar musu da basuyi ba wallahi, amma da yake sunsan zata sanya musu ido suyita zuba rashin mutuncin da suke so ai kaga dole su kashe ka atsaye".

Da sauri ya ce" ince uwar tasu ce ta dawo ko"?.

"eh itace ai agabansu ma aka tafi dasu tana ta zage zage tana ƙara rura wuta har da zagin matar, wallahi dama ni gobe zan tafi ƙauye kada azo ahaɗa dani haka kurum".

Ai kuwa Baba yakai har wuya, sai zazzaga zagi yake kamar bamaguje har ya ida shiga ɗakin Umma baki ɗaya, sai zazzaga zagi yake gamida aibatawa.

babu kalar zagin da bai yi ba, sannan daga bisani ya ce" kuma wallahi babu inda zanje saboda ni na kusa ciresu a ƴaƴana suje can idan ma shiga duniyar zasuyi suyi domin ni ba asarata bane, dama basu suke ciyar dani ba ballantana idan sun daina inji haushi, sannan ki tafi gidanku kema har sai lokacin da kukayi tarbiyya keda ƴaƴanki ƙwa dawo".

Da sauri mama Salamatu ta magantu da ce wa" haba Babansu Humairah, kayi zaginka da aibatawarka babu wanda aka kula sannan kuma yanzu kace wai ta tafi gidansu? wannan ma ai ba magana bace".

Da sauri ya ce" ke kin isa ki faɗamin magana kiyi shiru ku barni da ita, ƴar masu mugun abu azuciyarsu, kubarmin gidana tun kafin in sanya ayimin waje daku masu butulci kawai".

Mama Salamatu ta buɗe baki a harzuƙe da niyyar yin magana, da sauri Umma ta hanata ta hanyar ce wa.

Umma tana kuka ta ce" Salamatu tashi mu tafi tun kafin zuciyata ta fashe, domin zama acikin gidan nan dai dai yake da fashewar zuciyata domin ni kaɗai nasan halin da nake ciki".

nan da nan taɗan haɗawa Umma wasu daga cikin kayansu, sannan suka fito Umma tana kuka Baba kande tayi musu gwalo. Mama Salamatu tayi irin murmushin nan wanda yafi kuka ciwo sannan ta ce" Kande kafin kiyo mana gwalo ki fara yiwa kanki, domin mudai da kike ganinmu bakya gabanmu sannan ke baki isa kiyi mana komi ba, dama duk abinda kika ga ya faru da sanin ubangiji koda mutum ne silar abun, amma ba dabararsa bace ko wayonsa".

Umma dai tuni tayi gaba, domin bata buƙatar wani surutu, gida kawai zataje ta ajje kayanta ta siya abinci tayi wajen ƴaƴanta don taji ta inda Allah zai kawo musu ɗauki"..................

*Aƙwai grp ɗin da zamu buɗe na yadda mace zata dinga gyara jikinta ciki da waje, sanin ilimin zama da miji da iya shagwaɓa da rarrashi*

*sai grp ɗin koyarda mayafai na bead work, da stone work da kuma koyarda turarukan wuta kala kala*

Duk wacce keso tayi min magana.
07068606171

UMMU MAHER
MISS GREEN
[7/1, 11:54 AM] UMMU MAHER (MISS GREEN)🍃: *_💋ƊAN HALAK💋_*

MALLAKAR
*UMMU MAHER(MISS GREEN)🍃*

_*AREWA WRITER'S ASSOCIATION📖*_

_AREWABOOK_

https://arewabooks.com/book?id=6631fffa0eeb3b80f1ef8159

_WATTPAD_
https://www.wattpad.com/story/368199708?utm_medium=link&utm_source=android&utm_content=story_info

12

_______Bayan babanmu ya gama banbaminsa da masifarshi, ƙaninshi kawu Jafaru ya shigo gidan da sallamarsa hankalinsa a matuƙar tashe jin cewar an tafi da ƴaƴan yayansa folis tashon. Ganin babanmu yasa ya yi turus baki buɗe ya ce "A a mai zan gani yaya? Ni na ɗauka ka tafi wajen yaran nan kuma sai na ganka a gida zaune hankalinka a ƙwance"?.

Wani kallon banza yabi Jafaru da shi sannan ya ce"hum! yaro baisan wuta ba sai ya taka, uban waye yace su gayyatowa kansu abin da suka aikata yanzu? Ai kasan Allah Jafaru? yaran nan suna dawowa sai dai su nemi wani gidan uban amma ba nan ba, yara sun zama yaran masifa ƴaƴan Allah bani, masu mugun hali irin na uwarsu to ni dai baza su kashe ni ba sai dai su kashe uwarsu".
Sosai kawu Jafaru ya yi mamakin babanmu amma duk da haka yasan yaran ma suna da laifi sai ya ce"haba mana yaya, saboda me zaka dinga binsu da wannan bakin na ka mai dafi gare su? Babu kyau hakan ai, an san dai sun yi kuskure kuma na tabbatar yanzu haka sun gane basu kyauta ba, kawa Allah da manzonsa ka taho mu tafi domin mu gano halin da yaran nan suke ciki"?.

"Jafaru kake kowa? Malam dai ba zai je ba, akan mi zaka takura mishi? Sai kace ubanshi? Ƙaninshi ne fa kai? Amma kake nuna kai kamar kaine babba, saboda haka nima ina bin bayanshi kada yaje don Allah su kashe su ma kowa ya huta".
Mamaki ya kusan kashe Jafaru, dama abin da ake faɗa akan Kande gaskiya ne? Shi dai bai taɓa ganin rashin mutuncinta ba sai yau, tunda shi dai ba mazauni bane yana zuwa lagos da jos siye da siyarwa.

Sosai ya harzuƙa har baisan lokacin da ya fara maida martani kakkausa ba. "Kar Allah yasa yaje, idan bai je mutuwa za suyi? Da ki hana shi da ki barshi duk uwar uban ɗaya ne saboda haka kada kaje".
Bai sake magana ba ya fice a zafafe zuwa gidanshi, domin ya ɗibi kuɗi yaje can caji ofis ɗin. A tsakar gida ya tarar da hansai matarshi, tana zaune gaban fanfon yana ƙwaranyowa sannu a hankali, ita kuma tana wanke shinkafa fara domin yin tuwo. Sosai gabanta ya faɗi domin ko sallama bai yi ba, jikinta yana kyarma ta matsa jikin shi sosai har suna jiyo numfashin juna ta ce"lafiya kuwa Baban Audu"?. Ya maida mata da tambayarta a gaggauce ya ce" Wai dama haka Kande take gurza rashin ɗa'a yaya kuma yana biye mata? tsohuwar alakwakwai".
"Hum me kuma ta yi? Domin mu dai har mun saba da rahin mutuncinta, musamman ma ni

ganin cewar kishiyarta mamar Humairah ƙawata ce, shi yasa ko ga miciji bama yi da ita wallahi Baban Audu matar nan muguwa ce, duk ta raba shi da yaransa gashi ita kuma bata haihun ba, ƴan uwanshi ma ɗai-ɗai ne bata rabasu ba"......Tana kaiwa nan ya dakatar da ita wajen cewa"To amma ai baki taɓa faɗamun ba sai yau? Ashe abin har ya kai haka? Kinga irin tsinuwar sa yake jifansu da ita, Yanzu idan bakin ya bisu ya zai yi? Dole ai ba a canjawa tuwo suna".

Taɓe baki tayi, wallahi baza ta bisu ba tunda ai ba suyi mishi komi ba". Tashi ya yi ya ɗibi kuɗaɗe sannan ya fita zuwa wajensu Humaira, har Hansai zata bishi ya dakatar da ita domin yasan za suje ne suyi ta kuka mata da rauni.

acan kuwa tuni Hajiya Babba ta hallara, sai Tasleem, Nasreen, duk yaranta ne sun ƙwama wani uban gilashi. Sai kallon mutane suke ɗai-ɗai tamkar suna jiran ƙiris su hau rashin mutunci, kiran wayar Hajiya Ƙarama ne ya shigo a wayar Hajiya Babba. Tana ji tana gani ta gama sauti ba ta ɗaga ba, sai a karo na biyu ne sannan ta ɗaga ba tare da ta ce komi ba.

"Duk inda kike kizo Alhaji ya dawo yana son ganinki". Tana kaiwa nan ta katse wayar ba tare da ta ƙara magana ba. Tasleem ta ce"uwar me zaki yi mata idan kin koma gidan? Uwar ƴan jin kai har tana baki comment sai kace wata uwarki"?.
Hajiya B. tayi jim ranta a matuƙar ɓace sannan ta ce"to ina zan sani ne? Kinsan Allah Lulu na kusa maganin matar nan a gidan nan, kishiyata ce fa ba uwata ba? Amma na rasa dalilin bani wannan comments ɗin da take yawan bani, ga shi kuma Alhaji baya ganin laifinta sam ni har na rasa ma me zance saboda baƙin ciki, amma a juri zuwa rafi"...

Tun kafin ta ƙarasa ta yi saurin tashi fuskarnan babu annuri, biyo bayan wasu kuɗaɗe da taga ana bawa wani sajan. Bayan shigowar wani mutumi wanda taga suna kama dasu Humairah ko da ba a faɗa mata ba tasan babansu ne.

"Uban waye wannan yake baka kuɗi? Har kake yaƙe tsinannun haƙoranka"?.

Ko ba a faɗawa kawu Jafaru ba ya tabbatar wannan ita ce matar da ta kulle yaransu, ya haɗe gabas da yamma a zuciyarshi yana ce wa Inda ba ƙasa nan ake gaddamar kokawa.
Jikin Sajan ya ɗau rawa, amma sai ya danne ya jajige domin kuwa wannan harkar ba somin taɓi bace a wajen shi, ya ce"A a Hajiya daina zagi haka shi wannan sulhu yazo ba faɗa ba, dama kuma yanzu nake son kiranki sai kuma ga shi kinzo"...
Ƙarar wayarta ita ce ta ƙara sanar mata da in har bata koma gida ba, yau ita da Marshal ne saboda dama basa shiri ya yi tafiya. Tana mugun tsoronshi shi yasa take matuƙar gudun ɓacin ranshi in har ba ta yi abin da yake so ba.

Bata samu zarafin magana ba, ta kaɗawa su Tasleem hannu suka taso jikinsu ba ƙwari domin basu san me ke faruwa a gidan ba?.

Muna hango tafiyarta Ameera ta ce"Insha Allahu mune zamu zamewa matar nan ciwom ido, wallahi tallahi tunda har ta sanya aka kulle mu ita ma bazan barta ta yi farin ciki ba". Ummi ta

karɓe caraf " Faɗa ma ɓata baki ne, ai wallahi sai tasan ta taɓo mu ina dai tana da yara maza ko?". Ameera ta ce"eh yaronta ɗaya ne namiji". Ummi ta yi wani shu'umin murmushi wanda ni da kaina na kasa fassara murmushin da yaran suke yi".

Muna ganin Kawu Jafaru muka fara kuka, sosai muke yi har da riƙe hannun shi idan ka kalle mu sai mun ba ka tausayi, nan da nan muka yi baƙi duk da kasancewar mu farare. Ga yunwar da take nuƙurusarmu domin tun safe muke a cikin sel ɗin, ga wani irin zafi da huci duk da akwai raga-raga amma tamkar dai babu, ga wasu shaiɗanun mata da aka haɗa mu dasu wai an kamasu da kayan shaye- shaye, waɗanda aka kamo a gidan karuwa. Wannan takaicin ya haɗu ya yi min yawa, wai yau mune aka haɗamu da karuwai mu ba sata ba? Ba fashi ba? Ba komi ba, amma haka aka haɗamu da ƴan iska saboda mun yi faɗa da gidan Mashal?.

Kawu Jafaru ya ce" kuyi min shiru, duk ba kune kuka janyowa kanku ba? Kuna cikin rufin asirinki ku ka tonawa kanku? Uban me ya kai ku gidan waɗannan? Harda ku ka yi faɗa dasu? Yanzu kunga gashi zancan dama sajan yake wai kotu za a kaiku, akan kunje har gida kun ci musu mutunci".

Jin abin da yake cewa ya sanyani a cikin wani mummunan hali, da ƙarfi na ce"kotu kuma? Akan me zasu kaimu kotu? Sata? Ko kuma fashi?". Tuni na saki wani irin wahalallan kuka mai tafe da abin tausayi. Kallon banza karuwan nan suka shiga yi mana gami da cewa" Ke! yi mana shiru dalla, kotun uwarki ce ko ubanki? Ko kuwa cewa aka yi za a yanke miki hukuncin kisa? Da za ki ɓarewa mutane shegen ƙaramin bakinki? Shut up!".

Suka faɗa da ƙarfi, ya yinda na ƙara tsorata su Ameera suna gefe suna jan zuciya domin dama ita da Ummi suna da taurin zuciya da taurin kai rin na Babanmu, ni kuma zuciyata irin ta Umma ce. Suma haushina suke ji, saboda kukan dana ishe su da shi su kam sun ɗau aniyar indai har suka fito takan Hajiya Babba za su fara.

¢¢¢¢¢¢¢¢¢¢¢

_HAIDAR_

…"Haidar na ce ka yi aure, amma ka ƙi yi shin so kake na mutu banga aurenka ba? Ga shi yanzu liikita yana faɗin indai har ba ka yi aure ba spam yana taking ɗin rayuwarka zai kumbura matsirarka saboda rashin fitar shi". Sai ta fashe da kuka mai ban tausayi, Mimi ta ce"Sorry Ammi ki daina kuka ai ga shi ya samh lafiya". Ta faɗi hakan a kunya ce saboda abin da Ammi ta

faɗa yanzu ya ba ta kunya duk da dama can tasan da wannan matsalar.

Hammud ya gyara zama sannan ya ce"Ammi akwai wata ƴar ƙanin Baba na tana Zaria tana karatu ana ce mata Amira, kuma yarinyar na yaba da hankalinta wallahi idan da hali a haɗa su aure mana, wallahi zai so ta domin kuwa yarinyar ta haɗa duk abin da ake so a jikin mace, ilimi, tarbiyya, addini, kyau, nasaba, arziƙi".

Ammi ta nisa sannan ta ce" to ba matsala Hammud, idan ta dawo ka yi min magana". Hammud ya ji daɗi sosai domin ya gaji da ganin abokin shi a haka, saboda haka tun yau ya kamata ya yiwa Ameera albishir domin yasan ta daɗe tana matuƙar son Haidar, tun wani zuwa Office da ta yi wajen Hammud anan ta ganshi ta hargitse ta fita a hayyacinta da ganin shi.

Duk abin da suke faɗa yana jinsu, xuciyarshi na mishi wani irin zafi da raɗaɗi wai yau shi ne ake rarraba soyayyarshi zuwa ga ƴammata, tabbas yanza cikin taskon rayuwa ba don amininshi ya yi mishi haka ba da wani ne da tuni sun daɗe da raba gari, amma hausawa sunce sawun giwa ya tadda na raƙumi duk su biyun ba zai iya ja dasu ba, Ammi da Hammud yana jinsu acan cikin ranshi saboda haka yanzu zai haƙura ya sakko, duk wacce Allah ya zaɓa mishi a matsayin mata zai karɓa sai dai inda gizo yake tsakar, shi ne sam bai da ra'ayin auren macen da baya so tabbas idan hakan ta faru zai ƙwari ko wacece ma. Domin kuwa ba za ta taɓa samun farin cikin shi ba ko annushuwa irin na mata da miji ba.

Ammi ce ta katse shirun da ce wa" ni bari na tafi gida, tunda ga Triple ɗin ka a zaune Alhaji ya dawo tun jiya, yana maka sannu ma an jima zai zo meeting ya shiga ɗazu ne a babban hall".

Bai ce ƙala ba, saboda bai san me yasa ba sam baya son mutumin ba wai don ba shi ne mahaifin shi kawai sai domin wani babban sirrin da aka rufe wanda buɗe shi tamkar ɗaukewar numfashin wasu ne, ciki kuwa har da shi Alhajin.

Tasan dama ba zai ce komi ba, saboda haka ta ajje wata rantsatstsiyar kular da suka zubo mai abinci sannan suka fice ita da Mimi. Har sun fita Mimi ta dawo da baya kaɗan, suka kashewa junansu wani irin mayen cingum ɗin kallo ita da sahibinta Hammud, sannan ta yi saurin fita tun kafin Yayanta Haidar ya gansu, A banza tuni ya ga komi a zuciyarshi yana mamakin lokacin da suka ƙulla soyayya mai ƙarfi har haka, ba tare da ya sani ko ya ji labari ba domin a iya saninshi Hammud baya ɓoye mishi komi, ciki kuwa har da sirrikan da ba kowa ne ya sani ba sai shi sai Hammud sai Allah buwayi gagari misali.

₵₵₵₵₵₵₵₵₵

_HAJIYA BABBA_

Sosai ta razana har ta kasa ɓoye damuwarta ta saki ƙara...

*hum, me Hajitya b ta gani ta tsorata? Shin menene abin da ya janyo tsoron?".*

MISS GREEN CE
07068606171
CHART ONLY.📲
[7/1, 11:54 AM] UMMU MAHER (MISS GREEN)🍃: *_💋ƊAN HALAK💋_*

MALLAKAR
*UMMU MAHER(MISS GREEN)🍃*

_*AREWA WRITER'S ASSOCIATION📖*_

_AREWABOOK_
https://arewabooks.com/book?id=6631fffa0eeb3b80f1ef8159

_WATTPAD_
https://www.wattpad.com/story/368199708?utm_medium=link&utm_source=android&utm_content=story_info

🥳🥳🥳🥳🥳_Ina masu son shiga adashe Amma kuna fargaba🤔yar uwa ki tsarkake zuciyan ki kizo kiyi adashe cikin aminci da kwanciyan hankali insha Allah Babu rigima ko tashin hankali kwanciyan hankali zaki Yi adashen ki Kuma mu gama lfyh da yardan Allah..🥰🤝

30k weekly parking 300k

1)Haj Maryam✅

2)Ada umar/hafsat yahya✅

3)Usman

4) barrister hauwa'u

5)shafa bello/baby daura

6)

7)

8)

9)

10)
Akama slot

https://chat.whatsapp.com/HAkm8rINu8a0ouQsRmuDuL

13

_HAJIYA BABBA_

________Farida ƴarta ta gani,  ita da wani saurayinta sun shige wani katafaren hotel, duk wanda ya kwana a wannan garin yasan su waye suka fiye zama a wannan hotel ɗin. Ta saki wata ƙara gami da raza ni, ta tsani ganin mace a cikin hali na rashin tarbiyya tunda take bata taɓa karuwanci ba, ta tsani kuma mai yin shi amma yau ace ƴarta ta cikinta tilo ce a cikin irin wannan hali?.

  Lulu ta ce"jar uba lallai anti Farida ta iya gilla ƙarya, ce min fa tayi ta tafi skull kuma kin ganta Hajiya ita da wani? Haba don Allah wanman ai munafurci ne".  Nasreen dai saboda mamaki kasa magana ta yi, Hajiya kuwa tuƙi take hannunta yana kakkarwa ga baƙin cikin abin da ya faru ma zagin da yaran can suka yi mata ga baƙin cikin abin da ƴarta ta cikinta ta yi.
gudu sosai Hajiya Babba take har Allah ya kawo su gida, saboda babu wanda zai ga gudun da

suke ya ce zasu je gida lafiya".

Hancin motarsu ya danno gidan, Alhaji Deen ta gani tsaye a farfajiyar gidan yana rabo kamar yadda ya saba bayan ya dawo daga tafiya. Ta tsani wannan al'adar ta shi ta rabon kuɗi, domim kuma Allah ya baka kuɗi sai ka yi ta rabarwa? Duk da tasan ko zai kwana dubu yana raba kuɗi, kuɗinshi ba za su rago ba sai dai ma su daɗu. Ba iya sadakar da yake yi ba, duk duniya idan ya wuce ita da yaranta ba ta so ko jin ya bawa wani ko wata wani abu, tana matuƙar jin haushin hakan shi yasa ita da ƴan uwanshi musamman na ƙauye babu wani sabo ko haba-haba da jama'a, amma Hajiya Ƙarama ita ce ta ɗauke su tamkar ƴan uwanta ciki ɗaya.

Tsabar haushi bata tsaya ba ta yi wucewarta, a cewar ta idan yaga dama ya biyo ta ɓangarenta. Damuwar da take ciki ita ce ta mantar da ita shin waye Alhaji Marshal tasan izzar shi da isar shi musamman ma akan matan shi.

Iya Abu ce ta fara cin karo dasu a ɓangarensu, Lulu ta yi kamar ta harbeta ma kowa ya huta, tunda duk ita ce ta yi silar faruwar komi Nasreen kuwa ta galla mata wata uwar harara tamkar dai za ta cinye Iya Abu ɗanya. Ni kuwa Ummu maher na ce, oh duk mutum ɗaya akewa wannan? Sai kace wata nama? Baiwar Allah ga ta tsohuwa.
Ta risinar da kanta sannan ta ce"sannu da zuwa Hajiya, ya..." Tun kafin ta ƙarasa faɗar abin da za ta ce ɗin Hajiya Babba ta ce" Za ki matsa na wuce ko kuma sai na bige ki na wuce? Munafukar tsohuwa annamimiya, wallahi tallahi sai kin kwashi kashinki a hannu dani ki ke magana".

Tasleem ta danne babban ɗan yatsan Iya Abu, da wani takalminta mai mugun tsayi tamkar za ta tsallake sama.
wata uwar ƙara ta saka, tamkar za ta sakj fitsari wanda dama jin fitsarin ne ya korota daga cikin kicin ta fito domin yi, sai ga shi Allah ya haɗa ta da waɗannan yaran masu mugunta tamkar ƴaƴan fir'auna. Mai makon ta sakar mata ƙafar sai ta ƙara takawa gami da nuna ta da yatsanta ta ce" Ai indai baza ki daina munafurci ba ba za ki daina shan wahala a waje na, banza uwar gulma kuma wallahi kotu zamu kai yaran nan sai sun yi prison, kema za ki ɗanɗana kuɗar ki tunda ke ce mai ɗaur musu gaba".

Iya Abu ta saki wani marayan kuka, sautin kukanta yana tashi tamkar marainiyar da take neman iyayenta ido rufe. Ta daɗe a zaune tana tsinewa Hajiya Babba da yaranta, domin ta daɗe da sanin sam ba suna da imani basu san ma msye wai shi imani ba, ga kuma tausayin su Humaira da ya cika mata ciki. Yaran da suka zo neman taimako domin biyawa mahaifiyarsu kuɗin asibiti, sai kuma a ɓige da kai yara folis domin sun yi sa insa dasu? A zuciyarta tana Allah wadai da wasu masu kuɗin, domin ta fuskancin yaransu kawai suka sani da matansu su yi ta ɗaure musu gaba, suna cin karansu babu babbaka. Duk dama shi Marshal baya wulaƙanta ɗan adam, sai dai yana matuƙar son yaransa ta yadda komi za a ce sun yi in har matuƙar bai gani ba to ba suyi laifi ba, shi yasa ma suke yin abi da suke so, ga kuma Hajiya Babba a gefe wacce ko su masu aiki sun shaida irin tsantsar ƙaunar dake tsakanin ita da yaranta.

Yaran Hajiya Babba 7 ne, babbansu shi ne Tahir, Sadik, Farida, Jamal, Tasleem, Nihla, Nasreen. ba kowa ne yasan tana da yara da yawa har haka ba, saboda mafiyawancinsu duk basu ƙasar, Nihla, Jamal, Sadik, dukkansu basa ƙasarmu Nigeria suna ƙasar daular turawa greece, acan ne suke karatu kuma a yanzu haka Sadik ya fara aiki acan da yake ya karanci fannin likitanci, kuma fannin da ya karanta kusan shi ne scientist ɗin wato fannin ƙwaƙwalwa, sosai ya ƙware ya tumbatsa har ya gagari kundila, saboda haka sai Allah yasa suka riƙe shi acan, Nihla ma fannin lafiya ne amma yasha babban dana yayanta domim kuwa ita mai kacokan ce likitar mata, wanda ta haddace ta kuma gwanance gurin fannin mata, ita ɗin ma dai sun riƙe ta domin kuwa ta fara aiki dasu, sai dai kash! shi kuma Jamal gaba ɗaya gwara ma bai je wata ƙasa ba, domin kuwa babu abin da ya karanta sai tsantsagwaron iskanci, da iya safarar miyagun ƙwayoyi wannan fannin kuwa sai dai a kira shi da prof. Domin kuwa yasan takan fita da duk wasu miyagun ƙwayoyi, wajen shansu kuwa nan ma ba a magana domin kuwa ya ƙware ya kuma gwanance tsaf ya kuma haddace. Alhaji Marshal sarai yasan halin da ɗan na shi yake ciki amma ya yi biris sa hakan, domi kuwa babu yadda bai yi ba wajen ganin ya daina duk abin da yake, amma idan ya tare nan sai ya koma can saboda haka ne ma yasa ya sanya mishi na mujiya, domin shi baya cikin iyaye masu matsawa yaransu idan ya hana ka kaƙi  sai ya yi banza da kai ka yi rayuwarka, irin rayuwar yahudu da kuma nasara.

mu koma wajen Hajiya.
Nasreen ta shigo gami da ce wa" ni fa wallahi Hajiya na tsani waccan tsinanniyar mata, idan na ganta sai naji tamkar na bindige ta na huta sai iyayin tsiya da son nuna ita musulma ce, to uban waye ba musulmi ba?.

 Hajiya ta ce" wacece wai"?.

!Wacece kuwa idan ba Hajiya ƙarama ba, wai yanzu ta aiko na zo akan fara zuwa islamiyyar nan, ni da Mimi wai zamu dinga zuwa to ni na ce mata inason yi ne? Haba".
Gyaɗa kai kurum ta yi sannan ta ce"Nasreen ke kanki kinsan halinta, tamkad mayya take duk abin da ta sanya a gabanta sai ta ga bayan shi, shi yasa nima yanzu na ɗauki aniyar ganin bayanta ko ta halin ƙa-ƙa".

Lulu ce ta shigo da wayarta da murnarta ta ce" Hajiya gobe my sibling za su dawo fa, how comes da za su yi mana suprise". Ta faɗi hakan tana miƙowa Hajiya wayar.
Duk wannan ƙuncin d Hajiya ke ciki sai ya yaye d sauri ta ce" kai yaran nan sun iya suprise, kinsan Allah ba su faɗa..."

Mimi ce ta shigo da fara'arta ta ce" Hajiya ina yini?".

Ko kallo bata ishe ta ba, haka ta ƙara mata magana  akaro na biyu ba tare da ta duba rashin amsawarta ba.

"Ke! dalla malama ki yiwa mutane shiru, ƴar gadon maita kawai haba don Allah wi shin dole ne

sai na yi magana? Uban me ya kawo ki sasheba? Ban ja miki kunne ba? Shegiyar yarinya kawai".

Sosai maganar ta daki kunnen Mimi, wannan kalmar ta yi muni kuma ta yi tsauri sosai wai ita ce shegiya, ƴar gadon maita? Mimi ta zuciya a wannan lokacin yin shirunta zai cigaba da cutar da ita da kuma mahaifiyarta, saboda haka tuni ta buɗe baki ta ce" ai ba a shegiya ɗaya sai dai ayi shegu biyu, saboda haka ni ba shegiya ba ce sai dai idan ku..."

TAS...TAS...TASSS!!!

Tuni ta ji wasu irin tagwayen maruka har guda biyu, waɗanda Hajiya Babba ta yi mata, sannan ta nuna ta da yatsanta ta ce" ke har kin isa ki zageni, to ko uwarki da ta dire ɗan shege a gabanta ƙaryarta ta zage ni ballantana ke karan kaɗe miya, shasha marar mutunci kawai".

Ta yi gaba har tana ture Mimi, ta yi taga-taga za ta faɗi ƙasa Lulu ta sanya ƙafa ta harɗe ta ji kake tim a ƙasa, Mimi ta saki ƙara tamkar ranta zai fita saboda tsabar azabar da take ji.

Nasreen ta taɓe baki gami da ce wa"shegiya ki mutu ma kowa ya huta gayyar tsiya, bara gurbi kawai".

Kuka Mimi ta fara mai sauti, ga wani irin azabar da hannunta yake mata, abin ka da farar fata nan da nan sai ta yi jawur tamkar ɗanyan nama. tasowarta har zuwa yanzu basu taɓa sonta ko na second ba, ko da yaushe tsakaninta dasu sai hantara da zagi tamkar dai ba mahaifinsu ɗaya ba. Kalmar da tafi ɓata mata rai ita ce uwarki ma ta ajje ɗan shege, sosai take jinta aranta ita ma taji hakan? Ina ga yaya Haidar?. Innalillahi wa inna laihi raji'un, abin da ta dinga nanatawa kenan ta tashi da ƙyar tana hawaye ga hannun har ya fara kumbura.

juyawar da za ta yi, sai ta yi saurin yin baya saboda tsoron ganin shi da tayi ta ƙwalalo idanuwa waje tamkar za ta saki fitsari.....

MISS GREEN CE
SHARE
COMMENTS➡📱👏
07068606171
CHART NO CALL
[7/1, 11:54 AM] UMMU MAHER (MISS GREEN)🍃: *_💋ƊAN HALAK💋_*

MALLAKAR
*UMMU MAHER(MISS GREEN)🍃*

_*AREWA WRITER'S ASSOCIATION📖*_

_AREWABOOK_
https://arewabooks.com/book?id=6631fffa0eeb3b80f1ef8159

_WATTPAD_
https://www.wattpad.com/story/368199708?utm_medium=link&utm_source=android&utm_content=story_info

Ina masu son shiga adashe Amma kuna fargaba🤔yar uwa ki tsarkake zuciyan ki kizo kiyi adashe cikin aminci da kwanciyan hankali insha Allah Babu rigima ko tashin hankali kwanciyan hankali zaki Yi adashen ki Kuma mu gama lfyh da yardan Allah..🥰🤝

30k weekly parking 300k

1)Haj Maryam✅

2)Ada umar/hafsat yahya✅

3)Usman

4) barrister hauwa'u

5)shafa bello/baby daura

6)

7)

8)

9)

10)
Akama slot

https://chat.whatsapp.com/HAkm8rINu8a0ouQsRmuDuL

*AYI HAƘURI, AN SAMU MATSALAR EDITING NE A WASU PAGES, AMMA YANZU AN GYARA MUSAMMAN WAƊANDA SUKE KARATU A WATTPAD SAI DAI SU YI HAKURI SU CIGABA DA KARANTAWA HAKA.* NA GODE MASOYANA.

14

_MIMI_

________Ta faɗa da ɗan ƙarfi Ruhi me kake yi anan kuma?!".

Sosai yake kallon hannunta ganin ya kumbura ya ce"my baby me ya faru dake haka a hannunki"?. Kallon hannun ta yi tana zubar da ƙwalla ta ce"su Nasreen ne da Tasleem wai akan na zo kiran Hajiya". Ranshi ya ɓaci sosai kana hango hakan a idon shi har ma da fuskarshi, danne ɓacin ran ya yi amma sam zuciyar shi babu daɗi, ya rasa wani irin so yake wa yarinyar duk dama ta kasance ƙanwar amininshi dole dama ya so ta, amma duk da haka son da yake wa Mimi ya yi yawa. Ba kunya ya janyo ta jikin shi yana ce wa "sannu my baby, dama naje sashen Ammi ne shi ne tace min kina nan sai na biyo ki, sannu fatan baza ki faɗawa Ammi ba ko"?. Ta fara kuka tamkar yarinyar goye tana ce wa"Allah Ruhi sun tsane ni, na rasa me na yi musu wallahi kullum cikin yi min mugunta suke musamman ma Tasleem ta tsaneni, nasha kulle ɗaki na yi kuka saboda cin kashin da suke mana ni da Ammi ya Haidar, musamman ma mummunar kalmar da suke faɗa akanshi, ina ji kamar na shaƙesu saboda haushi amma don rainin hankali idan a gaban shi ne basa faɗa mishi sai a bayan idon shi". Ta fadi hakan tana kuka, saboda raɗaɗin da take ji a hannun ta.

Wani ɗan sanda ne ya kira Hajiya babba, tana fitowa da niyyar zuwa wajen Alhaji Marshal sai ta koma kai tsaye gida, ta ɗakko mayafinta suka fice ita da Tasleem.

Tana fitowa Munir ya kirata, yana tambayar me taje yi folis ɗazu? Yanzun haka yana cikin station ɗin.

Ƙala bata ce ba kai tsaye ta wuce da motarta, sai dai abin da ya bata mamaki bai wuce ganin ɗanta Munir a wajen ba.

*MAMA SALAMATU*

_______Mama Salamatu ta biyo bayan Umma tana ta sababi, Umma dai tuni tayi gaba abinda ke gabanta kawai take tunawa yaranta har guda uku a folistashon.

"Allah ya wadaran ahalinku marasa mutunci waɗanda basusan annabi ya faku ba".

Baba ne yake faɗin hakan yana shigewa ɗakin Baba kande, ita kuma sai zugashi take domin daman shi bai ƙi zuga ba ɗan abu kaɗan zai sa yahau kamar ƙwaɓin fanke.

****

"Ai waɗannan yaran yau sai sun san sun taɓoni, wallahi tallahi na rantse da wanda raina yake hannunsa sai sunyi gidan yari waɗannan yaran, marasa kunya iyalan malam audu me dattin hula ƴaƴan talakawa waɗanda suka ɗaurewa talauci gaba".

" ni fa babu wacce nafi tsana irin waccan yayar tasu, me take da suna ma? Humaira ko umaimah?".

Cewar Tasleem wacce take ta harararsu tana musu gwalo, su kuma suna cikin sell suna shan azabar zafi domin sell ɗin irin ɗan ƙaramin nanne, wanda numfashinka ma da ƙer zaka dinga shaƙa.

"Anti Humaira wallahi bana nadamar zuwana wajen nan, tunda naga alamar ba suda mutunci kuma har yanzu basu ɗauki talaka abakin komi ba".

Cewar Ameera wacce ta haɗa zufa sosai.

Ummi ta yamutsa fuska ta ce" uhum ni tunani na ɗaya ne Umma, domin kuwa nasan yanzu tana can cikin wani hali, ga matsalata da Baba kande kan wancan Alhajin ga kuma wannan matsalar, abin zaiwa Umma yawa gashi ba tada wanda zai ƙwantar mata da hankali".

"Akwai Allah ai, sannan nasan duk inda take yanzu tana kan hanyar zuwa gidansu, sannan mama Salamatu baza ta taɓa barinta haka ba za ta dinga ƙwantar mata da hankali".

Cewar Humaira baiwar Allah, wacce idanuwanta suka jiƙe da ruwan ƙwalla domin duk cikinsu ita kaɗai ce tayi kuka, domin ni ina da raunin zuciya su kuma ba suda shi yadda kasan masu zuciyar maza haka suke.

wani ɗan sanda ya kallemu sosai, sai naga ya ƙaraso inda muke ai kuwa nan da nan Hajiya Babba ta ƙaraso inda muke har tana haɗawa da tumtuɓe Tasleem tana binta tamkar zata karye saboda sirantaka.

"Ƴan mata me kuka yi aka kawo ku nan"?.

Da sauri Ummi ta ce" saboda zalunci mana, babu abinda mukayi har gida wata tazo ta sanyamu agaba mu duka uku aka kawomu nan".

Ɗan sandan yayi shiru, Hajiya Babba ta gallama mana harara sannan ta ce" mara kunya, yaran talakawa in sha Allahu rayuwarku a birsin zata ƙare".

Ameera za ta yi magana na riƙe mata hannu alamar ka da ta ce komi, shirun kuwa tayi tunda dukkansu babu wani me ƙin bin umarnina, idan na tsawatar musu tamkar Umma ta tsawatar ne.

"Da ki yi magana mana, ƴar talakawa jikan talaka......."

Cewar Hajiya Babba, wacce take ta faman hura hanci tana ɗagawa.

Da sauri ɗan sandan nan ya dakatar da ita ta hanyar ce wa" haba Hajiya bai kamata kina kula waɗannan yaran ba, tunda kin yi jikoki dasu sannan bai kamata anan kina ɗagawa mutane hankali ba".

ƙwarjinin da yayi mata shi ne yasa tayi shiru, amma sam bata so ya hanata ba taso ne taci mana mutunci tunda mu mun zama marasa gata.

*******

Munir ya ce" haba Hajiya me kuma ya haɗaki da yara? da zaki je ki kaisu wajen ƴan sanda? sannan yara ƴan mata har guda uku kuma duk yaran mutum ɗaya? haba Hajiya bai kamata ba wallahi".

"to sannu mara mutunci, wanda baisan darajar uwa ba yanzu har kai ne zaka zo kana faɗar haka? agaban mutane saboda kaci min mutunci? to bari kaji tunda kai bakasan mutuncina ba ai yarana mata sunsan mutunci na".

Munir yayi shiru, yana kallon tsala tsalan ƴammatan waɗanda aka rabosu da iyayensu aka kawosu nan, saboda kawai tana tutiyar tana da kuɗi ya rasa me yasa Hajiyar take wulaƙanta talaka, alhali ita da kanta ƴar talakawan ce jikar talaka amma ahaka mahaifinsu ya aure ta kuma ya sakar mata komi sai yadda tayi dashi, ko ƴan uwansa basu isa suce ga yadda za'ayi ba amma ita tana ce wa ayi kaza sai kaga anyi.

wayarsa ya ɗakko ya kira Hajiya ƙarama kishiyar Mamansa, nan da nan ta ɗaga ta ce" ɗan arziƙi lafiya kuwa ɗazu naje ɓangarenka ban same ka ba, nayi ta kiranka nan ma ban same ka ba?".

"Mami ke dai bari, wallahi Hajiyarmu ce ta haɗosu da wasu yara ƴammata, to fa shi ne ta kawosu wajen ƴan sanda yanzu haka ma ina can".

Jikinta yayi sanyi sosai, ranta kuma ya ɓaci sosai wato ita Hajiya har yanzu batasan annabi ya faku ba? ace wai kina da yara har guda uku amma ace wai bakisan darajar yara mata ba har kina kaisu wajen ƴan sanda saboda aci musu mutunci, zato zunubi ne ko da ya kasance gaskiya amma ta tabbatar Hajiya ce ta tsokani waɗannan yaran, domin tasan halinta sama da shekara ashirin take tare da ita tafi kowa sanin mugun halinta.

ta samu kanta amai kira Munir, yana ɗagawa ta ce "zanzo wajen yanzu ka ƙwatantamin"?.

Jikinsa a matuƙar sanyaye ya faɗa mata wajen sannan ya kashe wayar, domin yasan in har Hajiya Babba ta samu labarin shiya faɗawa kishiyarta wannan maganar sai ta kusa yi masa baki, domin akaf duniya yasan babu wanda ta tsana irin Hajiya ƙarama kishiyarta, ya rasa me yasa? domin yasan kishiya ai ƴar uwa ce idan da mutunci.

Tun daga nesa Hajiya Babba take kallonta, ranta amatuƙar ɓace tuni fuskarta ta koma tamkar ta shanu saboda tsabar haushi, tun da jajayen sahu ta tsani Aisha, sam bata sonta ko kaɗan tun lokacin da mijinta ya auro ta tayi ƙaura da farin ciki.

Aisha macece kyakkyawar gaske, fara sol ga ta da kyaun jiki da kuma kyawun sura. Aisha tana ƴar shekara 15 aka auro ta mahaifinta hamshaƙin me kuɗi ne wanda ya amsa sunansa, gidajen radio da talabijin ko ina ka zaga aikin alkhairinsa ake yaɗawa saboda shi mutum ne me taimakon talaka, shi kuma Alhaji Mashahud yaronsa ne, wanda ayanzu haka ya koma Alhaji Marshal saboda sunansa dana Aisha dake haɗe saboda soyayyarsu.

Babu haukar da Hajiya babba batayi ba, wato Hajiya Habiba uwar gidan Marshal akan ta tsani auren Aisha da mijinta, amma da yake Allah yayi Aishar matar Marshal ɗin ce dolenta ta haƙura, tunda babu yadda za tayi domin ita da kanta Aishar ba son Marshal ɗin take ba, mahaifinta ta yiwa biyayya ta auresa wanda alokacin tsaf Marshal zai haifi kamarta tunda yana da kusan 38 ya aure ta.

Sam Hajiya babba bata san da Hajiya ƙarama ta ƙaraso ba, har sai sa ta ƙaraso inda take ta wannan mayen ƙamshin da take amfani dashi ya daki hancinta, ai kuwa fitgigit ta farka daga mummunar duniyar hassadar ta, sannan ta ce" ke kuma meye ya kawo ki nan? anzo munafurci da iyayi da karuwanci ko"?.

da sauri Aisha ta kalle ta sannan ta kawar da kanta, har ga Allah taji haushi sosai amma ba tada yadda za tayi dolenta kome ta ce mata ta amshesa hannu bibbiyu, saboda ayanzu haka ita ta kawo kanta kome ta faɗa mata ma ba laifinta bane, sannan bai kamata ma sam ta biye mata ba saboda haka kai tsaye ta wuce ofishin babbansu saboda taji matsalar.

ko da tazo wucewa gabanta ne ya tsananta faɗuwa, ta ƙaraso da sauri saboda ta gane Humaira sosai domin sanda mahaifiyarta tana aiki agidan tana yawan ganin yarinyar, saboda haka ta ƙaraso da sauri ta ce" daman kune Hajiya babba ta kulle? me kuka yi mata haka"?.

cikin kuka na fara yi mata bayanin komi, domin nasan matar dama kuma kaf mutanen gidan bayan ita da megidan sune masu mutunci amma daga Hajiya babba har yaranta duk kanwar ja ce.

Shiru tayi, sai naga ta goge ƙwallar idonta sannan ta ce" babu komi kada ku damu zaku fita yau ɗinnan in sha Allah".

Muka amsa da "Amin".

ita kuma ta shiga daga ciki wajen folis ɗin.

"yallaɓai kunfa san aikinku sarai, saboda me zaku dinga biyewa irin waɗannan masu kuɗin da babu abinda suka sani sai cutar yaran jama'ah? domin sunsan ko me zasuyi musu gwamnati ba magana za tayi ba, tunda sunsan ba suda shi saboda haka ni dai da muryar adalci nazo ba wai zan bada kuɗi domin asakesu bane, ayi musu adalci a komar dasu gidan iyayensu".

DPO ya gyara zamansa akan kyakkyawar kujerarsa me juyawa, sannan ya ce" ba komi Hajiya Aisha Marshal in sha Allahu ayau ba gobe ba zasu bar wajen nan, domin nima da kaina nayi bincike sosai kuma na gane gaskiyar komi, sai dai zamuja musu kunne akan su daina zagin babba ko da shi babban ne ya yada girmansa, kuma zasu bata haƙuri domin amatsayinta na babba bai kamata su zage taba".

"naji na kuma yarda DPO nasan sunyi laifi amma ayi musu uzirin ƙuruciya, domin yaran suna da mutunci da mutuntawa kuma sunsan mutunci".

haka dai yayi ɗan rubuce rubucensa sannan ya ce" ki kirawomin sajen awaje ya shigo dasu sannan sai ayi abinda za'ayi su koma gidajensu".

Hakan kuwa akayi, aka fito dasu Humaira ganin an fito dasu Hajiya babba ta wani wurgo daka kan kujerar da take, yadda kasan zata daki sajen ɗin ta ƙaraso da faɗanta da hargagi tana son zaginsa.

wani kallo ya wurga mata sannan ya ce" Hajiya ki kiyayi bakinki idan kuwa ba haka ba xa'ayi ƙaiƙayi koma kan masheƙiya su sun fito ke kuma kin koma inda suka fito, domin naga alama da irin wajen nan kika dace".

Haba wa, wannan maganar daya faɗa ai sai ta harzuƙa hajiya ta inda take shiga ba tanan take fita ba tana wani irin zagi wanda kana jinsa kasan cin mutunci ne ɗanyensa.
Munir sai haƙuri yake bata amma ko kallonsa bata yi ba, baisan shima haushinsa take jiba domin tasan babu wanda zai faɗawa Aisha sai shi, shi da Aisha aƙwai amana saboda rabin rayuwarsa a ɓangarenta yayi....................

*$HAJIYA KARAMA*

*$ HUMAIRA*
*$ UMMI*
*$ AMIRA*
*$ HAJIYA BABBA*

UMMU MAHER.
[7/1, 11:54 AM] UMMU MAHER (MISS GREEN)🍃: *_💋'DAN HALAK💋_*

MALLAKAR
*_UMMU MAHER(MISS GREEN)🍃_*

*_AREWA WRITER'S ASSOCIATION📚_*

~*Arewabooks*~
D'AN HALAK:: https://arewabooks.com/book?id=6631fffa0eeb3b80f1ef8159

~*Wattpad*~
D'AN HALAK
https://www.wattpad.com/story/368199708?utm_medium=link&utm_source=android&utm_content=story_info

MAHER'S COLLECTION
https://chat.whatsapp.com/C3tsX4CqiEp939DhYvJ3SZ

Ina masu son shiga adashe Amma kuna fargaba🤔yar uwa ki tsarkake zuciyan ki kizo kiyi adashe cikin aminci da kwanciyan hankali insha Allah Babu rigima ko tashin hankali kwanciyan hankali zaki Yi adashen ki Kuma mu gama lfyh da yardan Allah..🥰🤝

30k weekly parking 300k

1)Haj Maryam✅

2)Ada umar/hafsat yahya✅

3)Usman

4) barrister hauwa'u

5)shafa bello/baby daura

6)

7)

8)

9)

10)
Akama slot

https://chat.whatsapp.com/HAkm8rlNu8a0ouQsRmuDuL

15

_______Tun tana hana shi zuwa ɓangaren Aisha har ta dena, domin shi yaro idan jininsa ya haɗu da abu da wuya kace zaka cire masa shi lokaci ɗaya, akwai sanda suka yi rigima da Aisha baki ɗaya Munir Hajiya babba ta tirsasawa mahaifinsa da ya kaishi bodin, da yake duk abin da take so yana so nan da nan aka kaishi karatu ƙasar waje lokacin yana ɗan shekara 13, anan ya cigaba da rayuwarsa har ya yi shekara 27 sannan ya dawo, bayan ya kammala digiri ɗinsa aƙasar Tunusia.

Ɗan sandan yayi rubutu, sannan ya bada odar fito damu, idanuwanmu sun yi jawur saboda kuka musamman idan muka tuno da halin da Umma za ta iya shiga, domin duk inda take yanzu hankalinta idan ya yi dubu ya tashi.

Ya ce" ina son ku bawa baiwar Allahn nan haƙuri musamman akan rashin kunyar da ku ka yi mata, sai asanya hannu kubar wajen nan baki ɗaya, domin ganin dacewar hakan yasa muka yanke wannan shawarar, sannan abu na biyu sel ɗinmu ya cika da mutane bama buƙatar yawan jama'a domin tun ɗazu aka kawo wasu gasu can a zaune, kunga da kun bar ɗakin sai su shiga".

Tunda ya fara maganar Hajiya babba ta saki salati, sannan ta ce " Ni awa zasu bani haƙuri? Ai waɗannan ƴaƴan ƙwaltan ba iya bani haƙuri za suyi ba, ko da ma sun bani haƙurin ai sun cuce ni saboda sun ci mutuncina, ni kuma wallahi basu bama duk wani me ji da rashin mutuncinsa na fisa iyawa, saboda haka su riƙe haƙurinsu kawai idan ma ba zaku ƙwatar min haƙƙina ba nasan

ni inda zan kai, kuma wallahi duk sai kun yi nadamar abin da ku ka yi".

Ganin tana ta masifa kowa yayi shiru yana jinta, domin babu wanda zai kulata ganin ayanayin yadda take faɗan idan ka kulata jarabar tata gaba za tayi ba baya ba, domin kome za'a faɗa mata ba yarda dashi za tayi ba, kawai gani za tayi ai anbi bayanmu.

Bayan mun fito Munir ya biyomu da sauri, Hajiyarsa ta daka masa wata uwar tsawa tamkar tsawar dake rugugi acikin samaniya, ko kuma tsawar amon wuta me tafe da sauti sosai.

Abin da zai baka mamaki yadda Munir ya maze ya yi wucewarsa, ya buɗewa Hajiya ƙarama gaban motarta sannan shima ya shiga, ya bamu umarnin shiga cikin motar jikinmu duk amatuƙar sanyaye, domin ni na tabbatar ayanzu haka Umma tana cikin tashin hankali mara misaltuwa.

Har ƙofar gida suka kawomu, bisa jagorancinmu Munir ya fito da sauri ya buɗe murfin ƙofar da take ɓangarena. Yadda kasan zai ƙwanta na taka bayansa na wuce, haka ya yi min domin har rausayar da kansa yake saboda tsabar jin tausayina.

Har cikin gidanmu Hajiya ƙarama ta biyomu, jikinta duk yayi sanyi a yanayin da ta same mu amma sai ta daure bata nuna hakan ba, amma jikinta duk ya yi matuƙar sanyi zaka fuskanci hakan ayanayin kuzarinta. Domin duk wani karsashinta ya ragu sosai, kai talauci bai yi ba domin annabi ma da kansa ya nemi tsarinsa, (S.A.W) domin talauci wani babban kataɓus ne arayuwa da zai hanaka gaba balle baya ya Allah muna roƙonka ka fitar damu daga ƙangin talaucin da muke fama da shi Amin.

Baba ne atsakar gida, yana hangota yayi saurin tashi da fara'arsa kamar dai daman can ya santa, sai kuwa ya gimtse fuskarsa lokaci ɗaya saboda ganinmu tare da ya yi. Ganin hakan yasa Hajiya ƙarama ta fuskanci aƙwai wani lamari, amma bata nuna ko a fuska ta gane abinda ya ke nufi ba, domin ance labarin zuciya a tambayi fuska.

Baba kande ta ɗakko mata kujera da sauri, ta samu waje ta zauna tana yiwa Baba kande kallon tsaf domin aɗan lokaci kaɗan ta fuskanci wacece ita, domin ayanayin mutum da mu'amalarsa kana gane komi, na farko taga sauyin fuska sosai alokacin da Baba kande taga ta shigo da yaran, sai taga ta haɗe fuska tamau tana wani muzurai tamkar dai za ta kawo hannu ne.

Bayan sun gaisa Hjy Ƙarama ta ce" dama waɗannan yaran na rako gida, amma ashe ba nan gidan bane domin alamu sun nuna ba nan ne gidansu ba, domin da nanne gidansu zanga kun nuna damuwarku da alhinin abin da ya same su na ƙaddara".

Da sauri Baba ya kallemu, sai kuma ya haɗe girar sama da ta ƙasa ya magantu da ce wa" eh tabbas nanne gidansu sai dai sam basa daga cikin yarana, musamman waccan munafukar".

Ya nuna ni da manuniyarsa, yana me dalla mini harara wasu zafafan hawaye suka shiga ƙwaranyo mini na sanya gefen yalolon mayafina ina sharewa, tabbas an shiga tsakanina da mahaifina tsakani me doguwar wutsiya tamkar wutsiyar raƙumi, domin ni ɗinnan yarinya ce ƴar gatan gaske wajen mahaifinta, da yaji kuka na gwara yana zaune ka taƙarƙare ka maresa, domin yana sona sosai kasancewa ta me sunan mahaifiyarsa kuma ƴarsa tilo daya fara samu aduniya, kafin yasa kowanne ɗansa ni ya fara sani aduniya saboda haka duk wata ƙaunar da zai yiwa ɗansa to bari na ne, domin ni da kaina na shaida kuma na tabbatar ni ƴar lelen babanta ce kuma shalelensa maganin kukansa, tun ranar daya auri Baba kande har zuwa rana me kama ta yau Babana bai taɓa buɗe baki yayi min addu'ar samun cigaba ba, ko kallona baya sonyi saboda wai ni ba nida kunya ina yiwa matarsa rashin kunya, ni kuwa indai akan a taɓa Umma ne inyi shiru a cutar min da ita shiyasa bana jurar rarrasar zuciyata wajen yin shiru idan har an taɓa ta ɗin, musamman Baba kande sam bana mata uzuri ko kaɗan idan har ta taɓa Umma na bana shiru, har ta kai ta kawo yau agabana Baba Kande za ta zagi Umma na amna ban isa ko ɗaga kai nayi ba, saboda furucin Baba akan fushin Baba kande akaina, tun lokacin da ta faɗa na faɗa kuma yaji saboda haka sai yayi min babban baki akan in har na yarda na ƙara faɗa mata magana akan mahaifiyata Allah ya isa bai yafe mini ba, saboda haka tun daga nan nasha jinin jikina na daina yiwa kai na ingiza me kantu ruwa na daina kula ta sam, in dai ba abin yaci tura ba.

Ina cikin wannan tunanin naji Hajiya ƙarama ta baje kolin sallallami tana ce wa" ya subhanalillahi, me ya kawo maganar cire su daga cikin yaranka? su fa ƴaƴa rahama ne sannan ubangijin daya bamu su kiwo ya bamu bawai namu ne ba, duk abinda yayi zafi maganinsa Allah".

Da sauri Baba kande ta ari bakinsa taci masa albasa ta ce" haba ke kuwa baiwar Allah, ina ruwanki da wannan batu wannan ai tsakanin uba da yaransa ba a shiga ko da kuwa ita ce ta tsugunna ta haife su".

Baba ya yi saurin gyaɗa kansa, alamar gamsuwa da maganar ta. Amira tayi karaf ta ce" mijin ta ce ko kafin ta ce".

ta faɗi hakan ba tare da ta kalli kowa ba.

Baba ya kawo mata mazga domin babu wanda baiji abinda ta ce ba, ni kuwa gabana ya tashi sosai domin ko giyar wake nasha bazan faɗa ubana ya faɗa ba, domin duk abinda kake nema na duniyar nan banza ne indai babu albarka iyaye, saboda haka tun kafin Baba ya kai mata duka ni nayi saurin wanke ta da mari ina shirin ƙara mata Hajiya ƙarama tayi saurin ce wa" haba ke kuwa Amira me yayi zafi haka?, maza zauna kuyi haƙuri dukkanku amma inaso ki sani duk lalacewar uba ko uwa to fa ba a canjawa tuwo suna".

Baba sai ciccika yake yana yi mana wani wulaƙantaccen kallo irin wanda ya ke wa Ummanmu aduk sanda ta yi masa wani laifi ko matar sonsa Baba kande.

¢¢¢¢¢¢

_HANAN_

Cike da razani Hanan ta ce" whats me kike ce Saleema? aure Haidar ɗin zai yi? Dalili dame za'a masa auren dole abarsa mana ya auri wacce ya ke so?".

Kuka kawai Saleema take, domin tasan sarai son da take wa Haidar in har bata aure sa ba komi zai iya faruwa da rayuwarta, tunda take bata taɓa son wani ɗa namiji ba sai Haidar, shi ne na farko kuma shi ne na ƙarshe domin ta tabbatar ba zata ƙara samun wanda ya kama ƙafarsa ba ballantana ya kaisa, shi ne bugun zuciyarta shi ne komi na ta shi ta baiwa yardata domin duk macen da ta samu miji kamar Haidar to ta samu rabin jin daɗin duniya.

Hanan kuwa jin zuciyarta take tamkar za ta tarwatse, domin ita a ganinta kaf duniya ma babu wata macen da ta kai ta son Haidar ciki kuwa harda uwar da ta kawosa duniya domin ita gani take ma babu maƙiyyarsa irin mahaifiyarsa, domin ita aganinta da tana sonsa da baza tayi masa auren dole ba.

Ko kula Saleema ba ta yi ba, tayi saurin ɗaukar ƴar ƙaramar handbag ɗinta ta fice daga ɗakin tana tafiya ko kallon gabanta bata yi har tazo inda take son tsayawa wato parking space, ta waiwaya bata ga kowa ba sai wasu fadawan sarki acan daga jikin wata kyakkyawar baranda kewaye da filawa masu matuƙar kyau da ɗaukar ido domin baby ƙarya gidansu Saleema gida ne babba sannan gashi gida na sarauta ga kuɗi.

Ta dannawa Antinta kira, sai da tayi kira har sau biyu sannan ta ɗaga ai kuwa ko gaishe ta batayi ba ta fara faɗa mata maganganu masu zafi akan zuwan da sukayi wajen boka kuma gashi babu abinda zuwan ya haifar.

"Hanan yanzu ni kike faɗawa magana kan wannan yaron?".

"Eh na faɗa ɗin, ƙarya nayi aikin da akayi ya kamasa ne? ai kinga an cuce ni an ƙwacemin ƴan kuɗaɗena".

"Au ke yanzu ba kiji abin da boka ya faɗa bane? Cewa ya yi irinsu asiri bai fiya kama su ba, amma muci gaba da yin abin da za a samu hankalinsa ya karkata kanki, amma saboda ba kida kunya kike faɗar wannan maganar".

"Yanzu dai sai in bari har sai yayi aure, wa ta ta rigani shiga gidan kafin ni na shiga ko? To ta Allah ba taki ba Allah ni zan fara shiga gidan idan ma baƙin ciki kike ki dena".

Ƙit! ta kashe wayarta tama wani irin mugun tsaki, dama ta barta da ta gwada basirarta ta kissa da kisisina har Allah yasa hankalinsa ya karkata agare ta, amma yanzu ma baza ta yi wasa da damar ta ba za ta baje kolin basirarta.

Ta koma cikin gidan ta nuna ita masoyiyar Saleema ce, wajen rarrashinta da nuna mata ai dole ma sai ta auri Haidar domin babu namijin daya dace da aurenta sai Haidar, ƴar sarki jikan sarakai kuma gimbiya..............

$HUMAIRA
$AMIRA
$UMMI
$HAJIYA ƘARAMA
$HAJIYA BABBA
$BABA KANDE
$SALEEMA
$HANAN.

*MISS GREEN CE*
07068606171
CALL NO CHART
[7/1, 11:54 AM] UMMU MAHER (MISS GREEN)🍃: *_💋ƊAN HALAK💋_*

MALLAKAR
*_UMMU MAHER(MISS GREEN)🍃_*

*_AREWA WRITER'S ASSOCIATION📚_*

~*Arewabooks*~
D'AN HALAK:: https://arewabooks.com/book?id=6631fffa0eeb3b80f1ef8159

~*Wattpad*~
D'AN HALAK
https://www.wattpad.com/story/368199708?utm_medium=link&utm_source=android&utm_content=story_info

MAHER'S COLLECTION
https://chat.whatsapp.com/C3tsX4CqiEp939DhYvJ3SZ

*MY CHANNEL LINKS*

DOMIN SAMUN ƊAƊAƊAN LITTAFAINA.
https://whatsapp.com/channel/0029VaEuTqi17En0eYizXq3d

*KEMA HAKA KI KE ZAUNE BA KIDA SANA'A? KO KUWA KINA YI SAMU NE BAKYA YI? KO KUWA KINA CIKIN MATA MASU KIWA?*

TO KU BUƊE KUNNUWAN KU DA KYAU, SANNAN KU SANI SANA'A ITA CE JIGON RAYUWA MUSAMMAN MU MATA, UMMU MAHER TA SHIRYA TSAF WAJEN KOYA MUKU WAƊANSU SANA'O'I KAMAR

*BEAD WORK*🧶👚🧵
*GRAPHICS*✍🏻
*MAGUNGUNA NA MU NA MATA*🍃
*RIBOMS NA YARA DANA MANYA*💇🏻‍♀️💇🏻‍♀️

IDAN KIN SHIRYA KOYON DUKKANIN WAƊAN NAN SANA'O'IN KI YI MIN MAGANA TA NO ƊINA KAMAR HAKA;
07068606171

14

*_HAIDAR_*

Wani irin ciwon kai ne ya turniƙesa, computer ɗin daya ɗauka domin yin aiki ya ajjeta can gefe, ransa amatuƙar jagule yana tunanin abubuwa da dama musamman kan wannan auren da za'a masa wanda bai shiryawa hakan ba, jin jikinsa yake tamkar ba nashi ba. ko da ya rasa yadda zai yi ya ɗauki wayarsa ya kira amininsa Hammud domin ya faɗa masa halin da yake ciki ko Allah zaisa ya samu sassauci.

Bugu ɗaya ya ɗaga yana tsokanarsa da ce wa" a'ah kaga manyan mutane kira ɗaya ninkin kuɗi biyu Allah dai ya.

Bai kulasa ba, daman kuma Hammud yasan ba lallai ne ya magantu ba saboda haka ya ce" kaga malam riƙe son kuɗinka agefe ba wata ƙwangila da zaka samu, wata magana ce na kira ka muyi amma inason ka bani shawarar daya kamata".

ya ɗan ja fasali, sannan ya ce" uhum ina jinka Horror".

baiyi niyyar sakin dariya ba, amma saboda kiran sunansa da yayi ahaka yasa ya ɗan dara sannan ya ce" Ammi ke son yimin auren dole, kuma wallahi ni ban shiryawa hakan ba, sai dai inason ka sani wallahi bana son wannan auren sam domin ni ayanzu haka auren ma ya fice min

azuciya, gwara inyi zamana kawai domin aƙwai mutane da dama da sukayi rayuwarsu ba tare da kowa ba, kuma suka mutu cikin aminci".

sai daya gama maganarsa tsaf, sannan Hammud ya ce" banƙi ta bakinka ba Terro amma gaskiyar magana abinda Ammi tayi shi ne dai dai, haba Haidar shekararka nawa aduniya? ayanzu haka fa kana da kusan shekara 35 aduniya idan baka kai ba to kaɗanne, amma ace baxa ka yiwa kanka faɗa ba? Ammi ta sanya maka ido ne kawai, amma ganin baza kayi abinda ranta yake so ba yasa ta nema maka mafita, sannan kai da kanka kasan rashin lafiyarka aure shi ne maganinta, amma madadin ka samowa kanka mafita da maganin damuwa me ɗorewa sai kuma kayi watsi da hakan? gaskiyar magana kabi umarnin Ammi, amma idan har kace zaka bijire mata ka zauna babu mata gaskiya har abadan ba zaku taɓa shiryawa da Ammi ba".

"Hammud ba wai naƙi ta taku bane, a wannan rayuwar da muke ciki mafi yawanci mata suna aure ne saboda kuɗi, ba wai don suyi aure saboda samun aljannah ba, suna yi ne saboda muradin kansu da kuma wani ɓoyayyan sirri na son shagalin rayuwa, kuma ita kanta matar bakasan wacce iriya ba shin ƴar gidan tarbiyya ce ko akasin haka? shin me son abun duniya ce ko akasin haka? sanin gaibu sai Allah".

"haka ne, amma duk da haka ka sanya yaƙinin zakayi aure ne ba don komi ba sai don son sunnar annabi, sannan kayi domin mahaifiyarka kai yanzu awajenta kake neman aljannah ba wajen matarka ba, saboda haka ka bita sau da ƙafa azauna lafiya".

shiru ya ɗanyi alamar tunani, sannan ya ce" uhum zanyi yadda kace amma Hammud sai na dinga ganin kamar ba Ammi ce ta haifeni ba, domin tunda na taso ko jana ajiki batayi kamar yadda take jan Baby ajikinta, ko ƴan aikin gidanta tana matuƙar ɗaukarsu da muhimmanci fiye dani ma duk da nasan aƙwai wasu abubuwan da suka sanyata haka, ciki kuwa har dani na kasance ɗan fari kasancewarta Bafulatana to dole asamesu da kunya, amma abin yana shafata sosai bayan rashin uba har da rashin uba akusa dani".

Hammud ya gane me yake nufi, amma saboda bayason ya sanya abokinsa cikin damuwa sai ya ce" Ammi tana sonka Haidar, domin babu wata uwa da zata ƙi ɗan ta, saboda wani dalili hakan ma zai faru? tasha wahalar ɗaukar cikinka rani, zafi, inuwa, haka har ka girma ka mallaki hankalinka, to duk idan bata sonka wallahi baza tayi maka su ba, domin idan bakason mutum fita kake daga rayuwarsa amma ita Ammi kullum burinta ta janyo ka ajiki, shawarata gare ka kayi haƙuri komai zai zama dai dai".

ba tare daya ce komi ba ya kashe wayar, kiran Ammi ne ya shigo jikinsa amatuƙar sanyaye ya ɗaga kiran, gamida gaishe ta cike da ladabi sai dai ransa babu daɗi gamida alƙawarin da ta ɗauka na yi masa aure.

"Haidar inaso gobe kaje ku gaisa da Najma, saboda kaga abubuwa suna ƙara ƙaratowa kuma ta sanar dani cewar haryanzu bakaje gidansu ba".

jin taja wa'adin maganar sai ya ɗan ja fasali sannan ya ce" zanje in sha Allah".

daga nan bai ƙara ce wa komi ba, sanin hali yasa ta katse kiran baki ɗaya, zuciyarta duk babu daɗi akan auren da za ta yiwa ɗanta namiji tilo, sai take ganin kamar tayi masa ƙarfa ƙarfa ne ko kuma auren dole, domin sanin kanta ne Haidar mutum ne wanda bai damu da rayuwar mace ba, xata iya rantsewa da Allah tunda take bata taɓa ganin yarinyar da Haidar ya buɗe bakin ƙasaitarsa ya ce yana so ba, sai dai su suce suna sonsa wanda kusan duk macen da tayi katari dashi sai ta ƙyasa.

Ganin tayi shiru yasa Baby ma yin shirun, ta tafi duniyar tunani domin har ga Allah bataji daɗin wannan haɗin ba, domin tasan yasan wacece Najma yarinya ce wadda iyayenta suka lalatata, batasan komi ba sai shashanci da danna waya, chart da game  sai kuma tiktok domin Najma tana ɗaya daga cikin ƴammatan da suke Tiktok, a ɓangaren hausawa kuwa za a iya ce mata don, domin tasan ta kan Tiktok duk inda wasu selebiriti suka kai a tiktok tasan dasu, suma kuma sunsan da ita.

Ammi ta ce" Baby bansan me yasa nayi wannan haɗin ba, saboda harga Allah wannan yarinyar ba kalar Haidar bace, yadda bai da magana da son tashin hankali na haɗasa da Najma, yarinyar da agidansu ta fitinesu idan tana gida hatta karnukan gidan nutsuwa suke, amma inaji ina gani saboda ƙawancan da muke da mahaifiyarta muka haɗa wannan haɗin, addu'ata Allah ubangiji ya basu zaman lafiya me ɗorewa".

"Ammi ni dai nasan za'a samu matsala wallahi, gata da shegen yawo da kuma ƙaryar tsiya duk da ansan mahaifinta yana da kuɗi kuma kowa yasan da hakan amma gaskiya idan kika ga rashin arxiƙin da suke aclub Allah Ammi abin ba daɗi, tamkar ba yaran musulmi ba".

Wata gauruwar ajiyar zuciya Ammi tayi sannan ta ce" to yanxu ya zanyi ne Baby? ai aikin gama ya riga daya gama, addu'ata ɗaya Allah ya daidata kansu ai mutumin banza yana komawa na gari, haka zalika mutumin ƙwarai yana komawa na banza, saboda haka ni na yarda da ƙaddara daman can Najma tana cikin allon ƙaddararsa wanda babu wanda ya isa ya goge hakan".

*******

WASHE GARI.

Shi kaɗai ya fito amotarsa ba tare da kowa ba, yasan gidansu Najma yana nan a Nasarawa G.R.A saboda haka awaje yayi fakin ɗin motarsa ya daɗe yana nazarin yadda zaiyi ya kirata, domin har ga Allah jin tsanarta yake sosai aransa tamkar dai yadda ya tsani ɓatawa mahaifiyarsa, ba don bin umarnin uwa ba da ko ahanya bata isa ya ɗaga kai ya kalle ta ba, saboda sam bata da wani tsarin matar daya yarjewa zuciyarsa wajen neman aurenta, domin

manzonmu annabi Muhammad (S.A.W), ya horemu da mu auri mace don tarbiyyarta da addininta, ba don kuɗi ko kyau ko mulki ba idan ma kuɗi ne shima yana dasu kuma har yafi nasu ma, saboda haka dole ne ya samarwa kansa mafita domin ko ganin murmushinsa baza tayi ba, ballantana ma har ta ce zata faɗa masa wata magana irin tasu ta ƴan duniya ƴan tasha.

daga can nesa ya hangota cikin mota ƙirar corolla, ita da wani yana jan motar sai dariya take har tana wani ƙamesa tamkar da mijinta take hira, kana ganinsa kasan ƙwararran ɗan duniya ne wanda duniya ta gaji dasu a gidan ɗan kande, daga can gefen gidansu ya ajjeta ta fito ya yafito ya da hannunsa yana wani kashe mata idanu tamkar wanda yayi shekara ɗari rabonsa da mace.

haushi da nadamar zuwa suka ishi  Haidar ƙiris ya rage zuciyarsa tsinkewa ya tafi, amma sai ya tuna umarnin da mahaifiyarsa ta basa tuno da hakan yasa ya sauke kansa ƙasa, zuciyarsa sai tsinkewa take tana wani irin luguden dakan masara.

Har ta shige gidansu bata kawo komi aranta ba.

ganin zata shiga gida kuma bata gansa ba yasa ya fito ahankali, cike da takun nan nasa mai matuƙar burge ƴam mata, daga nesa da ita ya tsaya sannan ya kira sunanta acan cikin maƙoshi.

"Najmah".

wani irin magana ɗisu ne ya kamata, tayi saurin juyowa domin tunda take arayuwarta ba'a taɓa kiran sunanta taji daɗin sunan irin na yau ba, ta amsa da sauri.

"Na'am".

Ganin Haidar yasa ta saki wata irin ajiyar zuciya gamida yin wani ƙayataccen murmushin daya gaza ɓoyuwa har sai daya fito fili ya zama kamar dariya".

wani irin baƙin ciki ne ya turniƙesa ganin murmushin da tayi, ya haɗe girar sama da ta ƙasa bai ƙara ce wa komi ba ya ɗan dafa jikin motarsa yana kallon wani waje na daban.

Cike da garaje ta ƙaraso tana yaƙe haƙora, da rashin kamun kai tamkar kurar da taga abin hararta har wani tuntuɓe take tana lilo tamkar zata faɗo kansa.

"sannu da zuwa yaya Haidar, baka faɗamin zaka zo ba ai da ban fita ba".

ya ɗan ja numfashi sannan ya ce" no ba komi".

Tasan halinsa da jin kai, da kamun kai saboda haka yasa ta ce" to mu shiga daga ciki ka gaida Hajiya ko? Dady ma yau zai dawo kaga daya dawo sai ku gaisa".

wani irin kallon ƙasa yayi mata, ta tsargu da kanta saboda haka sai ta ce" to bama sai ka shigo ba ai mun gaisa".

Sam baya son mace me shegen surutu tamkar wata aku, amma babu yadda zaiyi tunda ya ɗakko kanki da motsi........😝😝😝

*na ce ba su Aisha arage surutu saboda zamuje shagalin bikin Haidar da Najma*😝😝😝🤪😂 ni dai ina cikin ƙawayen masu kamun kai😂

Ina masu son shiga adashe Amma kuna fargaba🤔yar uwa ki tsarkake zuciyan ki kizo kiyi adashe cikin aminci da kwanciyan hankali insha Allah Babu rigima ko tashin hankali kwanciyan hankali zaki Yi adashen ki Kuma mu gama lfyh da yardan Allah..🥰🤝

30k weekly parking 300k

1)Haj Maryam✅

2)Ada umar/hafsat yahya✅

3)Usman

4) barrister hauwa'u

5)shafa bello/baby daura

6)

7)

8)

9)

10)

Akama slot

https://chat.whatsapp.com/HAkm8rlNu8a0ouQsRmuDuL

$HAIDAR
$NAJMA
$AMMI
$BABY
$HAMMUD

*MISS GRERN CE*
[7/1, 11:54 AM] UMMU MAHER (MISS GREEN)🍃: *_💋ƊAN HALAK💋_*

MALLAKAR
*UMMU MAHER(MISS GREEN)🍃*

_*AREWA WRITER'S ASSOCIATION📖*_

_AREWABOOK_
https://arewabooks.com/book?id=6631fffa0eeb3b80f1ef8159

_WATTPAD_
https://www.wattpad.com/story/368199708?utm_medium=link&utm_source=android&utm_content=story_info

Ina masu son shiga adashe Amma kuna fargaba🤔yar uwa ki tsarkake zuciyan ki kizo kiyi adashe cikin aminci da kwanciyan hankali insha Allah Babu rigima ko tashin hankali kwanciyan hankali zaki Yi adashen ki Kuma mu gama lfyh da yardan Allah..🥰🤝

30k weekly parking 300k

1)Haj Maryam✅

2)Ada umar/hafsat yahya✅

3)Usman

4) barrister hauwa'u

5)shafa bello/baby daura

6)

7)

8)

9)

10)
Akama slotd

https://chat.whatsapp.com/HAkm8rINu8a0ouQsRmuDuL

17

________Najma kuwa ba ta ma san Haidar yana yi ba, domin kuwa tuni ta tafi tunani wai ga shi ta auri Haidar yana son ta gami da lallashinta. Shi kuwa Haidar ganin irin kallon da take mishi ya sa ya buɗe ƙasaitaccen bakin shi da ƙyar ya ce" kinga tafi gida zan wu " ... Tun kafin ya ƙarasa maganar ta ce"haba ya Haidar ya daga zuwa sai tafi? Please mana ka ƙara tsayawa"?. Ganin za ta ƙara ɓata mishi lokaci yasa ya shiga motar shi ya tayar da ita kawai. Ganin hakan yasa ta yi saurin matsawa, ya yinda shi kuma a nashi gefen ya faɗi a zuci, da mana kar ki matsa in yi ƙwallo dake. Ya figi motar da ƙarfin tsiya tamkar zai ta shi sama, saboda har ga Allah tsanar Najma yake ji har cikin ƙwaƙwalwar shi. Kai tsaye kuma yaga kiran Ammi ya ɗaga.

"Zaki, idan ka gama abin da kake kazo ina son ganin ka".

Da "to" ya amsa sannan ya cigaba da tuƙin shi cikin wani irin yanayi na mai jin kewa da kuma tunanin ƙuncin da zuciyar shi za ta kasance in har ya auri Najma, saboda tsabar tsanar da ya yi mata har kuma ga Allah yana so ya samu macen da yake sonta take son shi ba ihun ka a banza ba, ma'ana wanda kai kaɗai kake kiɗanka tare da rawar.

Kai tsaye ya juya hancin motar shi hanyar Road ɗin su Ammi, duk da wajen aminin shi Hammud yaso yaje amma sawun giwa ya taka na raƙumi, haka ya dinga saƙe-saƙe da kwance-kwance har ya isa katafaren gidan na su, wanda faɗin irin haɗuwar da ya yi ma ɓata baki ne.

Tana hango shi ta yi saurin fitowa daga ɓangarensu, dama kuma unguwa za taje bata san irin ƙaunar da take wa Haidar ba, sai dai sam shi bai ma san tana yi ba ma'ana ihunka a banza, sannan tasan ko dama tana son shi to tabbas Hajiyarsu da mahaifiyar Haidar ɗin ba za su yarda ba, saboda takun saƙar dake tsakaninsu sannan uwa uba bata girmama Ammi yadda suka taso suka ga Hajiyar su na yi mata haka ita ma take yi.

"Tasleem!".

Ta ji an faɗi sunan ta, ba ta amsa ba kuma ba ta juyo ba ta ji Nasreen ta cigaba da magana.

"Lulu wai me ki ke nufi ne da Haidar? A duk lokacin da kika gan shi sai naga kina ta kallon shi tamkar za ki haɗiye shi, anya kuwa kina tuna shi ɗin waye a wajen mu? Shi ɗin ɗan babbar maƙiyiyarmu ne, idan ma kin manta ya kamata ki tuna waye ɗin".

Da sauri ta juyo ta maida mata da martani "ok! saboda haka sai akace kada na so shi ko? To bari kiji in har kika ga ban auri Ya Haidar ba sai dai idan bana numfashi ko kuma shi, amma duk abin da iyayanmu za suyi bai dame ni ba".

Nasreen da mamaki ta ƙara buɗe baki za ta yi magana, amma Lulu ta yi caraf wajen ce wa "da kin adana bayanan ki zai fi miki alkhairi, domin kuwa ni dai ba za su yi min amfani ba kin gane"?.

Tana faɗar hakan ta bar wajen tana mai shiga sabuwar motar ta wacce Dadinsu Alhaji Marshal ya kawo musu ita da Hajiyar su,  sosai take gudu akan titi tana sauri domin zuwa wani party ɗin aminiyarta, wanda ta haɗa haka kawai na jin daɗi da sangarta irin ta ƴaƴan masu hannu da shuni.

*¢¢¢¢¢¢¢¢*

_HUMAIRA_

Baba ya kalle ni sannan ya ce" na ce daina kallo na ko? Yarinya sai kace mayya? Shegiyar yarinya mai mugun hali, ina zaman zamana aka kira ni wai naje ofishin ƴan sanda, kun jajiɓo min abin kunya kai tir da halinku wallahi dama ku sani na barku ku zauna a gidan nan, amma saboda mutuncin wannan baiwar Allahn, da kuma kuɗin da ta bani domin dubu hamsin ɗin nan za ta ishe ni in ciyar da bataliyarku har na tsawon wata".

Da sauri Ameera ta ce"Baba bafa kai aka bawa wannan kuɗin ba, mu fa ta ce a bawa amma kuma na ji kana cewa wai za ka yi amfani da kuɗin, kuma wallahi ba mu za ka yiwa amfani da su ba waccan muguwar za ka..."

Wata irin ashar ya mulmula ya miƙawa mata sannan ya ce" to bazan baku ɗin ba don ubanki, ƴar iska ƴar gadon talauci da tsiya to don uwarki idan ban baku kuɗin ba ki kai inda kika fito wajen ƴan sanda, tunda kunga yadda wajen yake kisa nima a kai ni mara kunya, mara tarbiyya idan har baki yi ba ai sai Allah ya tambayeki ai kin sha a nono dole ki yi abin da ki ke so".

Baba Kande ta yi caraf ta karɓe ta ce" ni fa Allah sai naga wannan yarinyar tamkar idan aka bata wuƙa aka ce ta kashe ni da gudu za ta soka min, domin naga duk ta fisu ma rashin mutunci yadda kasan ƴar tasha haka take, Allah Malam kamata ya yi ka yafewa duniya waɗannan yaran, domin kuwa basa tsinana maka komi sai janyo maka rigima da rashin kunya".

Ummi ta ce" to sai me idan ya yafewa duniya mu? Wata uwar yake ma..."

Bugu na kaiwa Ummi a bakinta na ce"haba me yasa ba kida kunya wai? To idan ma kin manta ki tuna waye a gabanki mahaifinmu ne a gabanki saboda haka ki kiyaye bakin ki, sannan kuma ku durƙusa ku bashi haƙuri tunda ba ku da kirki".

"Ai da kin barsu su rufe ni da duka, ai har ke ɗin duk kanwar ja ce ina marin uwarki na zo yi ki ka riƙe mun hannu, saboda zan daki ƴar gwal to tunda haka ne ku tafi can gidansu uwarku ku zauna, sannan kada ku sake ku zo min gida na yafewa duniya ku kamar yadda Kande ta ce, haba ina dalili yara sai kace ƴaƴan Allah ba ni"?.

Yana faɗar hakan ya tashi ya shiga ɗakinmu yana cillo mana da kayanmu yana watso kayan yana zagin gami da mita tamkar mita uwar gami. Ni kuwa sai kuka nake mai cike da abin tausayi domin duk wanda ya saurari kukana yasan tabbas ina cikin matsala. Su Ameera kuwa ko gezau babu sai kallon shi suke suna hararashi, sam basu san ma wani abu ɓacin rai ba a wannan lokacin.

Muna ji da gani haka ya tisa ƙeyarmu zuwa ƙofar gida, baki ɗaya hankalina a tashe yake domin nasan Umma ba za taji dadɗin abin da ya faru ba, ga baƙin cikin sanya mu a bayan sel da aka yi

tamkar waɗanda suka yi fashi, duk a silar rashin gata domin idan ace muna da gata duk hakan ba za ta kasance ba.

Ummi ta ce" wai miye ki ke kuka ne? Ni wallahi wannan abin da Baba ya yi naji daɗin shi, ko ba komi yanzu mun ƙara gane waye shi sannan kuma anan gaba ba zai ji daɗinmu ko son ya raɓemu ba sanadiyyar mun yi arziki, a wannan lokacin ne zamu wulaƙanta shi son ranmu".

Ameera ma ta ɗora "uhum! Ai ni abin Baba yanzu ya daina damuna, abu ɗaya nake tunani Umma jin hakan zai ƙara sanyata cikin wani hali, duk ta saba da ire-iren waɗan nan abubuwan idan da sabo ta saba da cin mutuncin shi".

Ni dai bance musu komi ba, takaici ne fal zuciyata fatana dai ɗaya ne Allah ubangiji yasa Umma ta sanyaya zuciyarta akan lamarin.

****

_UMMA_

Abinci ne a gabanta, ga jariranta suna ta kuka ita ma kuma kukan take yi domin kuwa ita kaɗai tasan ɗacin da take ji a zuciyarta saboda duk matar da aka jarabce ta da rashin samun miji nagari ta haɗu da babban ƙalubale na rayuwa.

"Haba yaya? Kin tsaya ke baki ci abincin ba ke baki tashi mun je inda zamu ba? Mu gano yaran nan a halin da suke ciki, tunda tun shekaran jiya dana je ban samu naje jiya ba sannan ke kin kasa zuwa, sai yau Allah ya yi za kije sannan yau ɗin ma kina shirin ƙin zuwa".  Cewar Anty Salamatu ƙanwa ga Ummansu Humairah.

"Salamatu wallahi bana son zuwa na gano halin da yaran nan suke ciki, idan naje nima sai naji dama su haɗa dani su kulle domin kuwa babu uwar da za taga yaranta a irin wannan halin ta jj daɗi, duk yadda za tayi dole taji tana son fitar dasu, sai dai kash! kinsan ba ni da halin yin hakan haƙuri da addu'ah shi suke buƙata".

"Eh duk da hakan dai ki tashi mu tafi, saboda shi kanshi ganin ki ɗin da za suyi zai sa su samu sauƙi da sassaucin halin da suke ciki".

Yayansu Umma ya shigo ya tarar dasu a cikin wannan hali ya ce" Fatima har yanzu wannan damuwar ba za ki daina ta ba? Yanzu haka ma daga can nake, sai akace wai an bada belin su sun tafi gida to shi ne naje gidan na su aka ce wai sun taho nan to kuma ban gansu anan ɗin

ba?.

Da sauri Umma ta tashi, gabanta ya tsaya cak da faɗuwa ta ce" Allah na gode Allah abin godiya, duk inda suke nasan yanzu za ka gans......"

"Amma wai Babansu ya ce su dawo nan gidan da zama".

da sauri Umma ta ce" su dawo nan gidan da zama kuma? Me kuma suka yi mishi?".

"To bai dai faɗa ba, amma gaskiyar magana Amadu bai da kirki ko kaɗan wallahi, ace yara mata ka barsu ba arabi ba boko? Sannan tsabar rashin arziƙi kace su koma gidan iyayen matarka da zama"?.

Ita dai Anty Salamatu kasa magana ta yi saboda tsabar takaicin abin da ya faru, domin ita al'amarin na shi ya daina bata mamaki domin duk abin da akace ya yi za ta yarda, biyo bayan cin mutumcin da ya yi mata ita da yayarta wacce ya saka da ɗanyan jego, wannan rashin imanin har ina?.

Suna cikin maganar muka shigo, da gudu muka yi kan Umma muka rungume ta muna kuka me ciwo.

*IFKAM FAMILY*

---

Babban hall ne mr ɗaukar kusan mutane ɗari biyar, kowa yana zaune cikin shigarsa ta alfarma wajen mata daban wajen maza ma daban, wani kyakkyawan mutum na hango kan wata kujerar alfarma, yana sanye da shiga ita ma ta alfarma wacce kana ganinta kasan ta ƙasaitattun mutane ce, ya fara magana kamar haka.

*KEMA HAKA KI KE ZAUNE BA KIDA SANA'A? KO KUWA KINA YI SAMU NE BAKYA YI? KO KUWA KINA CIKIN MATA MASU ƘIWA?*

TO KU BUƊE KUNNUWAN KU DA KYAU, SANNAN KU SANI SANA'A ITA CE JIGON RAYUWA MUSAMMAN MU MATA, UMMU MAHER TA SHIRYA TSAF WAJEN KOYA MUKU WAƊANSU SANA'O'I KAMAR

*BEAD WORK*🧶👚🧵
*GRAPHICS*✍🏻
*MAGUNGUNA NA MU NA MATA*🍃
*RIBOMS NA YARA DANA MANYA*💇🏻‍♀️💇🏻‍♀️

IDAN KIN SHIRYA KOYON DUKKANIN WAƊAN NAN SANA'O'IN KI YI MIN MAGANA TA NO ƊINA KAMAR HAKA;
07068606171

*$HAIDAR*
*$HUMAIRAH*
*$AMEERA*
*$UMMI*

MISS GREEN CE
SHARE
COMMENTS📲👏
07068606171
CHART NO CALL
[7/1, 11:54 AM] UMMU MAHER (MISS GREEN)🍃: Follow the 💌UMMU MAHER(MRS GREEN)FANS💌 channel on WhatsApp: https://whatsapp.com/channel/0029VaEuTqi17En0eYizXq3d

*_💋ƊAN HALAK💋_*

MALLAKAR
*UMMU MAHER(MISS GREEN)🍃*

_*AREWA WRITER'S ASSOCIATION📖*_

_AREWABOOK_
https://arewabooks.com/book?id=6631fffa0eeb3b80f1ef8159

_WATTPAD_
https://www.wattpad.com/story/368199708?utm_medium=link&utm_source=android&utm_content=story_info

Ina masu son shiga adashe Amma kuna fargaba🤔yar uwa ki tsarkake zuciyan ki kizo kiyi adashe cikin aminci da kwanciyan hankali insha Allah Babu rigima ko tashin hankali kwanciyan hankali zaki Yi adashen ki Kuma mu gama lfyh da yardan Allah..🥰🤝

30k weekly parking 300k

1)Haj Maryam✅

2)Ada umar/hafsat yahya✅

3)Usman

4) barrister hauwa'u

5)shafa bello/baby daura

6)

7)

8)

9)

10)
Akama slotd

https://chat.whatsapp.com/HAkm8rINu8a0ouQsRmuDuL

18

________"Ni Ifkam na bada shawarar haɗa yaranmu aure, musamman da ayanxu muke da ƴammata kusan goma a gidan nan sannan ga samari ma saboda haka a madadin bakin mai martaba na yanke wannan hukunci, duk kuma wata ko wani da zai zo daga baya ya ce hukunci bai masa ba, to ya kuka da kanshi domin hukunci Sarki shi ne dai-dai sannan ko kusa ba muyi hakan domin zalunci ba, ilahu yasan manufarmu ta yin hakan".

Kallon-kallo aka shiga yi a wannan babban ɗakin, nan da nan fuskokin wasu suka juye zuwa baƙin ciki, wasunsu kuma akasin hakan domin har yau har gobe wasu suna ɗaukar hukunci sarki abu mai yiyuwa, sannan duk abin zancen da zai fito daga bakin Waziri Ifkam sun san tabbas wannan ba ƙaramin abu bane wanda zai sa suyi fatali da shi, domin a wannan masarautar ana matuƙar girmama maganar shi, duk da shi dama Waxiri Ifkam ya kasance ɗan uwa kuma kaka a cikin wannan babbar masarauta, kuma a yanzu ɗan ɗan uwanshi ne yake wannan sarauta, kuma shi da kanshi Ifkam ɗin yana matuƙar girmama al'amuran wannan babbar masarauta.

Ganin kamar a wannan karon kowa ya yi shiru baka jin ambaton Alhamdulillah ya Allah, yasa ya ƙara motsi sannan ya gyara zaman shi akan kilishi wanda ya kasance tamkar doki wajen yake, domin an zana hoton doki sak da daƙwa daƙwan gwala-gwalai sai sheƙi yake sannan aka ɗora kilishi akai, sai abun ya bada wani irin mugun haɗi amma ba ana nufin haɗin gambiza ba.

"Kamar yadda na faɗa babu wata ko wani da zai ce wannan hukunci bai yi ba, sannan kuma wannan aure bama so ya wuce wannan watan da muke ciki, babu ruwanmu da wani biki ko kaɗe-kaɗe hakan nan za a yi wannan biki cikin salama, domin idan mun tuna da shekarun baya muna duk al'adunmu na wannan babbar ƙasa wajen yin shagalin biki, amma yanzu dole ne a tsayar da komi domin ganin abin da ya faru a baya wanda ya zana babban allon da har yanzu bai goge a cikin allon zuciyoyinmu ba, wanda nima shaida ne kuma shaida ne saboda a yanzu zan faɗi wannan haɗi da ya kasance".

SHAHID WA ZEINEB

ƘASIM WA JAWAHIR

LUKUMAN WA ZEHRATU

RABIAAT WA TANIM

FARUK WA BILQISS

ASSADIK WA MINAT

HILAL WA BINTU

SAGIRR WA ESHAT

BILAL WA KUBRAT

NURRR WA NURATU

Ai kafin ya gama rufe baki wajen ya fara kaurewa da surutu mai ƙarfi har aka fara jiyo muryoyin wasu suna yiwa juna ƴan gore gore da habaici, wasunsu kuma har da kuka wiwi tamkar dai iyayensu sun mutu ne, ganin hakan yasa Ifkam ƙare musu kallo sosai yana nazarinsu da kalamansu, masu yin kuka ma ba a barshi a baya ba kallon idanuwansu yake ganin hango tsagwaron baƙin ciki tamkar dai zasu balbalawa wajen wuta, mutane biyu ne yaga suna farin ciki da wannan aure amma in ka cire su biyun nan sauran duk cikon aji ne, ma'ana duk ƴan daɗawa wuta fetur ne wasu kuma rabon faɗa suke amma sai su ɓuge da shigarwa wani ɗan uwansu mafi kusa.

Ifkam bai hanasu ba har suka yi suka gaji sannan ya ce"kowa ya tashi ya tafi mun sallame shi, idan da akwai abin da kuke so ku yi da kuɗi kowa ya yi magana za a bashi ba a cire mutum ɗaya ba, domin gudanar da hidima".

Ya nuna musu sam baisan abin da suka yi yanzu a gabanshi ba, sai jikinsu ya yi mugun yin sanyi domin har yau hat gobe basu manta waye Ifkam ba, in har ya zartar da hukunci ko akan waye sai anyi ko da kuwa ɗan cikinsa ne.

sosai wannan babbar masarautar ta yamutse, kowa cin karanshi ba babbaka yake kullum a cikin tashin hankali tun bayan da Ifkam ya zartar da wannan ɗanyen hukuncin, domin a ganinsu ai wannan ɗanyen aiki ne idan ba haka ba abar yaransu su zaɓa mana, amma sai ace za a y musu dole saboda an tsane su?.

Ɗakin cike yake da ƴan taro, Omer sai zagaye ɗakin yake yana hawaye mai sosai zuciya, ganin wannan hawayen ya ƙara sanya jikin kowa yin sanyi ya murza idonsa wanda yake yi masa matuƙar nauyi ya ce" tabbas a yau muna cikin alhini, tabbas Ifkam ya rusa mana dukkanin abin da muka rufe, domin yana ganin shi ne babba kuma shi ɗin ba wanda zamu iya taɓawa bane wallahi tallahi ba don shi bane da wani ne da sai inda ƙarfin takubban mu suka ƙare, tsabar tozarta wai kamar Ƴata Nurata wai ita ce za a haɗata da Nurrr yaron da har yanzu bai daina shirme da shiririta, kullum cikin yawon ƙasa-ƙasa yake yana neman ƴar iskar da zai shaƙata da ita, saboda shi ba a yo shi da mutunci ba sannan mu nan duk bai ɗaukemu da mutunci ba, hatta shi sarkin ba wai yana ganin mutunci shi bane amma shi ne za a jajibo shi a haɗa shi da ƴata"?.

Abu Nurrr ya yi saurin ce wa "kai Omer ka iya bakinki, akan mi za ka dinga zagin ɗana? Yaron da ko a yanzu bai haura shekara 30 ba shi ne ake yiwa irin wannan zagin ɗibar albarkar?

Domin kawai son kai, ita ɗiyar ta ka wani irin iskanci ne ba ta yi? Ko an faɗa maka bamu sani ba ne? To har da boka tunfafiya tana lalatar ta dashi, wanda ya kasance ƙazami kuma faƙiri sai ni za a dinga zaginmu saboda bamu kai ka kuɗi ba, to idan ma domin kuɗi ne ai har yanzu baka kai shi Sarkin ba duk da ana haɗawa dana sat..."

Wata irin shaƙa Omer ya kaiwa Abu Nurrr sannan wajen ya kaure da bala'i, mai makon abarsu suyi faɗansu faɗan mutun biyu sai ya zama faɗan mutane sa yawa waje ya hau sowa, abin ka da ɗakunan gidan sarauta manya-manya sai ga shi an jiyo faɗansu tun a babban masarauta idan ka kasa kunne za ka ji.

babu shiri aka buga busar giwa, nan da nan suka ja munafukan bakunansu suka yi shiru domin sun tabbatar suka bari aka ƙara buga wannan sarewar to fa kashinsu ya bushe, duk da haka basu daina aikawa juna mugayen kallo ba saboda Ƙabilar Turam akwaisu da taurin kan tsiya yadda kasan mutanen farko, ga su da mugun yawa domin iya su gidan masarauta za a haɗa gari biyar awaje ɗaya kuma ba ƙaramin gari ba a a babban gari wanda yake ji da tumbatsar mutane.

ƘASAR NIM

Babbar ƙasa ce mai tafe da mutane da dama, sannan idan ka gansu saboda kyau sai ka ɗauka su ne da kansu suka ƙera kyawunsu ba manya ba yara, gasu da kyawun halitta yadda kasan larabawa haka suke sai dai har sun fisu ma fari da haske su ɗin mutane ne masu yare da al'adu da dama, suna wani yare wanda ake kira YIMAN yaren kamar larabci yake amma ba larabci bane, sannan suna yin yare da dama a garin har yaren da baka tunanin ji ba sai ka ji shi a ƙasar, kusan mutanen duniya da dama suna zuwa ƙasar domin yawan buɗe idanuwa domin Allah ya yi musu kyawun gine gine, kyawun furanni,shuke-shuke albarkatun gona. Sannan suna da dukiya sosai ba kaɗan ba idan nace ba kaɗan ba ina nufin sosai ɗin nan. Ta yadda ko da za suyi shekara malala gashin tunkiya suna raba kuɗa ɗe ba zasu ƙare ba, domin kullum arziƙinsu gaba yaje ba baya ba saboda Allah ya sani suna cinikayya da haɗakar dukiyoyi da ƙasashen africa dama na yamman duka, shi yasa sam ko asara idan ta hau su basa damuwa domin suna da bila adadin ɗinsu a bayan ƙasa.

Wannan rigimar da aka fara sarki yasa aka buga ƙahon giwa ya yi ne saboda kawo ƙarshen tarzoma, domin shi da kanshi ba magana zai yi musu ba saboda sam ba ya son surutu ko hayaniya a tsakanin mutanen shi, ya fi son ya yi musu shiru yaga iya gudun ruwansu saboda sai suyi fin wata ma ba tare da sun sanya idanuwansu akan sarki ba, suna gida ɗaya mai sassa daban-daban kuma duniya daban tunda kowa ba ya ganin kowa tsakanin inda suke, da inda sarki yake a ƙalla ana samun tafiya mai nisan gaske wacce idan a ƙafa za kaje sai ka yi tafiyar awa ɗaya.

*HMM KA DA KUGA LABARI YA JUYA, TI BAI JUYA BA YANA NAN DAI AKAN ƊAN HALAK ƊIN SHI KU DAI KU CIGABA DA BIYO NI*

_HUMAIRAH_

Babu mutanen da ba a aikawa Babanmu ba, akan mu koma gidan shi ya yi haƙuri, amma ya murzawa udanuwanshi kwalli ya ce sam ba zamu koma mishi ba, idan munga dama mu shiga duniya ma amma shi ba shi ne ya haifemu ba, tunda mu ba zamu zauna lafiya ba.

Wannan maganar da ya yi ta ƙara tunzura zuciyoyinmu, musamman ma su Ameera Umma ma taji haushin furucin sosai.

Muna zaune a tafkeken tsakar gidansu Umma, ni Ummi, Ameera, Anti Salamatu, Matan gidansu. Duk hira ake akan Iyan Salame wato mahaifiyarsu Umma wacce take ƙasar larabawa shekaru goma kenen amma har yanzu ba ta dawo ba taje aiki. A nan ne ma ake ƙara tattaunawa kan matsalarmu, Anisa ce ta shigo tana kuka wato ƙaramar ƙanwarmu, idanuwanta sun yi jawur ga ƙafafunta babu takalmi, raina ya yi mugun ɓaci idanuwana suka kawo ruwa domin duka-duka shekarar Anisa uku, amma mahaifinmu ya yi tsallen baɗake ya ce ba za a ɗaukar mishi ƴa ba, domin kada mu koya mata mugun hali irin na mu da uwar mu. Ni daman nasan za a rina wai an saci zanin mahaukaciya domin ni nasan Baba ba zai iya kula da ƙannen mu ba balle kuma Anisa da take yarinya ƙarama, ga hantarar Baba kande da dukan da take musu.

Da gudu ta rungume ni tana ce wa"Yaya unwa ina ji, cicina ciwo ake mini".

Sosai na fara hawaye na ce"Sannu baby Anisa zo ki ci abinci". Na ɗakko sauran gadin kwakin da muka sha na fara ba ta tana ci, hannu baka hannu ƙwarya tamkar dai za ta haɗa da ƙwanon saboda gunwa. Kowa ya dinga kallon yarinyar cike da tausayi, tana gamawa na ɗebo mata ruwa tasha na ɗora ta akan cinyata ina shafa kwantaccen gashinta mai kyau da sulɓi, dama ga Anisa da son jiki sai ta ƙara shigewa jikina na fara tambayarta? "Baby Ani tun yaushe rabon ki da abinci"?.

"Yaya tun da chafe da Baba kande a bamu ɗumamen tuwo".

Da sauri Ameera ta ce" tun da safe Ani? Yanzu fa la'asar ake kira? Inna lillahi wa inna ilaihi raji'un".
Muka saki kuka, amma banda Umma domin tabbas abin ya girgizata shi yasa ma ta kasa magana saboda baƙin ciki.

muna zaune matan gida suna ta zagin Babanmu da matarshi da ta gama mallake shi, sai kuma wani tashin hankalin ya riskemu domin kuwa Anisa ce ta fara wani irin amai tamkar za ta amayar da kayan cikinta, ga bakinta sai kumfa yake...

*KEMA HAKA KI KE ZAUNE BA KIDA SANA'A? KO KUWA KINA YI SAMU NE BAKYA YI? KO KUWA KINA CIKIN MATA MASU ƘIWA?*

TO KU BUƊE KUNNUWAN KU DA KYAU, SANNAN KU SANI SANA'A ITA CE JIGON RAYUWA MUSAMMAN MU MATA, UMMU MAHER TA SHIRYA TSAF WAJEN KOYA MUKU WAƊANSU SANA'O'I KAMAR

*BEAD WORK*🧶👚🧵
*GRAPHICS*✍🏻
*MAGUNGUNA NA MU NA MATA*🍃
*RIBOMS NA YARA DANA MANYA*💇🏻‍♀️💇🏻‍♀️

IDAN KIN SHIRYA KOYON DUKKANIN WAƊAN NAN SANA'O'IN KI YI MIN MAGANA TA NO ƊINA KAMAR HAKA;
07068606171

*$IFKAM*
*$HUMAIRA*
*$AMEERA*
*$UMMA*

*SHARE*
*COMMENTS MY FANS*
*CHART NO CALL 07068606171*
[7/1, 11:54 AM] UMMU MAHER (MISS GREEN)🍃:
https://chat.whatsapp.com/CMIWt3cUVvkDAXPthThNQx

*_💋ƊAN HALAK💋_*

MALLAKAR
*UMMU MAHER(MISS GREEN)🍃*

_*AREWA WRITER'S ASSOCIATION📖*_

_AREWABOOK_
https://arewabooks.com/book?id=6631fffa0eeb3b80f1ef8159

_WATTPAD_
https://www.wattpad.com/story/368199708?utm_medium=link&utm_source=android&utm_content=story_info

Ina masu son shiga adashe Amma kuna fargaba🤔yar uwa ki tsarkake zuciyan ki kizo kiyi adashe cikin aminci da kwanciyan hankali insha Allah Babu rigima ko tashin hankali kwanciyan hankali zaki Yi adashen ki Kuma mu gama lfyh da yardan Allah..🥰🤝

30k weekly parking 300k

1)Haj Maryam✅

2)Ada umar/hafsat yahya✅

3)Usman

4) barrister hauwa'u

5)shafa bello/baby daura

6)

7)

8)

9)

10)
Akama slotd

https://chat.whatsapp.com/HAkm8rINu8a0ouQsRmuDuL

19

________Hankalinmu ya yi ƙololuwar tashi, tun ma ba kamar ni ba domin kuwa kowa yasan yadda nake son Anisa tamkar ƴar dana haifa a cikina. Umma sai kuka take tana kiran sunan Anisa amma tamkar dai an shuka dusa saboda ko motsi ba ta yi, cike da tashin hankali muka yi waje neman ɗan sahu muka yi sa'a wani ya kawo wasu maƙotanmu, da gudu muka sanyata a ciki Umma ma ta shigo muka wuce asibiti, sosai muke kuka Umma ce ma me ƙarfin halin tofa mata addu'ah tana shafa kanta tana ɗan siririn hawaye mai tafe da abubuwa da yawa.

Ƙaddara da tsautsayi tamkar abu ɗaya ne a fassare sai dai a baki harufan suna da banbanci, domin ita dai ta tabbatar ƙaddara ce ta sanyata afkawa kogin maganaɗisun auren mahaifin yaranta, domin ko kusa ba ta ma sanya shi a sahun manemanta ba, saboda ba shi take so ba amma da ƙaddara ta zaɓa mata shi tasan tabbas da babu yadda za a yi ta zaɓe shi a matsayin mijinta, domin ko a lokacin da ta aure shi kowa tofa albarkacin bakin shi ya dinga yi, musamman ma masu cewa wai ita matar manya ce duk da ba shi da mugun hali kamar yanzu, tunda ada can baya in har ta ce yana mata wani abu tabbas ta yi mishi ƙarya, zuwan Baba Kande ne ya canja komi rayuwar su ta zamo tamkar rayuwar ƴan bariki, sannan baya shakkar dukanta a gaban yaransa duk domin matar shi.

*WACECE BABA KANDE?*

Baba kande dai ƴar asalin garin Jos ce, sannan babu wanda bai san mecece sana'ar ta ba ƴar bariki ce me siyar da taba da wiwi, aƙalla aurenta ya kai shida tun ana ƙirga mata aka daina saboda aurenta na biyu ne ma ta kai shekara ɗaya amma duka aurenta ba ta kai ko cikakkun wata biyu take tafiya, kuma duka babu wanda ta taɓa haihuwa dashi domin a cewarta ba ta zo duniya domin haihuwa ba ta zo ne domin hutawa. Saboda haka Allah ya ɗora mata son mahaifinsu Humairah tun wani zuwa da ya yi Jos, ta liƙe mishi tun yana guje mata har Allah yasa ya faɗa komanta, tunda ta asirce shi baki ɗaya ya zama bawanta babu abin da yake haɗa shi da yaran shi sai zagi da hantara. Bayan ya aure ta shi kenan bata ƙara fitowa ba da zummar bazawara, har yau da take da kusan shekara 5 a gidan shi.

Mu koma labarinmu.

Sosai take shan jiki, domin ko kafin mu zo asibitin ba ta numfashi ko kaɗan hankalinmu ya ƙara tashi sosai, da ƙyar likitoci suka amsheta domin sun ce tana cikin koma sosai, wato tana cikin matsanancin hali muna ji muna gani aka shigar da ita emergency(ɗakin gaggawa).

Muka tsaya a reception muna kuka har Umma ta gaji da kukan mu ta ce" wai shin bawa yana iya canja ƙaddarar shi ne? Shin idan Allah ya so ɗaukar rayuwar ta za ku hana ne? Bakwa mata addu'ah sai kuka? Haba ku dinga yawan kiran 'LA ILAHA ILLA ANTA SUBHANAKA INNI KUNTU MINAZZALIMIN, yawan kiran wannan addu'ar yana cire dukkanin bawa musulmi acikin wani hali, saboda haka kuyi ta kiran wannan addu'ar komi tsanani akwai sauƙi da yardar Allah".

Tuni bakunanmu suka fara wannan addu'ar, muna cikin wannan halin ne wani dr ya fito kai tsaye ya yo inda muke, jikinmu duk a sanyaye sai da ya fara kallonmu a nutse sannan ya ce" ku ne ƴan uwan yarinyar nan ko? Da sauri muka amsa, ya cigaba da magana "muna so ku sanya hannu da gaggawa za a mata tiyata ne domin fitar da gubar da ta sha a cikinta, sannan za ku biya kuɗin tiyatar naira dubu ɗari".

Salati muka sanya mu dukanmu, tashin hankalinmu a fili muka fara kuka a wannan lokacin har da Umma a masu kukan, likitan ya ce" ba kuka za ku yi ba ku nutsu kuyi abin da na ce idan ba haka ba zaku iya rasa ta baki ɗaya".

Ni ce na fara magana ina kuka" likita ayi mata aikin duk inda kuɗi yake zamu nemo shi don Allah ayi mata". Na saki kuka mai ƙarfi, gami da haɗe hannayena waje guda alamar ya taimaka su yi mata.

Ganin hakan ya ce" A a, bama aiki sai an fara biya kuyi haƙuri dai ku bubbuga ku kawo mu samu mu ceto rayuwarta".  Da sauri Ameerah ta ce" likita wallahi ko kaɗan bamu da wannan kuɗaɗen ko kusa, ko dubu biyar bamu da ita balle dubu ɗari ni na tabbatar akan kuɗin nan sai dai yarinyar nan ta mutu".

A kiɗime ya kalle ta sannan ya ce" shin ba ku da mahaifi ne? A iya sanina mahaifi shi ne jagaba akan dukkanin lalurorin iyalin shi, saboda haka ku kira shi ku faɗa mishi".

Babu musu na danna lambar wayarshi a wayar Umma, wacce Anty Salamatu ta bata domin ta dinga jinta tunda ita ta koma gidanta yanzu.

Bugu ɗaya ya ɗaga, da sauri na gaishe shi. Na faɗa mishi duk halin da muke ciki.

Saurin kashe wayar na yi, domin kuwa iya tashin hankali ina cikin shi domin maganar da ya faɗa min ba wacce ya kamata kowa ya jita bane domin girmanta ya girmama har ya gagari dutsen dala, ɗaukar maganar sai an naɗa gammo ɗari ba tare da an iya ɗauka ba.

_HAIDAR_

Kallon Mimi ya yi yana ce wa" ki fita a idona fa? Ni ba sa an wasan ki bane akan mi za ki dinga ce min ango?".

Mimi ta ƙunshe dariyarta tana ce wa"Sorry ya Haidar". Bai ƙara tanka mata ba ya zauna jiran Ammi da Alhaji.

A hankali suka fara saukowa a tare, Haidar yaji wani irin abu me masifar zafi ya sauko mishi a cikin zuciyar shi, tunda ya taso Allah bai taɓa ɗora mishi son wannan bawan Allahn ba, domin kuwa shi kaɗai ya barwa kanshi sanin abin da yasa ya tsane shi har haka, sam bai iya tsana ba idan ya so abu a farko abu mai wahala ne ya ƙi shi, idan kuma ya ƙi abu a farko to a ƙarshe ma yana matuƙar wahala ya so shi, ya kasa gane wacce kalar tsana ma yake yi wa wannan bawan Allahn, shi dai yasan tabbas tsana ce wacce har ka mutu kana yiwa mai shi.

Alhaji da fara'ar shi ya ce" A a Haidar ango, sannunka da zuwa".

Ya faɗi hakan da maɗaukakiyar fara'a. Haidar ya ɗan kawar da kai tamkar dai ba zai mishi magana ba, sai kuma ya tuna da alƙawarin da ya yiwa Ammi na gaida mijinta a duk lokacin da suka haɗu.

A ɗan basarwa ya ce"sannu da fitowa". Ammi ta yi saurin kallon shi alamar wannan gaisuwar da ya yi ba ta yi mata ba, yasan sarai dama ba za ta so gaisuwar ba amma saboda son tabbatar mata har yanzu fa wannan tsanar tana nan a cikin ran shi.

Alhaji ya amsa yana fara'a ya ce" Haidar ɗazu mun yi magana da Amminka akan gidan da za ka zauna, to ga mukullin sabon gidana mr part huɗu wanda na kammalashi kwanan nan, kuma ya kasance mallakin ka har abada domin da sunan ka aka gina shi".

Haidar haushi ya kama shi, tamkar dai zai saki kuka saki kuka domin shi dai ko kaɗan ya tsani shisshigin da wannan bawan Allahn yake mishi, ce mishi ya yi bai da kuɗin da zai sai gida ko mi? A iya sanin shi ya mallaki gidajen da ƙirga su ma tamkar ɓata baki ne saboda zunzurutun yawansu, cikinsu kuwa har da waɗanda shi da kanshi alhajin bai isa ya gina su ba.

bai gama tunanin ba yaji Alhaji yana ce wa" sannan na ware maka kuɗi kimanin naira biliyon biyar, domin ka yi hidimar biki sannan na ɗauki nauyin yi maka laife yanzu haka ma na bawa ƙanwata tana can dubai".

Cike da matsanancin haushin abin da ya yi mishi ya ce" na gode".

Daga haka bai ƙara magana ba, ya tashi gami da sanya hannuwan shi duka guda biyu a cikin aljihun shi sannan ya miƙe tsaye ya yi musu sallama. Ammi ta kira sunan shi da sauri, ya juyo yana mata kallon kar ki yi min haka. Cike da isa irin ta ɗa da mahaifi ta ce" amma Haidar kana da hankali kuwa? Kai bakasan ayi maka abin alheri ka yi godiya mai yawa ba? Shi ne ka yi mishi wannan banzar godiyar ka tafi? Allah wadai da lamarinka wallahi".

Da sauri Mashal ya dakatar da ita wajen ce wa" ahir ɗin ki Habibty, kada ki ƙara faɗawa ɗanki mummunar magana sabili da wani abu ya haɗa ku, kuma ma me ya yi ne? Godiya fa ya yi min so kike sai ya dafa ƙafafuna sannan za ki tabbatar da cewar ya yi mini godiya? Kada ki sake Allah wadai da shi kin ji?.

Cike da matsanan cin haushin ɗan nata ta amsa mishi da to, Shi kuwa Haidar rintse idon shi ya yi sannan ya fice baki ɗaya daga gidan, yau bai taho da direban shi ba dama kuma bai fiya fitowa da bodyguard ba idan zai je gidan Ammin shi ba, Yadda ya tsani mutuwar shi haka ya tsani mijin mahaifiyar shi har baya son tunawa da mugun ƙullin da ya haddasa mishi a arayuwa wanda har yanzu bai fita daga cikin shi ba.

Kiran Khausar ya dinga shigowa akai-akai, sosai yaji tamkar zai fasa wayar saboda haushi domin kuwa a rayuwar shi baya son ko tunawa da ita, musamman da ta zama ƴar aminin Mashal abokin cin mushin sa.

_LULU_

"Hajiya don Allah ki taimakeni ki shige min gaba wajen son na auri yaya Haidar, wallahi ina tsananin son shi da ƙaunar shi wallahi idan har ban aure shi ba bansan inda zan sanya kaina b"...

Wani irin mugun mari Hajiya babba ta gaura mata, sannan ta fara magana tana huci ta ce" Allah ina roƙonka ka sa mafarki nake, yaron da ba ɗan halak ba shi kike so"?.

*$HUMAIRA*
*$AMEERA*
*$ANISA*

*$UMMA*
*$HAIDAR*
*$MASHAL*
*$AMMI*
*$MIMI*
*$LULU*
*$HAJIYA BABBA*

SHARE
COMMENTS
CHART NO WHATSAPP📲

MRS GREEN CE
[7/1, 11:54 AM] UMMU MAHER (MISS GREEN)🍃: *_💋ƊAN HALAK💋_*

MALLAKAR
*UMMU MAHER(MISS GREEN)🍃*

_*AREWA WRITER'S ASSOCIATION📖*_

_AREWABOOK_
https://arewabooks.com/book?id=6631fffa0eeb3b80f1ef8159

_WATTPAD_
https://www.wattpad.com/story/368199708?utm_medium=link&utm_source=android&utm_content=story_info

Ina masu son shiga adashe Amma kuna fargaba🤔yar uwa ki tsarkake zuciyan ki kizo kiyi adashe cikin aminci da kwanciyan hankali insha Allah Babu rigima ko tashin hankali kwanciyan hankali zaki Yi adashen ki Kuma mu gama lfyh da yardan Allah..🥰🤝

30k weekly parking 300k

1)Haj Maryam✅

2)Ada umar/hafsat yahya✅

3)Usman

4) barrister hauwa'u

5)shafa bello/baby daura

6)

7)

8)

9)

10)
Akama slotd

https://chat.whatsapp.com/HAkm8rlNu8a0ouQsRmuDuL

20

______Ganin jikina ya yi sanyi ta ce"uhum dama wahalar da kanki ki ke amma ni nasan waye mahaifinku, ku kuɗi suna bin shi ba zai bayar ba domin kuwa ba don ku yake neman shi ba". Tana kaiwa nan ta fashe da matsanancin kuka mai cin rai, tabbas da ɗaci da ciwo ace uban ƴaƴanka ya maida ƙuntata maka shi ne abu mafi soyuwa a wajen shi.

Likita ya fuskancemu sosai, duk da ban faɗa mishi ba amma ya fahimci duk abin da yake faruwa amma wasiƙar fuska tana ga zuciya, idan kaga wani yana dariya to halin da zuciyar shi take ciki ne hakazalika idan kaga mutum yana kuka to tabbas zuciyar shi ma ba daɗi in har ba kukan farin ciki bane.

Cike da tausayawa ya ce"babu damuwa ni na ɗauki nauyin yi mata aiki, Allah ya bata lafiya". Ya

shige gaba ba tare da ya juyo ba. Kukan farin ciki muka fara yi, Umma tabi bayan shi tana mishi godiya kawai ya ɗaga mata hannu alamar ba komi.

Muna zaune kusan awa biyu, sai ga likitan ya nufo inda muke fuskar shi babu annuri, dukkanmu muka tsira mishi idanuwa tamkar masu gano wani abu a idanun na shi, mun kuwa hango ɗin domin kuwa kana ganin shi kasan yana cikin damuwa sosai.

Maganar da ya fara faɗa mana yasa na saki wata irin ƙara tamkar wacce iyayenta duka biyu suka mutu.

_HAIDAR_

Suna zaune da Hammud Ammi ta kira, jikin shi a sanyaye ya ɗauki wayar domin yasan dole sai ta kira.

"Haidar anya kuwa kana son gamawa da duniya lafiya? Shin meye laifin wanda yace yana son ka? Shin ya dace abin da kake yi wa Alhaji? Duk irin abubuwan da ya yi maka tun kana yaro sai yanzu ne za ka bijire mishi? Saboda ka kawo kai ko? Saboda a yanzu ya alkinta maka dukiyar ka ya baka ita shi ne zaka saka mishi da irin haka? To bari kaji ni ba wani abu bane a wajena in sallamawa duniya kai baki ɗaya, in yadda ƙwallon mangwaro na huta da ƙuda kuma aure ne ko kana so ko baka so sai an yi shi, fitinannan yaro kawai mtsss"!. Ta saki me ƙara, Haidar yaji ranshi ya sosu sosai wato ma tafi son mijinta akan shi? Wato duk irin abubuwan da ya faru acan baya ita ɗin ba ta ga hakan ba? Duk irin rashin mutuncin da ya yi musu bata gani ba? Tabbas akwai lauje a cikin naɗi, domin idan ba asiri ya yiwa Amminshi ba ya tabbatar bai kai ta manta irin abubuwan da ya yi mata ba har ma dashi ɗanta, shi kanshi abin da yasa yake ɗaga mishi bai wuce Mimi ƙanwar shi ba, ƴar shi ta cikin shi babu yadda zai yi dashi shi yasa ma yake ɗaga mishi ƙafa, amma da ace wani ne ya aikata mummunan aiki irin wannan to tabbas da tuni ya datse duk wata alaƙa dashi.

Hanmud ya tsura mishi ido, ganin shi cikin damuwa yasa bai tanka mishi ba ya kyale shi, idan ya gama tunanin sai ya yi mishi magana domin yasan halin shi yi mai magana zai iya janyo musu rigima.

Ko da ya fara tunanin baisan lokacin da barci ya sure shi ba, Hammud yana ta kallon shi yana dariya domin idan shi za a yiwa auren gata irin haka shi ko a jikin shi, amma duk ya wani bi ya ɗaga hankalin shi.

Wani farin mutum ya gani, a zaune cikin wata inuwa gwanin ban sha'awa ga wasu irin kurayen furanni masu kyau da sheƙi, yana ta yiwa Haidar murmushi yana so yazo wajen Haidar amma ya kasa, domin kuwa wani ƙaton rafi ne a tsakiyarsu shi ne abin da ya hana dukkaninsu ƙarasawa amma dukkansu a zaƙe suke domin son ƙarasawa wajen junansu.

Haidar ya hango wani ƙaton kwale-kwale wanda yake a kusa dashi, da sauri ya ƙarasa ya shige ciki yana murna domin bai san waccen mutumin ba amma Allah ta'Ala ya ɗora mishi son shi sosai fiye da son da yake yiwa kanshi.

Sauri-sauri yake ya ƙarasa, ai kuwa cikin ikon Allah sai ga shi a kusa da shi nan da nan ya fito da zummar zuwa wajen shi, cike da tsoro da firgici ya dinga kallon fuskar da ta tsaya a gabanshi, wajen tare mishi ƙarasawa kusa da wannan mutumin da yake son zuwa, wannan fuskar har ya mutu ba zai taɓa mantawa da ita ba wannan fuskar ita ce fuska mafi kyawu wacce ya taɓa ganinta sau ɗaya tak kuma bai yi sa'ar ƙara ganinta ba, wannan fuskar ya daɗe da mafarkin sake ganinta.

Firgigit ya tashi, yana waiwaye tamkar wanda ke son hango wata halitta a cikin ɗakin...

_TASLEM_

Marin da Hajiyarta ta wanke ta dashi bai sanya bakinta mutuwa ba, ta fara magana tana kuka"Hajiya ko zaki kasheni na dawo bazan daina son Yaya Haidar ba, son shi a jinin jikina yake ya zamanto tamkar shi ne komi na rayuwa ta, ina son shi tamkar yadda uwa take son yaranta Hajiya a son shi banƙi in mutu ba, auren shi kuwa shi ne babban burina a rayuwa".

Tana gama faɗar hakan ta fita da sauri tana haɗa ƙafa, domin sauri take ta cimma ɗaki saboda yadda take muradin yin kuka ba tare da wani ko wata ya hana ta ba.

takaici da baƙin ciki tamkar zai kashe Hajiya babba, ji take kamar ta shaƙe Tasleem ta huta da baƙin ciki, ga shi akaf yaranta tafi son Tasleem bata haɗa son ta dana kowa saboda ita kaɗai ce ƴa tilo ga Alhaji Mashal.

hum, ni ummu maher na ce idan baka mutu ba za ka yi kallo, yanzu ace yara kusan 7 amma mutum ɗaya ce ƴarsa? ikon Allah to me ya janyo hakan? Uhum wannan wani sirri ne me girma jin shi sai nan gaba.

Da sauri Tasleem ta fice, domin ba ta son kowa yaga fitar ta ayau ɗinnan za ta fasa kwai kowa ma ya sani, domin ba zata zuba ido mahaifiyarta ta hanata samun muradin ranta Haidar ba, ta rasa wacce irin ƙiyayya ce a tsakanin Haidar da Hajiya, domin ita dai tun tasowarta take ganin irin mummunar ƙiyayyar da Hajiya ke yiwa Haidar, acan baya ko kaɗan bata ji tana son Haidar ba shi yasa ma take taya Hajiyarta ƙin Haidar ɗin, amma tunda ta gane tana ƙaunar shi sai ta daina ƙin shi sai ma wata sassanyar ƙaunar shi wacce ke barazanar huda zuciyarta.

Jin fitar ta a mota ya sanya Hajiya fitowa da sauri, gate man ɗin dake baƙin ƙofa ta tambaya, suka sanar mata eh ita ce ta fita a mota. Sosai gabanta ya faɗi domin kuwa taji lokacin da ta fita a mota.

Da gudu ta ɗakko wayarta, ta dinga kiranta amma baturiyar waya ta sanar mata wayar tana a kashe, zuciyarta ta hau harbawa tana zillo tasan halin Tasleem da baƙar zuciya, in har ta ce tana son abu to tabbas tana son shi da gaba ɗaya zuciyarta, kuma za ta iya komi saboda abin da take so, idan ta tsani mutum kuwa ko duk duniya zasu taru to tabbas ba za su zamar wa mutum gata ba.

Babu irin neman da ba ta yiwa Tasleem ba, amma sam bata ganta ba hankali a tashe ta dawo gida, sai dai tana shigowa taja tunga saboda ganin motar asibiti a gidansu ga shi ko ina ya yi jina-jina, ai bata san lokacin da ta buga wani ihu ba ta faɗi ƙasa sumammiya.

_HANAN_

Durƙushe take gaban shi, Yaya Jummai sai kyafta mata ido take ma'ana ta fara magana.
"Boka ni Sunana Hanan, Allah ya jarabce ni da son wani bawan Allah saurayin ƙawata, kafin shi na so wani kamar me sai ya yaudare ni da kaina nake mishi hidima domin ya so ni amma ya gudu, yanzu ma tsoro nake kada wannan ya suɓuce domin kuwa gab ake da ɗaura mishi aure..."

*TIRRR ƘA SHI*
Me Hanan take nufi ne da Haidar? Sannan waye ya mutu a gidan Mashal? Sannan wani sirri ne da Tasleem take ɓoyewa? Wani sirri ne Haidar shima yake ɓoyewa? Wa ya gani a mafarkin sa? Sannan me ya faru a asibiti da fuskokin su Humaira suka canja?.

Wannan amsoshin na ku duk sai a littafi na 2, wanda zai zama na kuɗi ne complete ɗin shi 1k ne wanda zai kasance har da littafi na 3.

Idan kin tashi jin dukkanin amsoshin ki na cikin littafin ƊAN HALAK ki tura kuɗin ki ta wannan Account ɗin.
2212328303
RABIATU BASHIR
ZENITH BANK.

MRS GREEN CE
SHARE
COMMENTS
CHART NO CALL
07068606171.